***BARADEN MUSULUNCI 1***

# *ALKAKI DA RUWAN ZUMA*

Ingantaccen Tarihin Fiyayyen Halitta
Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam*
Daga Haifuwa Zuwa Jana'iza

***1***

Wallafar
**Muhammad Mansur Ibrahim**
Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci
Ta Jami'ar Usmanu Ɗan Fodiyo, Sakkwato

# Bismillahir Rahmanir Rahim

## Kumshiya

0.1 **Gabatarwar Baraden Musulunci** ..................................................

0.2 Muhimmancin Wannan Tarihi .....................................................

0.3 Wasu Ababen da Wannan Tarihi ya Keɓanta da su ......................

**Fasali na Farko:**

1.1 Halin da Duniya Take Ciki Kafin Bayyanar

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ..........................................

*1.1.1* Kasar Farisa: ................................................................

*1.1.2* Kasar Ruma: ...............................................................

*1.1.3* Kasashen Turawa: .......................................................

*1.1.4* Yahudawan Sham, Iraƙi da Hijaz da Nasara: ................

*1.1.5* Nahiyarmu ta Afirka: ...................................................

1.2 Muhammadu Zaɓen Allah: .........................................................

1.3 Me ya sa Aka Zaɓi Yankin Larabawa? ........................................

1.4 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Samu Gagarumar Nasara

1.5 Matsayin Birnin Makka da Darajarsa: ...........................................

1.6 Shekarar Giwaye: ..........................................................................

**Fasali na Biyu:**

2.0 Tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*

Daga Haifuwa Zuwa Manzanci: ........................................................

2.1 Sunansa da Asalinsa: .....................................................................

2.2 Babba Ɗan Manyan Mutane: .........................................................

2.3 Haɗuwar Dare Ɗaya Tarihin Har Abada: ............................................

2.4 Watan Bakwai Maƙarar Rani: ............................................................

2.5 Aure Mafi Albarka: ..................................................................

2.6 Alfijir ya Keto: ..........................................................................

2.7 Siffar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam:* ................................

2.8 Renon sa da Shayarwa a Tungar Banu Sa'ad: .....................................

2.9 Maraya Ɗan Gatan Ubangiji: .........................................................

2.10 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a Gidan Baffansa Abu Ɗalib

2.11 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a Lokacin Samartaka: ...........

1.11.1 Fatauci: ........................................................................
1.11.2 Yaƙin Rashin Dattaku *"Harbul Fijar":* .................................
1.11.3 Kungiyar Tabbatar da Adalci da Kariyar Marasa Galihu: ..........

2.11.4 Ginin Ka'aba: ................................................................

2.12 Aure da Gina Iyali: ..........................................................

2.13 Sanin Matsayin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam:* ...................

2.14 Wane Annabi ne ya fi? ..............................................................

2.15 Mu'ujizojinsa: ………………………………………………………..

2.16.0 Daga Cikin Fifikonsa: ....................................................

٢.16.1 Fifikon Shiriyarsa: ..................................................................

2.16.2 Albarkacin Sawunsa: ................................................................

2.16.3 Matsayin Iyalansa: ....................................................................

2.16.3.1 Su Wane ne Iyalansa? .........................................................

2.16.3.2 Darajojin Iyalansa: ..................................................................

2.16.3.3 Darajojinsu na Tarayya: ........................................................

2.16.3.4 Darajojin Ɗaiɗaikun su: ........................................................

2.16.3.5 Matsayin *Ahlulbaiti* a Wurin Musulmi: .......................................

2.17 Darajar Sahabbansa: ......................................................................

2.17.1 Me ya Banbanta Sahabban Annabi? ...............................................

2.17.2 Darajojin Ɗaiɗaikunsu: ...............................................................

2.18 Ɗaukakar Al'ummarsa: ..................................................................

2.19 Ɗarwaya, Shanya da Naɗewa: .....................................................

**Fasali na Uku:**

Tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*

Daga Farkon Annabta Zuwa Hijira: .....................................................

3.1 Gari ya Waye: ..........................................................................

3.2 Nana Aisha ta Sifaita Yadda Wahayi ya Fara Zuwa: ..........................

3.3 Wahayi ya Tsinke,

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Shiga Damuwa: .......................

3.4 Harsashin Musulunci: ......................................................................

3.5 Ayarin Farko: ................................................................................

3.5.1. Musuluntar Sayyidi Abubakar Siddiƙu: ..........................................

3.6 Ayari na Biyu: ...............................................................................

3.7 Makarantar Farko: Dar Al-Arƙam: ................................................

3.7 Da'awar Musulunci ta Fara Fitowa Fili: ...............................................

3.8 An Fara Kai Ruwa Rana Tsakanin Musulunci da Kafirci: .........................

3.9.0 Matakan Faɗa da Musulunci: ......................................................

3.9.1 Koƙarin Rage ma sa Karfin Tsaro: ..............................................

3.9.2. Barazanar Taɓa Lafiyarsa: .........................................................

3.9.3. Soke-soke da Tuhumce-tuhumce: ..............................................

3.9.4 Matakin Izgili da Tozartawa: ........................................................

3.9.5 Wasu Daga Cikin 'Yan Kungiyar "Masu Izgili': ...............................

3.10 Musulunci ya ci Gaba da Yaɗuwa a Sauran Sassa: ...............................

1. Musuluntar Abu Dhar Al-Gifari: ....................................................

2. Musuluntar Amru Ɗan Abasata: .....................................................

3. Musuluntar Dhimad Al-Azdi: .........................................................

3.11 Musulmi Sun ci Gaba da Fuskantar wulaƙanci: ................................

3.11.1 Matakin Azabtawa: ....................................................................

3.12 Musulmi Sun Jure Wahala: ..........................................................

4. Khabbab Ɗan Al-Arat:: ................................................

5. Khalid Ɗan Sa'id Ɗan Al-Ass: ..........................................

6. Mus'abu Ɗan Umair: ....................................................

3.13 Tura ta Kai Bango: ..................................................................

7. Abdullahi Ɗan Mas'ud: ..........................................................

3.14 Mushrikai Sun Ɓullo da Sabon Salo: ............................................

6. Matakin Sulhu: ......................................................................

1.15 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi Baran-baran da Mushrikai: .........................................................

3.16 Musulmi Sun Kaura Zuwa Habasha: ............................................

3.17 Yanayi ya Canja a Makka,'Yan Gudun Hijira Sun Dawo: ......................

3.18 Musulunci ya Samu Garkuwa: ......................................................

3.19 Makirci na Karshe: Manzon Allah da Danginsa Sun fuskanci

Ɗaurin Ta-la-la: ......................................................................

3.20 Musulmi Sun Sake Komawa Habasha: ..............................................

3.21 Jarrabawa ta Kai Maƙura: ............................................................

3.22 Musulunci ya Tsallaka Zuwa Ƙasashen Waje: ..................................

3.23 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Dawo Gida: .....................

3.24 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Samu Lambar Yabo: .......

3.25 Addinin Musulunci a Birnin Madina: ................................................

3.26 Waɗanda Suka Fara Yin Hijira: ...................................................

3.27 Tirjiyar Sahabbai a Wurin Yin Hijira: ...............................................

***Bismillahir Rahmanir Rahim***

## 0.2 Gabatarwar Baraden Musulunci

Godiya da yabo sun tabbata ga Allah Maɗaukakin Sarki a kan ni'imominsa da ba su ƙarewa. Tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen talikai, wanda fitilar shiriyarsa ta haskaka mana rayuwa, muka fita daga ɗimuwa zuwa shiriya, muka bar duhu zuwa haske. Allah ya daɗa tsira da aminci ga matansa, da zuriyyarsa da sauran iyalansa, da Sahabbansa kacokam da waɗanda duk suka taimaka masa wajen tsayuwar addininsa da gamewar saƙonsa har zuwa rana ta ƙarshe. Bayan haka:

Idan mutum ya yi ma tarihin wanzuwar ɗan Adam a bisa doron ƙasa kallon basira da nazarin ƙwaƙwaf, ya yi masa fiɗar ragon malam, ma'ana ya duba ciki da wajensa, zai gano cewa, a da can farkon zamani, mutane na rayuwa ne a cikin wannan sarari na *Subhana,* kara zube kamar dabbobi; babu doka babu oda. A wancan zamani babu abin da yake gaban mutum sai neman abin da zai cika masa tumbinsa, ta hanyar farautar ruwa da ta tudu, daɗa halas ce ta samu ko haramiya. Wannan duk bai dame shi ba; can ga su gada, zomo ya ji kiɗan farauta. Ɗan Adam kenan! Kamar ba ayi wani lokaci ba can baya wanda zancen sutura domin rufe al'aura a gurin sa bai taso ba. Zuciyar ɗan Adam a wancan lokaci ita ce a gaba shi ko yana bin ta, ga shi kuwa ita zuciya ba abin da take horo da shi sai mugun aiki. Domin canja wannan muguwar tafiya ne, irin ta kura, wadda ta yamutsa hazo, ta gurɓata rayuwar gaba ɗayan halitta, kuma domin ɗora halittu baki ɗaya a kan hanya madaidaiciya, Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓi ɗan Adam daga cikin sauran, ya yi masa ni'imar hankali da tunani, ya kuma aiko masa da Manzanni daga cikin jinsinsa. Saƙonnin da waɗannan Manzanni suka zo ma duniyar ɗan Adam da su, a dunƙule, na nufin canja wancan salon tafiya ne na farko; ɗan Adam ya dawo shi ne a gaba zuciyarsa tana bi; ya sa ta, ta so abin da ba ta so, ya hana ta, ta ƙi abin da take so, a matsayinsa na bawan Allah. Isowar saƙon Allah *Subhanahu wa Ta'alah* ke da wuya, sai ɗan Adam ya wayi gari cikin haske bisa haske; hasken hankali da hasken nassi. Watsuwar hasken ayyukan waɗannan Manzanni a faɗin duniya kuwa shi ya samar da kafuwar Dauloli daban-daban a bayan ƙasa.

Addinin da Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zo da shi daga wurin Allah *Subhanahu wa Ta'alah,* wato Musulunci, shi ne addini ƙwaya ɗaya tal, wanda cikin ikon Allah da iyawarsa, bai ci karo da matsalar gurɓacewa ko lalacewa a sanadiyyar tsawon lokaci ba, matsala irin wadda sauran saukakkin addinai suka yi artabu da ita. Alƙur'ani mai girma, tun da asubahin saukarsa, ya shafe gaɓar makeken gulbin rayuwar halittu baki ɗaya. Ba a taɓa samun irin sa ba a bayan ƙasa, ta fuskar inganci da bunƙasa da yaɗo da barbajewa duk da irin sara da sassaƙa da ya rinƙa cin karo da su daga ɓangarorin magabta.

A bisa waɗannan darajoji da addinin Musulunci ya keɓanta da su, babu wata Daula da aka kafa a duniya, a ƙarƙashin inuwarsa, face ni'imar da ɗan Adam ya samu kansa a cikin ta ta sa ya yi gurin ɗorewarta har abada. Ka san dalili? Bari ka ji. Allah Buwayayye ya halicci mutum ne da abubuwa biyu a tattare da shi; gangar jiki da kuma *rúhí*. To, addinin Musulunci shi ne kaɗai addinin da ya yi ma gaba ɗayan waɗannan sassa biyu tanadi da cikakken tsari masu gamsarwa. Ya tsara yadda za a nemi abinci na halas don ciyar da gangar jiki, da fatar ta kuɓuta daga azabar wuta gobe Kiyama. Ya kuma shirya yadda za a ba *rúhí* kyakkyawar tarbiya don ya tsira daga azabar ruɗu da kwan-gaba-kwan-baya a nan duniya. Daulolin Musulunci, a bisa wannan dalili sun himmatu wajen ba da cikakkiyar kulawa ga duk abin da ya shafi rayuwar jama'a na sha'anin duniya da Lahira.

Mamayewar da tunani da wayewa irin na Turawan gabashi da yammacin Turai suka yi wa duniya, sakamakon Juyin-juya-halin Masana'antu, wanda ya gurɓata tsarin rayuwar karkara, ya kuma gurgunta yanayin rayuwar birane, ya rusa gidaje, rusawa irin ta *baɗini* bayan ya gina su a *zahiri*, ya cika hanyoyi da lunguna da dituna da saƙo-saƙo, da 'ya'ya mata masu yawo tsirara, suna kaiwa da komowa a rana. Wannan mamayewa, ita ta haifar da tsame harkokin addini daga cikin harkokin duniya. Aka ce addini ya tsaya cikin Masallaci, sauran rayuwa kuma kowa ya yi ta sha'aninsa iya son zuciyarsa. Yarda da wannan sabon salo a duniyar musulmi shi ya jefa gaba ɗayanmu cikin fitina da tajin-tajin da halin ni 'yasu da muke ciki a yau.

Wannan littafi da yake a hannun mai karatu a halin yanzu, shi ne na farko daga cikin jerin littattafan da aka ba wa suna: “Baraden Musulunci.” Babbar manufar rubuta su ita ce, ƙoƙarin samar da gyara ga wannan hali da muke ciki ta hanyar karantar da al’ummar musulmi musamman matasa, rayuwa da ayyukan sadaukai da gwaraje; baraden Musulunci maza da mata waɗanda suka taka muhimmiyar rawa wajen tsayuwar wannan addini da bunƙasar sa da yaɗuwar sa har zuwa yau da addinin ya iso a gare mu. Wannan kuwa yana da fa’idoji da dama waɗanda suka haɗa da; sanin matsayin waɗannan bayin Allah da darajta su, da yi ma su addu’a irin wadda Alƙur’ani ya karantar da mu. Haka kuma idan muka mayar da rayuwarsu ta zamo madubi a gare mu za mu samu abin koyi mai yawa da zai yi mana saiti ga tafiyar da tamu rayuwa. A kullum kuma karanta tarihinsu zai ƙara zaburar da mu wajen ci gaba da yaɗa addinin Musulunci kamar yadda su ma suka yi. Za mu kuma gyara da yawa daga cikin tunane-tunane da muka yo aro waɗanda ba su dace da mu ba, da waɗanda aka cusa mana dangane da addini alhalin ba haka gaskiyar lamari take ba. Jerin waɗannan littafai guda bakwai ne kamar haka:

### *1. Alkaki da Ruwan Zuma I, II*

A cikin wannan littafi za mu yi bitar rayuwa ma fi tsarki ta ɗan Adam zaɓaɓɓe wanda Allah ya tsarkake shi, kuma ya sanya rayuwarsa ta zama madubi ga irin rayuwar da aka halicce mu domin ta. Wannan zaɓaɓɓen taliki shi ne Annabinmu Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Kashi na farko na littafin zai yi maganar rayuwarsa ne daga haifuwa zuwa hijira. Zai kuma ba da haske game da matsayi da darajojinsa waɗanda Allah ya fifita shi da su a kan sauran talikai. A yayin da kashi na biyu zai yi maganar kafuwar daular Musulunci ta farko a birnin Madina bayan hijira da yaɗuwar addinin daga nan zuwa sauran sassan duniya, da irin ci gaban rayuwa da Musulunci ya samar wa duniyar wancan lokaci.

### *2. Kaddara ta Riga Fata*

Wannan littafi zai ba da cikakken haske ne game da rayuwar Sahabbai da gudunmawar da suka bayar wajen yaɗa addinin Musulunci zuwa sassan duniya a zamanin halifofi biyar na farko, waɗanda suka haɗa da Sayyidi Abubakar da Umar da

Usmanu da Aliyu da ɗansa Al-Hasan, da kuma sarakuna guda biyu da suka biyo bayan su, su ne: Sayyidi Mu'awiya da ɗansa Yazid. Littafin zai tattauna ƙalubale iri-iri da al'ummar musulmi ta fuskanta a wannan zamani wanda ya haɗa har da kashe halifofi uku da aka yi a jere da juna, musamman juyin mulkin da ya kai ƙarshen rayuwar halifa na uku; Sayyidi Usmanu. Sai kuma yaƙoƙin cikin gida da aka ingiza musulmi zuwa gare su; *Jamal da Siffin* a zamanin halifa na huɗu; Sayyidi Ali. Sannan sai rikicin Karbala wanda ya faru a zamanin sarki na bakwai; Yazid wanda Sayyidi Husaini ya samu shahada a cikin sa tare da 'yan uwansa su goma sha bakwai. Za ayi maganar fitinun da wannan rikici ya haifar waɗanda har yau muna fama da sauran ɓurɓushin tasirinsu.

### *3. Daulolin Musulunci I, II*

Wannan ɓangare kuma, da zai ƙunshi juzu'i biyu, kowanne mai zaman kansa, zai ba da cikakken tarihin Musulmi da Musulunci ne a zamanin dauloli biyu; Banu Umayya da Banul Abbas waɗanda suka zo kai tsaye bayan wucewar hilafa irin ta Annabta. Yin haka ya zama wajibi, tilas kuma *hatmun* ganin yadda tarihin musulmi a waɗannan zamunan ya gamu da lahani mai yawa a hannun marubuta, musamman waɗanda suka yi wa fagen shigar sharu ba shanu. Ina nufin malaman Adabin Larabci da suka faɗa gonar tarihi wadda ba tasu ce ba, da kuma wasu marubuta masu son zuciya a cikin gida da waje, 'yan kankajeli masu ba-ni-na-iya, da 'yan gutsuri-tsoma a cikin sha'anin karatu. Za mu yi ƙoƙarin yi wa tarihin adalci ta hanyar ɗora shi a kan ma'aunan da amintattun malamai a duniyar ilimi suka kafa, don tantance gaskiya. Daga nan littafin zai jero sunaye da tarihin ƙungiyoyin da suka riƙa yin tawaye a kan sarakuna na wannan lokaci da hujjar cewa, sarauta gadon gidan Annabta ce kawai, babu mai haƙƙi a cikin ta sai iyalan Sayyidi Husaini. Kamar tawayen Mukhtar Ath-Thaƙafi (64-67H) da ƙungiyar tawayen *An-Nafs Az-Zakiyya* (145H) da ƙungiyar tawayen Musallas da sauransu.  A ɗaya juzu'in kuma za mu kawo cikakken tarihin Daulolin da 'yan Shi'a suka kafa da sunan Musulunci mu bayyana irin lahani da

ɓarnar da suka yi ma al'ummar Musulmi. Kamar Daular Idrisawa[1] da ta Hamdanawa[2] da ta Buwaihawa[3] da Ubaidawa[4] da Karmaɗawa[5] da Safawiyyawa.[6]

### *4. Magadan Annabawa I, II, & III*

Waɗannan littafai guda uku za su ba da tarihin wasu zaɓaɓɓun Sarakuna ne, nagartattu, irin su Nuruddin Zunki, da Ƙaɗaz, da Baibaras, da Muhammad Al-Fatih da jikansa Sulaiman Al-Kanuni da ire-iren su, waɗanda suka bunƙasa addinin Musulunci kowanne a lokacinsa, tun daga ƙarni na biyu har zuwa na goma sha biyu bayan hijira.

---

[1] Ta samo sunanta ne daga Idris ɗan Abdullahi jikan Sayyidi Al-Hasan wanda ya kuɓuta bayan yaƙin "*Fakh*" ya gudu zuwa Masar daga nan ya gangara yamma in da ya kafa wannan Daula da ta rayu tsawon shekaru ɗari biyu a yankin Afrika ta gabas. Zamu ƙirga wannan Daula a cikin Daulolin Shi'a saboda haka mawallafan tarihi ke lissafa ta tare da bayanin da zai gamsar cewa bai dace a ƙirga ta a cikin su ba sabodadalilan da za mu kawo.

[2] Wanda ya kafa ta shi ne Hamdan ɗan Hamdun gwamnan Mausil a zamanin Sarki Mu'utadhid a cikin ƙarni na uku.

[3] Buwaihi wani Bafarise ne mai kamun kifi wanda ya haifi 'ya'ya uku; Hasan da Ali da Ahmad waɗanda suka zama turakun da aka kafa Daular a kan ƙoƙarinsu a yankunan da ke cikin Iran da Iraƙi a yanzu. A zamanin gwamnatinsu ne aka canja mazhabar ƙasar Iran daga Sunna zuwa Shi'a a tsawon mulkin da suka yi na shekaru 113.

[4] Ta samo sunanta ne daga wani Ubaidullahi da ake tambaba game da asalinsa amma ya jingina kansa ga gidan Annabta kuma daga ƙarshe ya yi da'awar shi ma Annabi ne. A zamanin wannan Daula aka shigar da Shirkoki da Bidi'oi masu yawa a addini, aka hana Sallar Tarawihi, aka wajabta azumin wasu kwana biyu na daban, aka hana *Assalatu Khairun Minan Naum,* aka ƙara *Hayya Ala Khair Al-*Amal a cikin kiran Sallah. Shahararren Mujahidin nan Salahuddin Al-Ayyubi shi ne ya kawo ƙarshen wannan Daula a shekarar 567H.

[5] Ta samo sunanta ne daga wani dattijo da aka kira "Kurmut" wanda ya bayyana ibada da gudun duniya daga baya ya kafa wata babbar ƙungiya da ta bunƙasa ta kafa gwamnati a kan tafarkin Shi'a. Sun kashe Alhazai masu ɗinbin yawa a shekarar 294H. Tun daga wannan lokaci aka daina aikin Hajji har tsawon shekaru da dama. Bayan haka ne ɗaya daga cikin sarakunansu - Abu Ɗahir – ya gina wata Ka'aba ta daban a garin Hajar na ƙasar Yaman ya so ya karkata musulmi zuwa aikin Hajji a can amma bai ci nasara ba. Saboda haka sai ya yi ma alhazai afke a shekarar 317H ya yi ɓarna wacce ba ta da daɗin wasaftawa. Suka ɓantale *Hajarul Aswad* suka yi guzuri da shi, ba su dawo da shi ba sai bayan shekaru 22 bayan da waccan fatar tasu ta canja wurin aikin Hajji ta kasa tabbata. Sun yi mulki na kusan shekaru 100.

[6] Ana jingina ta ne ga Safiyuddin Al-Ardabili wanda ya yaɗa addinin Shi'a a ƙasar Iran a ƙarshen ƙarni na takwas shi da 'ya'yansa. A zamanin Daularsu aka wajabta bin mazhabar Shi'a, aka yanke hukuncin kisa ga duk wanda ya saɓa.

Da kuma manya-manyan malamai, fitattu. Ina nufin fitilun duniya, irin su Sarkin Malamai Sa'idu ɗan Musayyib da hamshaƙin malamin nan attajiri Abdullahi ɗan Mubarak da Sayyidi Abdulƙadir Al-Jilani da ire-irensu. Ko wannen su za a faɗe shi a layin da ya shahara da shi. Kamar a fagen Hadisi irin su Imamul Bukahri da Muslim, a sashen Fiƙihu irin su Imam Malik da Abu Hanifa, a ɓangaren Tasawwufi da Tarbiyya irin su Junaidu da Gazali. Sai kuma manyan mujahidai da suka haɗa alƙalami da takobi irin su Sarkin Malamai Izzuddini da Salahuddin Al-Ayyubi da Shehun Musulunci Ibnu Taimiyya. Daga cikin fitattun mawallafa na fannoni daban daban za mu bayyana tarihin Ibnul Kayyim da Ibnul Jauzi da Imam As-Suyuɗi da dai sauransu.

### *5. Kansakali*

Wannan littafi zai yi maganar fitintinu da yaƙoƙa ne da aka yi su a zamanin Daulolin Musulunci. Zai tattauna mas'alar jihadi; tushensa, manufofinsa da ƙa'idojinsa a addinin Musulunci. Sannan ya amsa wata muhimmiyar tambaya da takan taso a ko da yaushe, ita ce, ko gaskiya ne da kaifin takobi addinin Musulunci ya baje kolinsa har ya yaɗu a duniya? A cikin wannan littafi za mu ga ƙalubale iri daban daban da musulmi suka samu kansu a ciki a tsawon tarihi, kamar fitinar Tattar waɗanda suka ɗauki sama da shekaru ɗari suna yawatawa a duniyar musulmi, suka ƙoƙƙona tare da rurrusa birane masu ɗinbin yawa kuma suka hallaka miliyoyin jama'a daga cikin al'ummar musulmi. Da kuma fitinar "Yaƙoƙin Kuros" waɗanda a lokacinsu An-Nasara suka yi wa musulmi ƙawanya ta ko ina, suka yaƙi daulolin Musulunci na wancan lokaci suka kwararar da jinin miliyoyin jama'a kamar ba 'yan Adam ne ba. Sai kuma yaƙin duniya na ɗaya da na biyu[7] da irin yadda suka shafi al'ummar musulmi kuma suka zama sanadiyyar faɗuwar Daular Musulunci ta ƙarshe wadda har yau babu wadda ta maye gurbinta. Babban maƙasudi shi ne fitar da darussa da za su amfani musulmi na yau da na gobe daga waɗancan fitinu. Bugu da ƙari kuma

[7] A cikin waɗannan yaƙoƙa (1914-1939) an yi hasarar sama da mutane miliyan 62 (kashi 2% na mutanen duniya a wancan lokaci) ban da rugujewar tattalin arziki da yawan zawarawa da marayu da nakasassu da marasa aikin yi da yaƙin ya bari. Amma kuma duk da haka akwai alherori da yaƙoƙan suka bari waɗanda a yanzu muke cin moriyarsu kamar yadda za mu gani idan muka zo kan bayanin su in Allah ya so.

za mu ga cewa, kusan duk waɗannan fitinu Annabinmu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ba da labarin su a cikin ingantattun hadisai wasu ma har da sunayensu da na garuruwan da za su auku, abin da zai tabbatar mana da gaskiyar Annabtarsa kuma ya wajabta mana yin aiki da umurninsa a cikin irin waɗannan lokuta, musamman kuma mafitar da ya bayar ga duk halin da muka shiga. Allah ya yi ma na gamon katar da alheri.

### *6. Musulunci a Afirka I, II*

Shi kuma wannan juz'i mai kashi biyu, an keɓe shi ne don ba da tarihin zuwan Musulunci a nahiyarmu ta Afirka. Zai soma ne tun daga bayanin kyakkyawar alaƙar da ta shiga tsakanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da wasu sarakunan Afirka kamar Najashi Sarkin Habasha da gudunmawar da Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* suka bayar wajen isar da saƙon Musulunci a gabascinta, musamman a zamanin Sarkin Musulmi Mu'awiya ɗan Abu Sufyan wanda ya tura na hannun damansa Amru ɗan Asi ya yaɗa Musulunci a ƙasar Masar, daga can kuma ya bazu zuwa sashen yamma. A nan ne za mu faɗi alaƙar auratayya da ta shiga a tsakanin Baraden Musulunci daga cikin Kuraishawa da mutanen wannan yanki, kamar auren da Uƙbatu ɗan Nafi'u ya yi da 'yar Sarki Barmanda na ƙasar Ghana mai suna Maryam wacce aka fi sani da "Bajjo Mango"[8] suka haifi 'ya'ya shida, cikin su har da Usmanu Toro kakan Musa Jokollo; kakan Mujaddidi Usmanu ɗan Fodiyo. Littafin zai yada haske a kan yanayin ƙasar Hausa kafin bayyanar Mujaddidi, sannan maganar jihadin da ya yi na sabunta karantarwar Musulunci da kafa daularsa, da irin gadon da ya bari, na gaskiya, da riƙon amana, da tsoron Allah, da cika alƙawari, da ba kowa haƙƙinsa, har zuwa shekaru ɗari da suka biyo baya (1804-1903). Haka kuma Juz'in zai kalli irin yadda almajiran Shehu na farko – musamman waɗanda suka karɓi tuta daga wurinsa - suka jagoranci mutanensu, da su ma irin gadon da suka bari, na karatu, da karantarwa, da zumunci, da tsare mutuncin dukiyar al'umma, da raya karkaru da Birane, ta hanyar gina rijiyoyi, da hanyoyi, da kasuwanni, da masallatai. *Hakaza,* da inganta masana'antu da sana'o'in gargajiya, da samar da kyakkyawan tsaro ta hanyar kafa

[8] Ita kaɗai ce Allah ya azurta Sarkin da ita, kuma wannan shi ne ma'anar sunan da aka laƙaba ma ta da Fulatanci "Bajjo Mango".

wuraren *ribaɗi* da inganta su, har aka wayi gari sun zama ƙasaitattun birane a wannan nahiya. Wannan littafi, ba zai shafa fatiha ba, sai ya yi tsokaci a kan irin yadda siyasar cikin gida da ta waje, a wannan shahararriyar Daula ta Ɗanfodiyo ta kasance.

*7. Sabuwar Duniya*

Littafi na ƙarshe a cikin wannan jeri, zai wasafta halin da Turawa suka samu wannan ƙasa a ciki, lokacin zuwansu, da kuma sauyin da suka kawo da irin sabon salon mulkin da suka shimfiɗa. Daga nan zai ci gaba da bin sawun abin da ya kai ya komo har aka samu 'yancin kai, aka kafa Jumhuriyyoyi daban-daban a Najeriya. Magabata a Jumhuriya ta farko, irin su Sardaunan Sakkwato Sir. Ahmadu Bello (1910-1966), da Firayiminista Sir. Abubakar Tafawa Ɓalewa (1912-1966), da sauran abokan aikinsu, yaya suka jagoranci wannan al'umma, kuma wane tarihi ne suka bari, a matsayinsu na musulmi 'yan Arewa? Wane hali ne Da'awa da kira zuwa ga addinin Musulunci suka kasance a ciki, a wannan zamani? Sai kuma gudunmawar da Shehin Malami Sheikh Abubakar Mahmud Gummi (1922-1991) da almajiransa suka bayar a irin wancan aikin na Mujaddidi don gyara abin da aka gurɓata. Kafuwar ƙungiyar Izala da Jama'atu da sauran lamurra masu kama da alaƙa da waɗannan, duk littafin zai tattauna su cikin yardar Allah. A ƙarshen wannan littafi ne kuma sakamakon binciken zai fito in Allah ya yarda, wanda shi ne zai ba da mafita ga matsalolin da muke fama da su don gina gobe, saboda 'ya'yanmu, kamar yadda muka tarar iyayenmu sun gina yau da muke rayuwa a kan ta.

Ina godiya ga duk 'yan uwa da suka bi wannan "Alkaki" a shafinmu na Fesbuk suka ɗanɗana shi tare da ni tare da yin ta'aliƙai masu ma'ana. Godiya ta musamman ga 'yata Saudatu bisa ƙoƙarin da ta yi na duba da gyara kurakuran ɗab'i da aka samu a ciki. Allah ya ƙara ma ta albarka ya ba ta 'ya'ya masu albarka irin ta. Shi kam ɗan uwa Aliyu Rufa'i ta sa gudunmawa wajen fitowar aikin ba sai mun faɗe ta ba. Amma ladarsa tana wurin Allah. Ni kam nawa bai wuce kawai in jinjina ma sa ba, tare da yi ma sa addu'a, Allah ya ɗayyaba zuri'arsa.

Allah muke roƙo ya yi ma na jagora, ya tsarkake aikinmu daga riya, ya aza mu ga sawaba ga duk abin da muke faɗa da wanda muke rubutawa da ma kuma wanda

muke aikatawa. Kamar kullum ƙofa a buɗe take don gyara kuskure ko tuntuɓen harshe da za su iya aukuwa a cikin wannan aiki ko wanin sa.

Tsira da aminci su ƙara tabbata ga Manzonmu, maigidanmu, masoyinmu; badaɗayin Allah; Muhammadu ɗan Abdullahi ɗan Abdulmuɗɗalabi, wanda kuma shi ne ɗan Aminatu ‘yar Wahabu ɗan Abdumanafi, tsarkakakke, ɗan tsarkaka, da iyalansa da Sahabbansa da mataimakansa kacokam ba mu cire ko guda ba.[9]

Baban Ramla

A birnin Sakkwato

6 ga Zul Ki’ida 1435 (31/8/2014M)

[9] Kamar yadda mai karatu zai iya lura wannan aiki da muka soma mai tsawo ne sosai da zai yiwu ya ɗauki shekaru da dama, musamman in aka yi la’akari da ɗinbin ayyukan da mawallafin yake fama da su da sauran wallafe wallafe da ba cikin wannan jerin ba. Fatar dai ita ce, idan Allah ya tsawaita rayuwa a kammala shi gaba ɗaya kafin shekara ta 2020. Idan kuma rai ya yi halinsa to, daga cikin zuri’a da almajirai sai a samu waɗanda za su ci gaba. Asalin wannan gabatarwa an rubuta ta a shekarar 2005 a birnin Doha na ƙasar Katar bayan rubuta littafi na farko ya yi nisa sosai. Cikin hukuncin ubangiji sai wannan aiki ya gamu da mishkilar na’ura mai ƙwaƙwalwa. Daga bisani muka fitar da litafi na biyu, sa’an nan muka soma sake wallafa na farko ta hanyar shafinmu na Fesbuk. A yanzu za mu miƙa kashi na farko na wannan juzu’i zuwa maɗaba’a. Yau Lahadi 6 ga Zul Ki’ida 1435 (31/8/2014M) a birinin Sakkwato. Godiya ta tabbata ga Allah ubangijijn talikai.

## 0.2 Muhimmancin Wannan Tarihi

Tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya banbanta da sauran tarihohi irin na manyan mutane da jagorori da ake karantawa ta fuskoki da dama:

1. Da farko dai karanta tarihinsa ibada ne.

2. Madubi ne na rayuwar da Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* yake son mu yi kwaikwayon ta.

3. Babu wata hanyar da take tabbatar ma na da gaskiyar wannan taliki da aka aiko kamar karanta tarihin rayuwarsa.

4. Babu wata hanya da za ta dawwamar da so da ƙaunarmu a gare shi sama da nazarin rayuwarsa mai albarka wadda take cike da ababen girma da wani ɗan Adam bai da irin su.

5. Sanin wannan tarihi mai albarka na taimaka mana wajen sanin dalilin saukar wasu da dama daga cikin ayin Alƙurani da kuma munasabar da ta sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya faɗi wasu hadisai. Wannan kuwa zai taimaka matuƙa wajen gane haƙiƙanin ma'anar nassi.

6. A cikin wannan tarihi ne zamu ga irin gudunmawar da Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* suka ba shi da taimakon sa da suka yi wajen isar da saƙon Musulunci. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* da kansa ya faɗi cewa, da su ne ya ƙarfafe shi har ya samu nasarar kafuwar addini.[10]

7. Kamar yadda a cikin sa ne za mu ga irin tarbiyyar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma su bisa ga umurnin da Maɗaukakin Sarki ya ba shi a cikin Alƙur'ani.[11]

Kaicon mutanen da suka yanke alaƙarsu da waɗannan bayin Allah waɗanda Manzon Allah ya tarbiyyantar da su domin mu koyi tarbiyyarsa daga wurin su.

[10] Suratul Anfal: 62 da Suratut Taybah: 88.
[11] Suratu Ali Imran: 164 da Suratul Jum'ah: 2.

Mutanen da tarbiyyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ta kama jininsu da tsokarsu har ta kai suka sayi aljannar Allah da ayyukansu. Kamar yadda Allah ya ce:

((إن الله اشترى من المؤمنين أنفسهم وأموالهم بأن لهم الجنة يقاتلون في سبيل الله فيقتلون ويقتلون وعدا عليه في التوراة والإنجيل والقرآن ومن أوفى بعهده من الله فاستبشروا ببيعكم الذي بايعتم به وذلك هو الفوز العظيم))

**Ma'ana:**

*"Haƙiƙa, Allah ya sayi rayukan muminai da dukiyoyinsu daga wurin su a kan suna da aljanna. Suna yaƙi saboda Allah, sai suna kashewa kuma ana kashe su. Wannan alƙawari ne na gaskiya daga Allah a cikin At-Taura da Linjila da Alƙur'ani. Wane ne ya ke cika alƙawari kamar Allah? To, ku yi bushara da cinikinku da kuka yi da shi. Wannan kuma shi ne rabo mai girma".*[12]

Kuma Allah ya ce:

((لكن الرسول والذين آمنوا معه جاهدوا بأموالهم وأنفسهم وأولئك لهم الخيرات وأولئك هم المفلحون * أعد الله لهم جنات تجري من تحتها الأنهار خالدين فيها ذلك الفوز العظيم))

**Ma'ana:**

*"Sai dai shi Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi sun yi jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu, kuma waɗannan suna da alhairai, kuma waɗannan su ne masu rabauta. Allah ya yi ma su tanadin gidajen aljanna*

[12] Suratut Taubah: 111

*waɗanda ƙoramu ke gudana a ƙarƙashin su suna masu dawwama a cikin su. Wannan shi ne babban rabo".*[13]

Kuma Allah ya shelanta ya yarda da su.[14] Su ne kuma Allah ya ba da shedar abin da ke cikin zukatansu na gaskiya da imani.[15] Kuma Allah ya bayyana cewa matsayinsu ya banbanta da na sauran musulmi duka waɗanda ba su ba.[16] Wai shin akwai wata daraja da ta kai tasu bayan Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya ce ya lizimta masu *Kalimatut Taƙwa* (kalmar shahada), ya ce kuma sun fi kowa cancantar ta, da zama ma'abotanta?!.[17]

8. Babu shakka sanin tarihin gwagwarmaya da faɗi-tashin kafa addinin Musulunci da aka yi tun zamanin farko yana haskaka mana tafarkin da ya kamata mu bi wajen tsayar da addinin Allah. Da yawa a yau akwai masu tunanin hanyar gyara ita ce, mu kafa gwamnatin Musulunci, sa'annan - da ƙarfi - mu sa gwamnatin ta gyara mutane. Sai mu ce masu a koma ga kundin tarihi, mu ga yadda shugaban tafiya *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi. Haka lamarin yake ga abubuwa da dama da suka shafi siyasarmu ta da'awa da malanta da makamantansu.

9. Kamar yadda masu kira zuwa ga Musulunci ke samun miƙaƙƙen tafarki a cikin wannan tarihi haka su ma masu tafiyar da mulki da jagororin al'umma da masu fatauci da 'yan ƙwadago da ƙungiyoyin sa kai.. Da maza da mata da manya da ƙanana.. Kai, da ma kowa da kowa.

10. Duk wata matsala da ka shiga a rayuwarka idan ka karanta tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* za ka tarar da wata mai kama da ita da hanya mafi sauƙi ta warware ta. Misali, maraici, talauci, arziki, mulki, matsalolin aure, na tarbiyyar 'ya'ya, ƙalubalen siyasa da fuskantar 'yan adawa da sauran su. Haƙiƙa, duk musulmin da bai san tarihin Manzonsa ba ya yi ma duniya zuwan zomo a

[13] Suratut Taubah: 88-89
[14] Suratut Taubah: 100, Suratul Ma'ida: 6, Suratul Fathi: 18 da kuma Suratul Mujadila: 22
[15] Suratul Anfal: 63, Suratul Fathi: 18-19.
[16] Suratul Hujurat: 7.
[17] Suratul Fathi: 26.

kasuwa.

### 0.3 Wasu Ababen da Wannan Tarihi ya Keɓanta da su

Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya fifita tarihin ma'aikinsa a kan na sauran 'yan Adam da duniya take ji da su ta fuskoki da dama.

1. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* shi kaɗai ne wanda aka haifa a cikin hasken rana, kamar yadda nazarin ƙwaƙwaf ga tarihin 'yan Adam yake tabbatarwa. Abin nufi, babu wani abin da zaka so ka sani game da rayuwarsa wanda ma'abotansa ba su sanar da mu ba. Tun daga rayuwarsa ta cikin gida har zamantakewarsa da masoyansa da magabta. Kai, har abin da mutane ke ɓoyewa na sirrin rayuwarsu, shi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* an bayyana nasa domin shi abin koyi ne ga musulmi fai da boye.
   Dubi yadda aka sifaita mana jikinsa kamar kana zaune a gabansa. Hatta da farin gashin da yake a gemunsa an ƙirge mana yawansa. Motsinsa ko wane iri an bayyana shi a cikin tarihinsa. Tun daga yadda yake zama da tafiya da cin abinci da sa sutura da kawaici da magana da komai da komai. Tambayi mabiyan Annabi Isah *Alaihis Salam* me suka sani game da rayuwarsa? Ballantana duk sauran addinai irin na gargajiya da makamantansu![18]
2. Sai kuma ingancin da kaffatanin wannan tarihi yake da shi. Saboda babu na-ji-na-ji a cikinsa. Kome aka faɗa an san wanda ya cirato shi kuma ta ina ya cirato shi. Don haka in ka ga ana rigima kan wata magana da ta danganci rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* to, ma'abota sani ne ba su zo ba. Yanzu suna fayyace maka kowa ce ruwaya da matsayinta.

[18] Dubi *"As-Shama'il Al-Muhammadiyyah"* na Imam Abu Isa At-Tirmidhi ko kuma *Zad Al-Ma'ad* na Ibnul Kayyim misali ba abin da ba zaka gani ba wanda ya danganci nasa salo na rayuwa wanda shi ne samfurin rayuwar da Allah yake so bani Adama su koya.

3. Ga shi kuma wannan tarihi ya cika ya batse ta kowace fuska. Rayuwar kowa akwai a cikinsa. Karamin yaro, maraya, matashi, dattijo, maigida, talaka, malami, basarake, ɗan kasuwa, jagora, soja, farar hula, liman.. Kai har da ɗan gudun hijira bai rasa abin koyi a cikin wannan tsarkakakken tarihi.
4. Tsaftataccen tarihi ne da ba abin yasuwa a cikin sa. Ko sau ɗaya ba zaka ji wani sharri ko zalunci ko duk wani abin da lafiyayyen hankali yake ƙyama ba a cikin sa. Rayuwa ce ta wanda Allah ya aiko shi don ya zama rahama ga talikai. Dubi duk kaifin adawar mutanen Makka, kai har da algungumai; Yahudawan da suka yi maƙwautaka da shi a Madina. Ka taɓa jin wanda ya tuhumce shi da wata magana ko aiki mai zubar da mutunci?
5. Tare da haka kuma rayuwarsa mai sauƙin koyi ce. Ba ta wuce iya ikon ɗan Adam da aka halicce shi a kai ba. In ban da mu'ujizoji - kamar Isra'i da Mi'iraji - mene ne ɗan Adam ba zai iya kwaikwayon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba a cikin sa?

## Fasali Na Farko:

## 1.1 Halin da Duniya Take Ciki Kafin Bayyanar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*

An samu yankewar isowar saƙon Allah zuwa ga mutane tun bayan ɗauke Annabi Isa *Alaihis Salam* daga duniya da aka yi. Domin kuwa sai da aka yi sama da shekaru ɗari shida ba wani Annabin da aka aiko ma jama'a ya yi gargaɗi a cikin su. saɓanin inda aka fito sa'ad da Annabawa suke zuwa a jere; wani bayan wani. Kai, wasu ma Annabawan a lokaci ɗaya ake aiko su ko dai zuwa ga mutane daban daban ko kuma zuwa ga al'umma ɗaya kamar yadda aka aiko Annabi Musa da wansa Haruna *Alaihis Salam* zuwa ga Banu Isra'ila. Annabi Ibrahim ya kasance Annabin Allah a lokaci ɗaya tare da Annabi Luɗu *Alaihimas Salam*. Haka kuma 'ya'yan Annabi Ibrahim; Isma'ila da Ishaƙa suka yi lokaci guda da shi ga Annabta. Shi ma Annabi Ya'aƙub ya yi lokaci ɗaya da ɗansa Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare su gaba ɗaya). Wannan yankewa ta zuwan wahayi da aka samu ta sanya duniya a cikin duhu ɗib; babu haske ko kaɗan a cikin ta. Bari mu ɗan yi maganar ƙasashen duniya na wancan lokaci don mu ga halin da suka shiga:

### *1.1.6* Kasar Farisa:

Kasa ce da ta samu ci gaba sosai ta fuskar lamarin duniya. Amma ta fuskar addini ƙasar gaba ɗayanta fanko ce. Suna da addinai guda biyu; Zaradishtiyya da Mazdakiyya. Babu na tsinta a cikin su. Abin bautar su babba shine wuta. Ba wanda ya san Allah a ƙasar, balle ya ce yana bautar sa. Kuma mata halas ne ga kowa a wurin su. Mutum zai iya auren uwar da ta haife shi ballantana ƙanwarsa ko kuma 'yar cikinsa. Banbancin addininsu na biyu da wancan na farkon shine su 'yan Mazdakiyya ban da mata ma ko kuɗi kayan kowa ne ba mai mallakar abin kansa, domin a matsayin ruwa da iskan shaƙa suke a wurin su.

### *1.1.7* Kasar Ruma

Wannan kuma ƙasa ce da suka ce suna bin addinin Nasara; kiristanci kenan. Amma ina su ina addinin Annabi Isah *Alaihis Salam* bayan duk an canja addinin an sanya wasa a cikinsa! Littafin ma da Allah ya saukar masa an canja shi an shigar da son zuciya da tatsuniyoyi a cikinsa. Sun maye gurbin Tauhidi da Shirkar nan ta "Allah uku" da aka sani. Ga kuma rikici na cikin gida da ya dabaibaye al'ummar da ke cikin wannan daula na yawan mazhabobin addini marasa sassauci ga junansu.

Mahukuntan waɗannan manyan ƙasashe biyu da muka faɗa sun shahara da zalunci da shan jinin talaka. Akwai wasu ƙananan ƙasashe kuma da ya dace mu yi magana a kan su.

### *1.1.8* Kasashen Turawa

Ban da waɗancan ƙasashe da muka faɗa a baya akwai ƙasashen turawa da kuma Japan, da ƙasar Sin, da Indiya. Su kuma waɗannan ƙasashen rayuwarsu ta fi kama da ta dabbobin dawa a wancan lokaci. Ba abin da ba sa bauta ma, tun daga rana da wata da ruwa da taurari har su shanu da makamantansu. Kai, har Farji ma akwai masu bauta a cikin su. Wai, saboda shi ne mafitar kowa, don haka shi ne Allan! Babu kasuwar da ke ci a cikin su sai ta almara da tatsuniya. Kuma dukan su sun yi imani cewa, ba a tashin ƙiyama. Amma sun yi amanna cewa, duk wanda ya mutu zai sake dawowa duniya a wata sifa daban ba ta mutum ba. Ya'allah kare ko biri ko mage ko dai wani abu daban.

*1.1.9* Akwai kuma Yahudawa waɗanda suka yi kaka-gida musamman a ƙasar Sham (Syria) da Iraƙi da kuma Hijaz (yankin da Saudia take ciki a yau). Su ma dai kamar Nasara sun daɗe da canja addininsu. Kuma sun musanya littafin da Allah ya saukar ma Annabi Musa *Alaihis Salam* da wasu surori da suka ƙago suna karantawa, inda suka mayar da Allah a matsayin ubangijinsu su kaɗai ba da sauran mutane ba. Suna da wani littafi da suka kira *Talmud* wanda suka fifita shi a kan At-Taurah. A cikin sa sun zaɓa ma kansu irin rayuwar da suke ganin ta dace da su a

matsayin zaɓaɓɓun bayi waɗanda Allah ya yi kowa don ya bauta ma su. Haka kuma sun kitsa labarai iri daban daban na cin mutuncin Annabawa da manzannin da Allah ya aiko masu. Sa'annan sun yi fice wajen cin rashawa da algussu a cikin kasuwanci, da kuma kuɗi da ruwa.

***1.1.10*** Sai kuma ƙasashen larabawa waɗanda suke a tsallaken tekun Fasha. Su kuma sun ɗauka cewa addinin Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* suke a kan sa. Kuma haka abin yake can da farko. Amma daga bisani wani basarake daga ƙabilar Khuza'ah[19] ana ce ma sa Amru dan Luhayyu ya yi wata tafiya a yankin Balƙa'a ta cikin ƙasar Jordan don neman magani, sai ya ga mutanen ƙasar sun duƙufa ga bautar gumaka. Daga nan shi ma ya nemi a ba shi izini ya kai wannan baƙar ɗabi'a zuwa yankinsu, sai aka ba shi gunkin "Hubal" ya je ma su da shi suka fara bautar sa.[20]

Daga nan kuma abin ya ci gaba har aka samar da gumaka da yawa, ta yadda ko wace ƙabila ta yi nata gunki, ko wace zuri'a tana da nata. Kai, duk ma wani dutse sai da ya zame ma su abin bauta. Aka cika ɗakin Allah maƙil da gumaka waɗanda adadinsu ya kai gunki ɗari uku da sittin (360). Ba kuma abin da za su yi sai sun nemi izinin gumakan nan ta hanyar yin ƙuri'a a gaban su. Wani dalili kuma da ya ƙarfafi bautar gumaka a wajen mutanen Makka shi ne wata bidi'a da suka ƙago ma kansu wacce Ibnul Kalbi ya ruwaito mana in da yake cewa: *"Mutanen Makka sun kasance duk wanda zai yi tafiya a cikin su saboda girmama haramin Makka sai ya nemi wani dutse daga cikin birnin ya yi tafiya da shi. Duk kuwa inda ya sauka sai ya kafa shi ya rinƙa zagayar sa kamar yadda ake ɗawafin Ka'aba".* Daga kan wannan bidi'ar ne Sheɗan ya ja su zuwa bautar duwatsu. *Wal iyadhu billah.*[21]

---

[19] Khuza'ah su ne ƙabilar da suka kori Jurhumawa - waɗanda suka kafa garin Makka - daga cikin ta, suka kuma shigo da bautar gumaka. Daga baya Allah ya kawo dangin annabinsa a zamanin Kusayyu suka karɓi ragamar tafi da garin na Makka, suka raya shi, kuma suka kula sosai da masu zuwa aikin Hajji.

[20] *Al-Asnam*, na Ibn Al-Kalbi, shafi na 6.

[21] *Al- Asnam*, shafi na 8.

Wani abin da yake da muhimmanci a sani shi ne cewa, larabawa da suka shigo da bautar gumaka sun gauraya addinin su ne da wannan sabon addini da suka kwaikwaya. Saboda haka, ba sa bautar gumakan a matsayin Iyayengiji. Sai dai a cewar su don su kusantar da su zuwa ga Allah mahalicci. Suna cewa: *"Mu ba mu bautar su don kome sai don su kusantar da mu zuwa ga Allah"*.[22] Haka kuma ba su neman kome a wurin su na alƙiyama sai dai abin duniya. Ba su kuma kiran su a lokacin tsanani da matsuwa, kamar idan sun shiga jirgin ruwa. Ga abin da Allah ya ce:

> *"Kuma idan suka hau jirgin ruwa sai su kira Allah suna masu tsarkake ma sa addini*[23]*. A lokacin da ya kuɓutar da su sai ga su suna masu yi ma sa tarayya"*.[24]

Kenan sun yi imani da Allah, kuma suna girmama ɗakinsa. Amma saboda jahilci suka riƙi gumaka a matsayin wani tsani zuwa ga Allah wajen biyan buƙatun duniya. Ya Allah ka raba mu da jahilci.

### 1.1.6 Nahiyarmu ta Afirka:

Ba wani addini saukakke da aka taɓa jin ɗuriyarsa a wannan nahiya daidai lokacin da muke magana a kan sa. Tsafe-tsafe da canfe-canfe da bukukuwan gargajiya su ne addinin mutanen wannan sashe na duniya a lokacin.

A taƙaice dai muna iya cewa, duniya ta koma dulum shekaru sama da ɗari biyar bayan ɗauke Annabi Isah *Alaihis Salam* da mahaliccinsa ya yi zuwa sama. Duniya ko ina ta cika da zalunci. A yayin da jin daɗi da sakewa na neman kashe mahukunta, yunwa da fatara gami da nauyin haraji su kuma sun ci zarafin sauran jama'a bayin Allah. Yaƙi ya game ko ina.

[22] Suratuz Zumar: 3.
[23] Kiran Allah a nan an kira shi addini. Kiran Allah tare da wani kuma an kira shi Shirka. Shi ya sa tsantsar Tauhidi yake nufin kada a kira kowa tare da Allah a wajen neman buƙata.
[24] Suratul Ankabut: 65.

Dokar dawa ita ce tsarin tafi da ƙasashe; mai ƙarfi ya cinye maras ƙarfi babu mai cewa ƙala. Ta fuskar zamantakewa tsakanin jama'a kuwa, mace ba ta da wani matsayi a duniyar wancan lokaci. A ƙasar Indiya sau da yawa mace kan ƙone kanta idan mijinta ya riga ta cikawa don kauce ma irin baƙin ciki da ƙuncin rayuwar da za ta iya shiga a bayan sa. A ƙasashen turawa har jayayya ake yi a kan "ko ita ma mace mutum ce?!!!". A ƙasar larabawa ma ba wani banbanci ke akwai ba. Domin kuwa mutum ya fi son kadaɗe dubin sa sannan ka kwashe shi mari a kan ka yi masa albishir an haifa ma sa 'ya mace.[25] Namiji kuma yana iya auren ko mace nawa ya ga dama. Sannan da rana tsaka balarabe yakan iya rufe 'yarsa ta cikinsa a ƙarƙashin ƙasa da ranta da lafiyarta saboda tsabar jahilci. Dalili wai, kada ta girma ta janyo ma sa abin kunya! Ko kuma ya kashe ta kawai saboda tsoron talauci domin ita 'ya mace ci-ma-kwance ce ba ta noma ba ta yaƙi balle ta nemo abinci. Kai, in ban da shan giya da dara da caca ba abin da larabawa suka sa gaba.

A daidai wannan lokacin ne Allah cikin rahamarsa ya kalli banu Adama da idon rahama, ya yada ma su haske wanda zai tsamar da su daga ɗimuwa da gigita ya mayar da su cikin hayyacinsu, ya aza su ga godabe miƙaƙƙe da zai samar ma su jin daɗin rayuwa a duniya da kyakkyawar makoma a gobe ƙiyama. A nan ne Allah ya ƙaddara haifuwar Manzon ƙarshe Muhammadu ɗan Abdullahi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*.

[25] Alƙur'ani mai girma, Suratun Nahl:58 da kuma Zukhruf:17.

### 1.2 Muhammadu Zaɓen Allah

A daidai wannan lokacin da muke magana a kan sa labari ya fara game ƙasashen larabawa cewa, wani Annabi ya kusa bayyana wanda zai ceto mutane daga halin la-haula da suka shiga cikin sa. Don haka, sai aka samu wasu bayin Allah suna gurin cim ma wannan matsayi kuma har suna yunƙurin kiran mutane zuwa ga gyara. Daga cikin su akwai Umayyatu ɗan Abus-Salti wanda Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce kaɗan ya rage ya musulunta saboda irin kalaman tauhidi da kushe Shirka da ke fita bakinsa.[26] Akwai kuma Amru ɗan Nufailu wanda ya rinƙa hana mutane rufe 'ya'yansu mata suna ji suna gani da rayuwarsu. Akwai Kussu ɗan Sa'idata wanda aka ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya saurari jawabinsa a kasuwar baje kolin fasaha da ake yi shekara shekara a Ukaza. Duka waɗannan ko wanen su ya yi fatar kasancewa shi ne Manzon ƙarshe da Allah zai aiko. Wannan daga ɓangaren larabawa kenan.

Yahudawa, musamman mazauna Madina daga cikin su, su ma sun yi irin wannan hasashen na bayyanar sabon Manzo, dogaro da abin da suke karantawa a cikin At-Taurah. Amma fa a zatonsu lalle ne wannan Annabi ya bayyana daga cikin su tunda yake tun bayan wucewar Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* babu wani Annabi da aka taɓa aikowa sai daga gidansu. To, sai dai kamar yadda bahaushe ke cewa, ana zaton wuta a maƙera sai ta ɓulla a masaƙa. A wannan karon Maɗaukakin Sarki ya kauce ma gidan Banu Isra'ila zuwa gidan 'ya'yan baffansu Banu Isma'ila. Daga cikin wannan tsarkakakkiyar zuri'a ta Isma'ila ne Allah ya zaɓi gidan Kinanata. Daga zuri'arsa sai ya zaɓi Kuraishawa. Daga cikin su kuma ya zaɓi Banu Hashim. A cikinsu ne gwanin sarki Allah ya zaɓo fiyayyen halitta, shi ne Muhammad ɗan Abdullahi *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, bawan Allan da bai taɓa mafarkin samun wannan matsayin ba duk da yake shi ne ya cancance shi. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* yana cewa:

((وما كنت ترجو أن يلقى إليك الكتاب إلا رحمة من ربك، فلا تكونن ظهيرا للكافرين))

[26] *Sahih Muslim* 7/49

Ma'ana:

> *"Ba ka kasance kana tsammanin a aiko ma ka wannan littafin ba, sai dai jinƙayi ne kawai daga ubangijinka. Don haka kada ka zama mai goyon bayan kafirai".[27]*

Kuma yana cewa:

((الله أعلم حيث يجعل رسالته))

Ma'ana:

> *"Allah shi ne wanda ya fi sanin a ina ne ya ke sanya saƙonsa" suratul An'am: 124.*

To, da yake a can baya mun yi maganar halin da duniya take ciki na jahilci da son zuciya, tambayar da ya kamata mu mayar da hankali gare ta a nan ita ce, me ya sa addini ya ɓulla a yankin larabawa?! Ko kuma mu ce, me ya sa Allah ya zaɓi labarawa da wannan alheri daga cikin sauran bil Adama na ƙasashen da muka zayyana?

### 1.3 Me ya sa Aka Zaɓi Yankin Larabawa?

Duk abin da Allah maɗaukaki ya yi ba za a rasa wata gwaninta ba ko kuma wata hikimar da take tattare da shi. Ko dai mu bil Adama mu gano haka ko kuma basirarmu ta kasa ganewa. Amma game da lamarin fitar da manzanci daga yankin larabawa hikimar a fili take, ba ta ko buƙatar wani dogon tunani. Muna iya lura da dalilai kamar haka:

1. Duk da yake duniyar duka ta rikice, babu wasu jama'a da suke kusa da tsarin halittar Allah ga ɗan Adam kamar su larabawa. Ina nufin su mutane ne masu kama da farar takarda wacce take jiran a rubuta duk abin da aka ga dama a kan ta. Su dai sun yarda cewa ba su sani ba, kuma suna neman a sanar da su. Ba zaka haɗa waɗannan ba

[27] Suratul Kasas: 86.

da waɗanda suke ganin suna kan wani ilimi har suna jayayya a kan sa alhalin ilimin nasu na-jabu ne.

2. Dalili na biyu shi ne irin kyawawan ɗabi'unsu da suka zarce sauran mutane da su a wancan lokaci. Domin kuwa duk da kasancewar su ma'abota shan giya da caca da sauransu, amma suna da karimci matuƙa[28] da kunya da sadaukar da kai da jarunta.[29] Sa'annan mutane ne masu kaifi ɗaya; ba sa ƙarya. Ga kuma tsananin cika alƙawari[30] kuma ba su ɗaukar wulaƙanci.[31] A waɗannan halaye da muka faɗa ba wata al'umma da ta kama ƙafar su. Haka kuma suna da tsarkin zuciya ga duk abin da suka ba da gaskiya da shi. Wannan ya sa suka yaƙi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bilhaƙƙi sa'ad da ba su fahimce shi ba. A lokacin da kuwa gaskiya ta yi halinta sai suka zamo su ne baraden Musulunci.

3. Ga kuma yanayin ƙasar tasu ita kan ta, wacce take tsakiyar duniya mai ɗauke da mutane a wancan lokaci. Don haka yaɗuwar addinin Musulunci zuwa sauran sassan duniya zai fi sauƙi a nan bisa ga ko ina daga sauran ƙasashe.

---

28 Balarabe kan iya shiga ko wace irin wahala don tara abin duniya, amma bai taɓa jin wahalar fitar da shi ya yi kyauta ko ya yi taimako in dai za a yabe shi ko da a bayan mutuwarsa. Wannan ya sa sahabbai ba su samu damuwa ba sam wajen taimakon musulunci da dukiyarsu tun da yake daman halinsu ne da suka saba.

29 Al-Alusi ya kawo labarai daban-daban a kan sadaukantaka da jarunta da karimcin larabawa a cikin littafinsa *"Bulug Al-Arab Fi Ma'arifati Ahwal Al-Arab"*, juzu'i na ɗaya. Sai a duba shi.

30 An ba da labarin Harisu ɗan Abbad jagoran ƙabilar Bakar lokacin da suka yaƙi Taglibawa. Harisu ya kama shugaban rundunar Taglib wanda ake ce ma Muhalhil amma bai san shi ba. Sai ya ce ma sa nuna min Muhalhil in sake ka. Muhalhil ya ce ma sa, tsakanin ka da Allah in na nuna ma ka shi zaka sake ni? Ya ce, eh. Ya ce, to, ni ne Muhalhil! Harisu ya ce, kash! Amma ka cuce ni. Haka kuma ya sake shi saboda saɓa alƙawari abin kunya ne babba a wurin su. Duba: *Al-Kamil Fi At-Tarikh*, 1/536

31 Mutuwa ta fiye ma su sauƙi a kan ɗaukar wulaƙanci. Labarin sarki Amru ɗan Hindu - sarkin Hiyra - wanda ya rasa ransa a hannun Amru ɗan Kulsumu – wani talaka - a kan sarkin ya sa uwarsa ta nemi uwar Amru ta ɗauko ma ta faifai. A lokacin da uwar sarki ta umurce ta da yin haka sai kawai ta ƙwala ihu! Tana faɗin "Wayyo Allah, an wulaƙanta ni!". Jin haka kawai Ɗan Kulsumu sai ya fille kan sarki. Wannan labari ya ishe mu misali a kan yadda larabawa suka saba da 'yanci da rashin ɗaukar wulaƙanci tun kafin zuwan musulunci.

4. In ka haɗa wannan da kasancewar daman can akwai ɗakin Allah na farko a garin Makka, wanda kuma waɗannan bayin Allah suke girmama shi matuƙa har ba sa bari ayi ko wane irin faɗa ko tashin hankali a kewayensa.

5. Larabawa sun kasance suna riƙe da sauran addinin Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* duk da shigar da maguzanci da suka yi a cikin sa. Misali, suna wankan janaba, suna jana'iza, suna azumi a ranar Ashura. Idan kuma ka kalli yanayin auratayya da hukuncin saki da na diyya a wajen su zaka san lalle suna da sauran abin da ya rage ma su na addinin gaskiya. Daga cikin abin da suke a kan sa na addinin Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* akwai aikin Hajji da Umra - ko da kuwa sun yi ɗawafi tsirara a wasu lokuta. Ko da kuma ƙabilar Kuraishawa sun ƙi fita Arafat don ji-ji-da-kai.[32]

6. Yaren da suke amfani da shi; larabci, shi ne wanda Allah a cikin hikimarsa ya sanya shi ya zamo yaren da za a isar da saƙonsa na ƙarshe da shi. Masana kuwa a fannin harsuna sun tabbatar cewa, babu wani yare da ya kai matuƙa wajen fito da saƙo a yadda ake son sa kamar shi.[33]

Idan ka kalli waɗannan dalilai da muka kawo za ka hango hikimar gwanin sarki da ya tashi Manzonsa a wannan waje, kuma a tsakanin waɗannan mutane. Babu shakka, Allah *Ta'ala* ya yi babbar ni'ima ga waɗannan bayi nasa; larabawa da ya ɗora ma su wannan nauyi. Suna a cikin halin rauni sai ya ƙarfafa su. Suna jahilai ya ilmantar da su. Suna talakawa ya wadatar da su. Suna a rarrabe sai ya haɗa kansu. Suna a matsayin sifili a cikin duniya ya mayar da su su ne kowa. Suka kawar da manyan daulolin da ke ci a cikin ɗan ƙanƙanen lokaci. A hankali kuwa sai addinin Musulunci ya game sassan duniya baki ɗaya. Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai.

---

[32] To ka ga bayyanar musulunci a wannan wurin a gyara kurakuransu ya fi tasowar sa daga wani wuri domin koya ma mutane addinin da ba su san makamarsa ba.

[33] Idan ka zo fassara waɗannan kalmomin daga larabci zuwa Turanci أنتَ، أنتِ، أنتما، أنتم، أنتنّ ba abin da zaka samu ban da "You". Ka ga fasahar ba ta zamo ɗaya ba!.

## 1.4 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Samu Gagarumar Nasara

Tun a lokacin da Mushrikai a garin Makka suka kasance suna nuna tirjiya; suna na-ƙi-na-ƙi da saƙon Manzon Allah, Allah Maɗaukakin ya faɗa masa kada ya karaya, ya sani nasara tana nan tafe. Saboda akasarin waɗanda suke adawa da shi ba suna yi ne bisa ƙin gaskiya ba, sai dai rashin fahimtar ta, kuma a hankali yau da gobe za su gane cikin yardar Allah. Allah *Subhanahu wa Ta'ala* yana ce ma Manzonsa:

**((عسى الله أن يجعل بينكم وبين الذين عاديتم منهم مودة، والله قدير والله غفور رحيم)) سورة الممتحنة: ٧**

**Ma'ana:**

> *Abu mai yiwuwa ne Allah ya sanya soyayya a tsakanin ku da waɗanda kuka ƙi. Kuma Allah mai cikakken iko ne, kuma Allah mai gafara ne, mai jinƙai.*
>
> *Suratul Mumtahana: 7*

A cikin wannan tarihi da za mu karanta za mu ga ƙarfin tasirin da'awar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a cikin waɗannan bayin Allah. Wani wuri za ka ga abin tausayi, wani wuri da ban sha'awa, wani ma sai ya sa ka tuntsure da dariya. Bari mu ɗan ba da 'yan misalai kaɗan daga cikin waɗanda suka cije da farko a kan kafirci, amma kuma Allah cikin rahamarsa ya sauya zukatansu; suka musulunta suka dawo cikin Baraden Musulunci:

1. Kafin musuluntarsa, halifa na biyu na Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kasance mai tsananin adawa ga Musulunci da Musulmi. Amma kuma a cikin ɗan ƙanƙanin lokaci ya koma daga cikin na hannun daman Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, bayan da Allah ya karɓi addu'ar da *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi a kan sa. Babu irin gudunmawar da bai bayar ga Musulunci ba a Makka. Haka ma babu yaƙin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya fita yi ba tare da shi ba. Ya samu albarkar surukuta da

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, sa'annan kuma da Sayyida Fatima wacce ya auri 'yarta Ummu Kulthum a zamanin halifancinsa.

2. Dubi kuma yadda Abu Sufyana ya kasance a cikin masu gaba da Annabi har iyakar zaman sa a birnin Makka. Har a bayan Hijira ma yana cikin waɗanda suka jagoranci faɗa da Musulunci. Amma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai gushe ba yana rarrashin sa har in da aka ci Makka. A wannan ranar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya mutunta shi matuƙa inda ya sa aka yi shelar cewa, duk wanda ya shiga gidan Abu Sufyan an amintar da shi. Kafin haka, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya auri 'yarsa wacce ta musulunta kuma ta yi Hijira tare da mijinta bayan da Allah ya yi ma mijin nata cikawa a can Habasha. Daga ƙarshe dai Abu Sufyana ya dawo a sahun Musulmi kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da kansa ya ba shi tutar yaƙi don faɗa da kafirci.
3. Khalid bn Walid shi ne wanda ya janyo samun matsalar Musulmi a Uhud bayan da ya jagoranci rundunar Mushrikai wadda ta zagayo dutsen Uhud ta yi masu ƙawanya. Daga baya kuma shi ne wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya umurce shi ya rusa gunkin Lata da Uzza, ya aiwatar da umurnin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana mai kabbara yana alfahari da haka.
4. Amru bn Al-Ass shi ne jekadan Kuraishawa zuwa ga Sarkin Habasha, inda yaje ya yi jayayya mai ƙarfi don kariyar kafirci a gaban Najashi, da manufar a dawo da Musulmi 'yan gudun Hijira zuwa Makka don su ci gaba da azabta su. Daga bisani Amru ɗin ne ya zama jakadan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zuwa ga Sarkin Oman.
5. Urwatu ɗan Mas'ud
6. Suhailu ɗan Amru shi ne jakadan Mushrikai wajen tattaunawa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a Hudaibiyya, kuma shi ne ya gitta ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sharuɗan nan da suka so su raba

kan Musulmi a wancan lokaci ba domin Allah ya tsare ba. Daga bisani ya musulunta. Idan ka ji huɗubar da Suhailu ya yi a ranar cikawar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zai ba ka tausayi matuƙa. Kuma za ka gane ƙarfin tasirin da Musulunci ya yi a cikin zuciyarsa.

7. Ɗufailu ɗan Amru shi ne wanda yake sanya auduga yana liƙe kunnuwansa don kada ya ji kiran Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Amma daga bisani idan ka ji yadda Allah ya ɗaukaka shi a fagen da'awa al'amarinsa zai ba ka sha'awa.

8. 'Ya'yan Abduyalil waɗanda suka sa aka koro Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* daga garin Ɗa'if aka yi masa jifar wulakanci har aka zubar masa da jini, duk sun musulunta kuma sun taimaki addini daga baya.

9. A lokacin Hijirar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zuwa Madina, Buraidatul Aslami ne ya jagoranci ayarin mutane saba'in da suka fita don bin sawunsa da manufar su kama shi su dawo da shi Makka da rai ko matacce! Amma daga bisani yana cikin masu shiga gaban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ɗauke da tuta a wuraren yaƙi don kakkaɓe kafirci.

10. Haka ma zamu ga sarakuna da dama a wancan lokaci sun karɓi Musulunci, sun ƙarfafe shi, kuma sun yaɗa shi a cikin jama'arsu. A cikin su akwai As'himatu; Najashin Habasha da Ukaidiru; Sarkin Dumatul Jandal da kuma Jafari; Sarkin Oman.

## 1.5 Matsayin Birnin Makka da Darajarsa

Kamar yadda Allah ya zaɓi wasu mutane ya ba su fifiko a kan wasu, haka su ma garuruwa da birane Allah ya fifita wasu a kan wasu. Idan kuwa ana maganar ƙasashe da manyan biranensu to, Makka ita ce "Ummul Kura" uwar birane da nassin Alƙur'ani.[34] Gari ne da Allah ya sanya aminci da kwanciyar hankali a cikinsa. Alƙibla

[34] Suratul An'am: 92 da Suratus Shura:7

ce ta musulmi a duk inda suke a duniya. Zukatan muminai a ko ina suna karkata zuwa ziyarar sa. Kuma idan sun koma gidajensu nan take sai su buƙaci komawa.[35] A nan ne ɗakin Allah na farko da aka gina don ibada yake. A jikinsa akwai *Hajarul Aswad* daga cikin duwatsun aljanna. Shi ne kaɗaitaccen wuri da aka amince ma musulmi ya shafa da sunan ibada. Sallah a wannan gari tana da ƙarin matsayi sama da ninki 100,000 a kan wani gari duk da ba shi ba. Sai dai masallacin Manzon Allah. Shi ma Makka ta fi shi da sama da ninki ɗari a ladar sallah.

((إن أول بيت وضع للناس للذي ببكة مباركا وهدى للعالمين * فيه آيات بينات مقام إبراهيم ومن دخله كان آمنا)) آل عمران:٩٦،٩٧

**Ma'ana**

> *Haƙiƙa gida na farko da aka gina domin mutane (su yi bautar Allah a cikin sa) shi ne wannan da yake a Bakka (Makka), mai albarka ne kuma shiriya ga mutane. A cikin sa akwai ayoyi bayyanannu ga talikai; matsayin Ibrahim. Wanda duk ya shiga a cikin sa ya zama amintacce.*[36]

Ba a zubar da jini a birnin Makka. Ba a farauta ko tada hankalin tsuntsu balle bil-Adama. Ba a cire ganye daga bishiya. Ba a ɗaukar tsintuwa sai idan za a cigita.[37] Bukhari da Muslim sun ruwaito hadisi daga ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhu* daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa, Allah ya haramta Makka, bai taɓa halalta ma kowa yin yaƙi a cikin ta ba gabani na, haka ma ba zai halalta ma kowa ita ba a baya na. Ni ma awa ɗaya ce daga cikin wuni aka halalta ma ni. Don haka, ba a tsinke ganyenta, ba a yanke bishiyarta, ba a korar dabbar farauta a cikinta, ba a ɗaukar tsintuwarta sai ga wanda zai yi cigiya". Sai Abbas *Radhiyallahu Anhu* ya ce "A cire ma na *Idhkhir*; bishiyar da muke yin rini da ita, kuma muke amfani da ita wajen rufe matattunmu". Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, "To, ban da ita".

---

35 Suratul Baƙarah:125

36 Suratu Ali Imran: 96-97.

37 Suratun Naml:91.

Albarkacin addu'ar Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* a kullum ana samun ko wane nau'in abinci da kayan marmari a birnin Makka.[38] A ƙarshen zamani kuwa idan Dujjal ya bayyana, Allah zai tsare wannan birnin daga ƙazantar takon ƙafafunsa kamar yadda ya tsare shi daga sharrin rundunar Giwaye. Zamu yi maganar wannan runduna a nan gaba kaɗan in Allah ya so.

Bukhari da Muslim sun karɓo hadisi daga Anas ɗan Malik *Radhiyallahu Anhu* daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa, "Babu wani gari da Dujjal ba zai shiga ba sai Makka da Madina. A lokacin bayyanar sa babu wata kafa a cikinsu (Makka da Madina) sai Mala'iku sun yi sahu a kai suna kare ta. Sa'an nan Madina zata yi girgiza uku da mutanen da ke cikin ta. Duk wani munafiki ko kafiri sai ya fita".[39]

A wannan tsarkakakken gari ne aka haifi shugabanmu kuma shugaban ma'aika Muhammadu ɗan Amina, *Sallallahu Alaihi wa Sallam*.

### 1.6 Shekarar Giwaye

Shekarar haifuwar fiyayyen halitta ita ce ake ce ma shekarar Giwaye. Abin da ya faru a wannan shekarar kuwa (shekara ta 571Miladiyya) shi ne, an yi wani sarki a garin San'a'a ta ƙasar Yemen wanda ake kiran sa *Abrahata Al-Ashram*. Ya kuwa mulki wannan garin ne a bayan da ya rinjayi *Aryaɗ* wani naɗaɗɗen sarki daga fadar Najashi na ƙasar Habasha. Wannan juyin mulki da ya yi kuwa ya fusata Najashi ainun, al'amarin da ya rikita Abrahata ya sa ya fara 'yan kame-kame don neman kuɓuta daga sharrinsa. A kan haka ne ya aike masa da saƙon cewa, zai gina wani babban ɗakin ibada a bisa tafarkin addininsa mai Kuros (Coci) wanda ba a taɓa jin labarin irin sa ba. Ya kuwa ɗauki alƙawarin idan ya kammala wannan Coci zai juya hankalin larabawa da suke yin tururuwa suna bi ta ƙasarsa don ziyartar ɗakin Allah da ke Makka. Abrahata ya gina wannan Cocin ya kuma ƙawata ta matuƙa bayan ya kashe maƙudan kuɗaɗe. A zatonsa idan larabawa suka gan ta hankalinsu zai raja'a gare ta su

[38] Suratul Baƙarah:126
[39] *Sahih Al-Bukhari,* Littafin Fitinnu, Babin ambaton Dujjal, Hadisi na 7125.

bar Ka'aba. Da wannan shi kuma sai ya samu ɗaukaka ma kansa da birninsa na San'a'a. Ya janyo ƙarin kasuwanci da ciniki ta hanyar 'yar ziyara sai ya bunƙasa tattalin arzikin ƙasarsa. Ga shi kuma idan haka ta samu ya kuɓuta daga sharrin Najashi tun da ya juya hankalin larabawa zuwa bautar Almasihu. Da haka sai ya yi fatar ya jefi tsuntsu biyu da dutse ɗaya.[40] To, amma ga alama ko tsuntsu guda bai samu ba. Domin kuwa ko da suka ahamo sai ga wannan coci an yi ma ta kaca-kaca da najasa! To, wa zai yi ibada a gida maras tsarki, wanda ba shi da alfarma da za ta kare shi daga wannan wulaƙanci?! Ai kuwa gogan naka sai ya shaci fushi ya yi rantsuwa sai ya rusa Ka'abar da ke Makka tun da yake larabawa ake tuhuma da yin ta'adi a kan wannan Coci. Ya shirya runduna wacce larabawa ba su taɓa jin irinta ba. A cikin ta har da Giwaye. Ya kuma jagoranci rundunar da kansa. Kafin isowar sa birnin Makka labari ya game sassa. Kuma duk wani yunƙuri da larabawa suka yi domin yin arangama da shi da hana shi isa Makka sai da ya ci tura. Amma fa sun yi amanna cewa, Allah shi ne mai wannan ɗakin kuma ba zai ƙyale shi ba.[41] Da rundunar Abrahata ta iso Ɗa'ifa sai suka ɓace hanya. Kuma duk wanda suka tambaya sai ya ƙi ɗora su a kan hanya. Sai da suka samu wani shaƙiyyin mutum mai suna *Abu Rigal* shi ya yi masu jagora zuwa Makka. Ba su yi nisa ba sai Mala'ikan mutuwa ya sharɓe shi. Shi ne wanda larabawa ke jifar ƙabarinsa har inda yau ke magana a wani ƙauye da ake kira Mugammas a hanyar Ɗa'ifa zuwa Makka.[42] Allah sarkin sarauta! Ashe dai ko ina akwai marasa arziki a cikin duniya.

A lokacin da Abrahata ya isa Makka sai mutanen garin duk suka taru wurin ɗakin Allah suka maƙalƙale gare shi suna kai ƙara ga ma'abocinsa. Sa'annan suka fice daga garin suna jiran faruwar ikon Allah gwanin sarki! A lokacin da ayarin Abrahata ya sauka wajen gari, Abdulmuɗɗalib ya samu ganawa da shi in da ya nemi a mayar ma sa da raƙumansa guda 200 da wannan runduna ta mamaye. A cikin ta'ajjubi

---

[40] *Mausu'at At-Tarikh Al-Islami*, na Dr. Ahmad Shalabi, 1/119-120

[41] A kan hanyarsa ta zuwa Makka, ƙabilun larabawa da dama sun tare Abrahata kuma suka yaƙe shi amma ya tarwatsa su. Tun daga ƙasar Yemen wani sadauki da ake kira Zu-Nafar ya ci karo da shi tare da rundunarsa amma tuni giwaye suka tattaka su. Kabilun Khas'am; Shahran da Nahis su ma sun tura ma sa wasu jarumawa amma aka fatattake su.

[42] *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Hisham 1/58-60.

Abrahata ya tambaye shi, raƙumanka ne suka fi ma ka muhimmanci ko wannan ɗaki da ka gaji ibada a cikin sa tun daga kaka da kakanni?! Sai Abdulmuɗɗalib ya kada baki ya ce ma sa: "Ba haka ba ne. Raƙuma mallakina ne, shi ya sa nake neman abina. Shi kuma wannan ɗaki yana da mai shi kuma zai kare shi. Ba zai bari kome ya same shi ba".[43]

Kangara irin ta kafirci ta sa Abrahata duk da jin wannan magana bai karaya ba balle ya fasa abin da ya yi niyya. Amma ya mayar ma da Abdulmuɗɗalibi duk dukiyarsa da aka riga aka ƙwace can da farko. An ba da labarin cewa, su waɗannan Giwaye sun turje a bayan garin Makka duk lokacin da aka fuskantar da su zuwa garin. Amma idan aka karkata su zuwa hanyar komawa sai su zura da gudu. Kaico! In da akwai basira da kafirai sun gane wannan ishara. Amma ina! Da suka ci gaba da nacewa a kan shiga garin ne sai Allah ya aiko ma su wasu irin tsuntsaye masu manyan kawuna waɗanda ba a taɓa ganin irin su ba, suna ɗauke da duwatsun wuta suna jifar su da su. Duk wanda suka samu kuwa ba shi kai labari. Da haka suka tarwatse rundunar kowa ya san in da dare ya yi ma sa. Shi kam uban tafiyar; Abrahata faɗuwa ya yi a tagayyare duk jikinsa ya lalace. Suka ɗauke shi suka koma da shi gida yatsunsa na sancewa guda guda, ya cika a nakkashe. Allah ya wulaƙanta shi.[44]

Faruwar wannan al'amari da muka faɗa na korar rundunar Abrahata da Mai-sama ya yi ya daɗa sanya larabawa su san girman ɗakin Allah, su kuma mutunta mazauna birnin Makka. Har ta kai ma ko ana fashi da makami ayarin Makka zai wucewar sa salun alun a ɗauke da dukiya mai ɗinbin yawa ba wanda zai tare su don matsayin da suke da shi a zukata. A cikin shekaru arba'in za ka so ka ga irin ƙarin kwarjini da muhibba da wannan birni na Makka yake da shi da yawan alhazai masu zuwa girmama shi. Ashe dai akwai abin da Allah ya nufa na jawo hankalinsu zuwa ga wannan gari domin a daidai lokacin ne alfijir yake ketowa; fitilar da zata haskaka duniya ta bayyana a wannan gari mai tarin kwarjini da albarka.[45]

---

43 *Tafsir Al-Kur'an Al-Azim* na Ibn Kathir (8/485).

44 *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Hisham 1/58-60 da *Fath Al-Bari* 12/210-216

45 *Rasulullah Fi Makka,* na Dr. Yahya bn Ibrahim Al-Yahya, shafi na 66.

## Fasali Na Biyu:

## 2.0 Tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* Daga Haifuwa Zuwa Manzanci

### 2.1 Sunansa da Asalinsa:

Cikakken sunan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* shi ne: MUHAMMAD[46] ɗan ABDULLAHI ɗan ABDULMUƊƊALIB[47] ɗan HASHIM.

Hashim babban mai arziki ne wanda ya sarrafa dukiyarsa gaba ɗaya wajen taimakon mutane. Zanannen sunansa ma shi ne Amru, amma an yi ma sa laƙabi da Hashim ne saboda yawan ciyar da abinci ga bayin Allah da yake yi. Shi ne kuma wanda ya tona rijiyoyi a cikin garin Makka don sawwaƙe ma mutanen gari matsalar ruwan sha da kuma sawwaƙe aikin da ake yi a gidansu na bin alhazai har a masaukansu ana ba su ruwan sha kyauta. Don ci gaban tattalin arzikin jama'arsu, Hashim shi ya faɗaɗa kasuwancin mutanen Makka daga kasuwancin cikin gida zuwa na ƙasashen waje. Ya ƙago abin da ake kira *Ilaf* in da ake haɗa ayari sau biyu a kowa ce shekara don kai haja a tallata a ƙasashen waje da kuma sawo wasu hajojin da ake buƙata daga can. Allah ya faɗi wannan tafiyar tasu a cikin suratu Kuraish. Da haka ne Hashim ya zamo jakadan larabawa a ƙasashen ƙetare wanda yake ƙulla duk wata yarjejeniya ta taimakon juna ko zaman lafiya da sauran ƙasashe.[48]

HASHIM ɗan ABDU MANAFI[49] ne ɗan KUSAYYU

Kusayyu ana ce ma sa Zaidu. Shi ne ya gina *Mash'arul Haram* a Muzdalifa inda alhazai ke taruwa in sun sauko daga Arafat domin hutawa da kuma ambaton Allah. Sannan kuma shi ne ya haɗa kan Kuraishawa, ya tsara al'amarinsu. Kuma shi ne ya

---

[46] Ma'anarsa: abin godewa. Ba a taɓa jin wannan suna ba a gabanin sa. Wannan suna yana da rassa. Su ne, Mahmood da Haamid da Humaid da Hamdaan.

[47] Sunansa na yanka shi ne SHAIBA. Zamu faɗi dalilin kiran sa Abdulmuɗɗalib

[48] *Mausu't At-Tarikh Al-Islami*, na Shalabi, 1/182.

[49] Sunansa na yanka shi ne MUGHIRA

fara hidimar baƙi masu zuwa aikin Hajji har ya samar da wasu ma'aikatu don kula da su. A cikin Waɗannan ma'aikatun ne ya sanya 'ya'yansa suna hidimar ɗebo ruwan sha daga rijiyoyin da ke wajen gari don shayar da alhazai kyauta. Haka kuma suna raba abinci ga mahajjata bayan sun tattara shi daga hannayen mutane tun kafin isowar baki wurin aikin Hajjin.[50]

KUSAYYU ɗan KILABU[51] ne, ɗan MURRATA ɗan KA'ABU

Ana ce ma Ka'abu Abu Husais. Yana daga cikin manyan mutane da larabawa ke bugun gaba da su. Shi ne ya fara haɗa jama'a a ranar jum'ah. A lokacin suna kiran ta "Yaumul Uruba"; ranar larabawa.

KA'ABU shi ne ɗan LU'AYYU ɗan GALIBU ɗan FIHIRU.

FIHIRU shi ake kira Kuraishu, wanda kuma gare shi ake jingina ƙabilar gaba ɗayanta ana cewa Kuraishawa. Babban barde ne wanda ya ci galaba a kan wani gwarzo da ake kira Hassan Al-Himyari a lokacin da ya zo da niyyar ya kwashe duwatsun Ka'aba don ya mayar da su ƙasar Yemen. Wasu kuma suka ce asalin wannan sunan na wani mahaukacin kifi ne da ya tare ayarin larabawa suna tafiya a cikin jirgin ruwa, saman teku. Sai mutane suka firgita matuƙa a kan sa. Ba tare da ɓata lokaci ba wannan sadauki daga cikin kakannin fiyayyen halitta ya fitar da kibiya ya jefa masa. Cikin ikon Allah sai kibiyar ta kafe kifin. Da jirgi ya kusanto wurin da Kuraishu yake kafe ba tare da tsoro ba Bayajidan larabawa ya sa takobinsa ya farke cikinsa, ya kuma gutsure kansa. Sannan ya nemi taimakon jama'a suka shigar da namansa a jirgi suka isa da shi Makka. Daga nan ne aka sa ma sa wannan suna Kuraish; sunan kifin da ya hallaka wanda ya tashi hallaka ayarinsu.[52]

---

[50] Duba *An-Nasabu Wal Musahara*, na Ala'uddin Al-Mudarris, bugun Mu'assasatul Mukhtar, Alƙahira, 2005, shafi na 59.

[51] Sunansa na yanka shi ne HAKEEM ko kuma URWA, amma laƙabinsa ya rinjaye shi. An yi ma sa laƙabi da Kilabu ne saboda yana zuwa farauta da karnuka

[52] Duba *Subh Al-A'asha* na Kalƙashandi, 1/352 da kuma *Ayyam Al-Arab Fi Al-Jahiliyyah*, na Muhammad Jad Al-Maula.

FIHIRU ɗan MALIKU ne, ɗan NADHRU[53] ɗan KINANATA ɗan KHUZAIMATA ɗan MUDRIKATA[54] ɗan ILYASU[55] ɗan MUDHARU[56] ɗan NAZARI ɗan MA'ADU[57] ɗan ADNANA.

Adnana shi ne kaka na 20 ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Kuma iyakacin abin da ake da tabbacinsa kenan dangane da nasabarsa. Amma an tabbata cewa, shi Adnana jika ne ga Annabi Isma'il ɗan Annabi Ibrahim *Alaihimas Salam*. An kuma ce Isma'il *Alaihis Salam* shi ne kakan Adnana na 38. Shi kuma Isma'il shi ne jikan Annabi Nuhu na 11. Idan muka lisafta za mu ga tsakanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Annabi Nuhu *Alaihis Salam* akwai kakanni saba'in cif har da mutum uku. Amma fa inganci da tabbaci yana ga iyaye ashirin na farko da muka faɗa daga mahaifinsa Abdullahi zuwa Adnana.[58]

## 2.2 Babba Ɗan Manyan Mutane

Wannan salsala da muka faɗa tsarkakakkiya ce; ɗan halas bayan ɗan halas. Babu wanda aka haifa ta hanya gurɓatacciya. Wannan gidan da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya fito daga cikin sa kuwa, babban gida ne mai daraja da alfarma kamar yadda muka gani. Iyayensa da kakanni duk muhimman mutane ne; daga babban sadauki sai cikakken barde, sai wanda ya fara wani aikin ibada kamar Hadaya da gina *Mash'arul Haram* da tufatar da Ka'aba, sai wanda ya haɗa kan jama'a, ko ya gyara ma su tattalin arziki ko ya ƙago ma su wani aikin alheri kamar hidimar baƙin Allah da raba ma su ruwan sha da abinci kyauta. Ga shi kuma a gidansu ne Kuraishawa suke haɗuwa domin tattauna mas'alolin ci gaban al'ummarsu. Su kuma ke

53 Sunansa na yanka shi ne KAISU
54 Sunansa na yanka AMIR
55 Shi ne mutum na farko da ya fara Hadaya; sadaukar da dabba a yanka ta don girmama ɗakin Allah.
56 Mutum ne mai kyakkyawar murya. Shi ya fara *Hida'u;* irin shewar da ake ma raƙuma don su samu kuzarin tafiya.
57 Gwarzo ne, sadauki; da ba a taɓa ka da shi ba a wurin yaƙi.
58 *Ar-Rahiƙ Al-Makhtum,* shafi na 57-58.

ɗaukar tuta idan yaƙi ya kama da abokan gaba. A dalilin mahaifinsa ne diyya ta tashi daga raƙumi goma zuwa raƙumi ɗari kuma shari'ar Musulunci ta zo ta tabbatar da hakan kamar yadda za mu gani a nan gaba.

### 2.3 Haɗuwar Dare Ɗaya Tarihin Har Abada

A cikin tafiyar da yake yi ta neman arziki, wata rana Hashim (kakan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* na biyu) ya tasar ma yankin Sham amma sai ya yada zango a birnin Madina.[59] Sai ya sauka gidan wani bawan Allah ana ce ma sa Amru ɗan Labid, wanda ya fito daga shahararren gidan nan na Banu An-Najjar. A gidan ne kuma Allah ya daidaita kan sa da Salma 'yar wannan gidan kuma aka ɗaura ma sa aure da ita. Sun samu wani ɗan lokaci a tare da amaryarsa sannan ya wuce zuwa sana'arsa, inda a can ne ya gamu da ajalinsa a garin Gaza na ƙasar Falasɗinu. Bai sani ba ashe ya bar Salma da cikin ɗa namiji wanda ta sa ma shi suna Shaibatu. Wannan ya faru a shekarar 497M.[60] Daga bisani ɗan uwan Hashim wato Muɗɗalib wanda aka san shi da tsananin ibada da kyawon hali da faɗa da zalunci ya yanke shawarar zuwa Madina domin ya ɗauko ɗan ƙanensa; Shaibatu. A lokacin da suka isa Makka Shaibatu ya yi ƙutut-ƙutut saboda halin tafiya. Don haka da mutane suka tambaye shi ina ka samu wannan yaron? Sai ya ji nauyin ya ce da su "ɗana ne". Don haka sai ya ce mu su "bawana ne". Daga nan aka rinƙa kiran sa "Abdulmuɗɗalib"; bawan Muɗɗalib. Amma asalin sunansa shi ne Shaibatu. Shi ne kuma mahaifin mahaifin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[61]

Abdulmuɗɗalib da ya girma shi ne ya gaji duk ayyukan alheri da baffansa Muɗɗalib yake yi. Don haka sai ya sake tona rijiyar Zamzam bayan har an manta da

---

59 Ana kiran ta Yathrib a wancan lokaci. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* ne ya sa ma ta suna Madina da kuma Ɗaiba.

60 A wata ruwaya an ce ya zo da ita Makka bayan dawowar sa daga birnin Sham in da ta samu ciki, sa'annan ya mayar da ita wurin iyayenta a Madina bisa sharaɗin da ubanta ya gindaya ma sa. Amma ruwayoyi sun haɗu a kan cewa, an haifi Shaibatu bayan cikawar uban nasa, kuma ita ce ta raɗa ma sa wannan suna. Duba: *Fiƙh As-Sirah*, na Gazali, shafi na 64.

61 *Ar Rahiƙ Al-Makhtum,* shafi na 58-59

ita saboda ƙarin sauƙi ga matsalar ruwan sha musamman a lokacin Hajji. Abdulmuɗɗalib dai ba a naɗa shi a matsayin sarkin garin Makka ba, ba kuma shi ne ya fi kowa hali da zarafi a garin ba, amma saboda yawan karimcinsa da hidimomin da yake ma jama'a ya saya wa kansa girma wanda ya sa duk al'amurran garin suka koma a hannunsa. Shi ne wanda yake zartar da kome kuma mutane suna yi ma sa ɗa'a. A lokacin ma da Abrahata ya zo ya yaƙi garin Makka shi ne kaɗai wanda ya tafi ya yi magana da shi. An ba da labarin cewa, a lokacin da ya tona rijiyar Zamzam Kuraishawa sun nemi ya yi tarayya da su a cikin ta, amma ya ƙi yarda. Suka kuwa yi jayayya da shi har wurin wata bokanya don ta yanke ma su hukunci. Amma kafin su kai garin da ita bokanyar take sai wani abin al'ajabi ya faru. Domin kuwa sun gamu da matsanancin ƙishi da ƙarewar guzuri. Ana haka sai suka ga hadari ya kankama, amma da ruwa ya sauka bai sami kowa ba sai Abdulmuɗɗalib. Ganin haka sai suka haƙura suka ce da shi mun yarda Allah ya zaɓe ka. Tirƙashi! Wannan fa shi ne kakan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*

A cikin 'ya'yan Abdulmuɗɗalib, Abu Ɗalib shi ne ya gaji ɗaukar nauyin hidimar alhazai bayan mutuwar Mahaifinsu. Dalilin da ya sa da kuɗi suka gaza ma sa sai ya ranci Dirhami dubu goma daga ɗan uwansa Abbas. Ya kuma kashe kuɗin gaba ɗaya wajen hidimar alhazai. Bayan da ya kasa biyan su ne ya zame ma sa tilas ya amince ya bar wannan matsayi da aiki mai daraja na hidima ga ƙanen nasa Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib.

## 2.4 Watan Bakwai Maƙarar Rani

Shaibatu (wanda aka fi sani da Abdulmuɗɗalib) ya haifi 'ya'ya goma sha shida; Goma maza, shida mata. Ga jerin sunayensu:

1. 'Ya'ya maza
    - Harisu
    - Zubairu
    - Abu Ɗalib

- Abdullahi
- Hamza
- Abu Lahabi
- Gaidaƙu
- Muƙawwamu
- Safari
- Abbas

2. 'Ya'ya mata:

- Ummu Hakim[62]
- Barratu
- Atika
- Safiyya
- Arwa
- Umaima

An ba da labarin cewa, a lokacin da Abdulmuɗɗalib ya tona rijiyar Zamzam ya sha wahala matuƙa. Ba domin ma haƙuri da juriyar da ya yi ba da aikin bai kammala ba. Saboda haka ya yi ma Allah alƙawari cewa, idan ya samu 'ya'ya goma mazaje kuma duk suka girma suka isa taimakon sa zai sadaukar da ɗaya daga cikin su ya yanka shi saboda Allah. Allah kuwa cikin hikimarsa sai ya ba shi abin da ya yi guri na samun 'ya'ya maza goma har da ƙarin 'ya'ya mata guda shida don ya jarraba shi. Da mazajen suka girma sai ya tara su gaba ɗaya ya sanar da su wannan alwashi da ke kansa, suka ce ma sa to, bismillah. Abdulmuɗɗalib ya ɗauke su gaba ɗaya ya je da su wurin da suke ƙuri'a domin a fitar da wanda za a sadaukar da shi a yanka. Kuri'a kuwa sai ta faɗa kan Abdullahi. Don haka ya ɗauki wuƙa ya janyo ɗan nasa zuwa wurin Ka'aba. Abinka da fitaccen mutum mai halin kirki, ganin haka sai duk mutanen Makka suka fito suka ce sam ba su amince ba. Ya za ka dubi ɗan da ya fi kowa biyayya gare ka, ya fi sanyaya ma mutane sannan ka ce za ka yanka shi? Abdulmuɗɗalib ya ce to,

[62] Ana ce ma ta Baidha'u. Ita ce tagwan Abdullahi mahaifin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* kuma kakar Sayyidi Usmanu ɗan Affana; mahaifiyar uwarsa Arwa ‘yar Kuraizu.

ya zan yi da alwashina?! Ala tilas aka nemi fatawa daga wurin wata bokanya (kamar yadda shi ne al'adarsu a zamanin jahiliyya) sai ta ce, a je ayi ƙuri'a a tsakanin Abdullahi da adadin raƙuman da ake bayarwa diyya idan an yi kisan kai bisa kuskure. Idan ƙuri'a ta faɗa a kan raƙuma shikenan sai a yanke su a madadinsa. Abdulmuɗɗalib kuwa ya ba da raƙuma goma cif aka yi ƙuri'a sai ta faɗa kan wannan bawan Allah; Abdullahi. Aka ce a ƙara wasu goma, ta sake faɗawa a kan sa. Ba su gushe ba suna ƙara raƙuma goma goma har sai da suka kammala raƙuma ɗari cif sannan ƙuri'a ta faɗa a kan su. To, ka ji yadda aka yi diyya ta tashi daga raƙumi goma zuwa raƙumi ɗari tun kafin bayyanar Musulunci. Addinin Musulunci kuwa da ya zo sai ya sa hannu a kan haka.

## 2.5 Aure Mafi Albarka

Bayan da Allah cikin ikonsa ya kuɓutar da Abdullahi daga kaifin wuƙa ne sai tauraruwarsa ta fara ɗagawa. Mahaifinsa kuma ya ga ya dace ya nema ma sa aure. Take aka yi matsaya a kan haɗa aurensa da wata mata 'yar babban gida, mai kwarjini, irin wacce ake ce ma "son kowa, ƙin wanda ya rasa". Sunanta Aminatu 'yar Wahabu ɗan Abdumanafi. Ta fuskar dangantaka ta fi shi kusa da gwarzon ƙabila. Domin kakanta na farko Abdumanafi, shi ne kakan mahaifinsa. Bayan da aka yi baikon ta ne da wani ɗan lokaci sai Abdullahi ya kama hanyarsa ta zuwa fatauci; sana'ar da ya gada daga iyayensa. A kan hanyarsa ne kuma ya gamu da ajalinsa a birnin Madina gurin kawunnen mahaifinsa, kuma a can aka yi ma sa jana'iza.

Allah sarkin sarauta! Abdullahi ya tafi amma ya fitar da ajiyar Allah da ke cikin jikinsa wacce aka ƙaddara zata fito da ɗan Adam ma fi daraja da girman matsayi a bayan ƙasa. Abdullahi ya tafi ya bar amaryarsa ɗauke da cikin fiyayyen halitta *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[63]

[63] *Zad Al- Ma'ad,* na Ibn Al- Kayyim 1/17.

## 2.6 Alfijir ya Keto

An haifi fiyayyen halitta Muhammadu ɗan Abdullahi bisa ga mafi rinjayen zaton masana tarihi a ranar litinin wadda ta zo daidai da 8 ga watan Rabi' Al-Awwal, shekara ta 53 kafin hijira, ranar 20 kenan ga watan Afrilun shekarar 571M.[64]

An haife shi ne a wani wuri kusa da Ka'aba, wata biyu kacal bayan faruwar wannan abin al'ajabi da muka faɗi a baya wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya ba da labarinsa a cikin Suratul Fil. A lokacin da Aminatu ta haife shi sai ta ga wani irin haske ya fito daga jikin ta wanda ya haskaka benayen ƙasar Sham. Shakka babu! Haske ne ta haifo ma duniya wanda aka daɗe ana jiran sa.[65]

Maccen da ta karɓi biƙinsa ita ce "Ummu Aiman" kuyangar mahaifinsa. Nonon farko kuma da ya tsotsa daga jikin Suwaiba ne; kuyangar baffansa Abu Lahabi.[66]

[64]A wani ƙauli an ce 2 ko kuma 12 ga watan na Rabi' Al-Awwal ne aka haife shi. To sai dai 2 ga watan Talata ne, 12 kuma Jum'ah. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* kuwa da kansa ya faɗi cewa, a ranar litinin aka haife shi. Ɗaya daga cikin dalilan da suka sa yake azumtar wannan rana ta kowane sati. Duba: *Sahih Muslim* 1162. Haka shi ma ra'ayin da ke cewa, a cikin watan azumi aka haife shi ba ya da ƙarfi sosai. Don haka dai abin da muka faɗa a sama (8 ga Rabi'ul Awwal) shi ne mafi kusa da inganci. Duba: *Al-Mawahib Al-Ladunniyyah*, na Kasɗalani, 1/25 da *Al-Bidayah Wan-Nihaya* na Ibn Kathir, 2/260 da *Al-Mi'yar Al-Mu'rib* na Wansharisi 7/100.
12 ga Rabi' Al-Awwal ita ce ranar da *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya isa Madina tare da rakiyar sayyidi Abubakar. Ita ce kuma ranar da ya cika kamar yadda za mu gani a nan gaba in Allah ya so. Amma ba ita ce ranar haifuwarsa ba. Duba: *Sahih As-Sirah An-Nabawiyyah* na Ibrahim Al-Ali, shafi na 191 da kuma 714.

[65] *Al-Musnad* na Imam Ahmad ɗan Hambali, 5/262 da *Al-Mustadrik* na Imam Al-Hakim, 2/600 da *Majma' Az-Zawa'id* na Haithami, 8/222.

[66] Manzon Allah ya 'yanta ta bayan da ya girma, sannan ya aurar da ita ga masoyinsa Zaidu ɗan Haritha wanda ya yi shahada a yaƙin Mu'utah. Kuma ita ce uwar Usamatu; fitaccen barden nan daga cikin sahabbai. Ta rasu bayan cikawar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* da wata biyar. *Sahih Muslim*, Kitab Al-Jihad, Babu Raddil Muhajirin Ila Al-Ansar, hadisi na 1771.

Babbar alama mai nuna cewa, shi ne Manzon da ya zo ya 'yanta bayi, ya fitar da al'ummar duniya daga ƙangin bauta.[67]

## 2.7 Siffar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*[68]

Ruwayoyi sun bayyana cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kyakkyawan mutum ne, mai kwarjini. Mutum ne kuma mai matsakaicin tsawo, fari, amma ba fari tas ba. Yana da faɗin ƙirji, da kai mai matsakaicin girma, da gashin kai mai tsawo. Haka kuma tafin hannayensa da na ƙafafunsa suna da girma da laushi kamar ka shafa al-hariri. Yana da faɗin goshi da fuska mai walƙiya. Yana da kaurin leɓata da wushirya ga haƙoransa masu haske. Idan ya yi magana har wani haske yake fita daga bakinsa. Idanunsa manya ne, farare tas kamar wata ɗan sha huɗu. Komai a jikinsa bai faifaye ba. Cikinsa a sade yake da ƙirjinsa. Ba zaka ce ma sa kakkaura ba, sannan kuma shi ba siriri ne ba. Mai yawan annashuwa ne da murmushi. Idan ka ba shi hannu ba zai fara janye hannunsa ba har sai ka janye naka. Yakan kalli mutum idan ya haɗu da shi a cikin murmushi da fara'a har sai ka yi tsammanin ba shi da masoyi kamar ka. A kafaɗarsa akwai wani hatimin Annabta da ya tsiro daga naman jikinsa. Yakan kuma sanya zobensa na azurfa a hannunsa na dama.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* mutum ne mai tausayi ga bayin Allah musamman masu rauni. Ba ya rama gayya da fushi. Haƙurinsa ya zarce ƙiyastawa. Domin ba ya fushi sai in an keta dokar ubangijinsa. Ga shi da karimci da baiwa kamar iskan asubahi. Duk wanda ya gan shi zai cika ma sa fuska. Wanda kuwa duk ya zauna da shi zai ce ma ka ban taɓa ganin irin sa ga kyawon hali ko halitta ba.

Yana da saurin tafiya kamar wanda yake gangarowa zuwa kwari daga jigawa. Ba kuma yakan waiwaya idan yana tafiya ba sai dai ya juyo gaba ɗaya. Waiwaye

67 *Ar-Rahmah Al-Muhdah,* na abokinmu Sheikh Dr. Ali Muhammad As-Sheikh, bugun Tarabulus, Lebanon, na farko, 1434H/2013M, shafi na 22.

68 Mun tattara wannan fasali ne daga wurare daban daban a cikin littafin: *As-Shama'il Al-Muhammadiyya* na Imam Abu Isa At-Tirmidhi kuma mun taƙaita matuƙa.

alamun matsorata ne. Jarumawa sun ba da shedar cewa, idan yaƙi ya yi zafi a bayansa maza ke ɓuya.

Kawaicinsa ya fi kalaminsa yawa. Idan ya buɗa baki zai yi magana mai ratsa zuciya da sanyaya gaɓɓai kuma wacce kowa yake iya ganewa. Masoyansa da maƙiyansa duk sun sheda cewa, bai taɓa ƙarya ba ko da a cikin wasa. Tare da haka yakan saki jiki ya yi raha da iyalansa ko da almajiransa, yana ƙanƙan da kansa ta yadda har idan baƙo ya zo yana cikin almajiransa ba zai gane wane ne shi ba sai ya tambaya. Yakan nemi labarin wanda bai gani ba a cikin Sahabbansa, ya kai ziyara wurin maras lafiya, ya halarci jana'izar wanda ya cika, kuma ya wa iyalansa ta'aziyya da kyakkyawar magana wacce take rage ma su raɗaɗi da jin zafin mutuwa. Yakan karɓi kyauta daga mutanen birni da na ƙauye, kuma ya yi godiya a kan ta, sannan ya saka da abin da ya fi ta.

Idan Manzon Allah ya ja mutane sallah ba ya kan tsawaita ba. Amma idan ya tsaya yana sallah a cikin gidansa yakan tsawaita matuƙa, ya dage yana mai ƙanƙan da kansa ga ubangiji har sai iyalansa sun tausaya ma sa.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai damu da abin duniya ba. Kuma ba ya zagi, ba ya la'anta, ba wata kalima yasasshiya da take fita daga tsarkakakken bakinsa. Idan ya ƙyamaci abu sai dai a gani a fuskarsa. Idan ya shiga gidansa abu na farko da yake fara yi shi ne amfani da aswaki don ya goge bakinsa. Saboda cikar tsaftarsa babu kayan da yake sha'awar sa wa kamar farare. A kullum ba shi rabuwa da ƙanshin turare.

Ya Allah! Ka dubi ƙaunarmu ga wannan badaɗayi naka ka yi mana rabon samun cetonsa da kusancin sa ranar alƙiyama.

## 2.8 Renon sa da Shayarwa a Tungar Banu Sa'ad

Makka - kamar yadda muka sani - babbar mahaɗa ce ta al'ummomi daban daban na larabawa a wancan lokaci. Abin da ya sanya mutanen garin suke nisantar da ƙananan yaransu daga garin tun daga haifuwarsu don kada harshensu ya gurɓata da

yaren baƙi masu zuwa ziyara daga sassa daban daban. Don haka sai su bayar da su reno a cikin ƙauyuka in da yaren Kuraishawa na asali ba ya canjawa. Wannan yakan sa yaro ya tashi da miƙaƙƙen harshe da gangariyar larabci wanda babu garwaye a cikin sa. Daga cikin amfanin tashin yara ƙanana a ƙauye kuma akwai nisantar cinkoson jama'a wanda sau da yawa yakan haddasa curutoci da annoba sakamakon gurɓatar yanayi. Samun sarari da iska tatacce da yake a ƙauye kan sanya ƙwaƙwalwar yaro ta zamo mai faɗi, basirarsa ta zamo mai kaifi, jikinsa kuma ya yi ƙwari.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* na cikin waɗanda suka amfana da wannan al'ada kyakkyawa. Domin kuwa Halima 'yar gidan Harisu daga cikin matan Banu Sa'ad ita ce wacce ta karɓi renon sa a daidai wannan lokaci. Ta kuwa tafi da shi can tungarsu ta Bani Sa'ad in da ya zauna wurin ta har zuwa lokacin yaye. An ba da labarin irin albarkoki da alhairai da wannan baiwar Allah ta gani a lokacin zaman sa a tungarsu ta Banu Sa'ad. Abin da ya sa ita da kanta ta fahimci cewa lallai wannan yaro yana da wani sha'ani na musamman. Halima ta faɗi cewa, ba ta da wadataccen nono kafin ta ɗauki Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Haka su ma dabbobin da suke kiwo suna cikin fatara da bushewa; babu ni'ima ko kaɗan ga jikinsu. Ta ci gaba da cewa, tun daga ranar da ta ɗauko shi sai yanayi ya canja. Kirjinta ya cika har nononta yana darara, haka su ma dabbobinta. Yalwantar arziki ta same su sosai har maƙwauta suka ci albarkacinsu. Wannan ya sa jinjirin - *Sallallahu Alaihi wa Sallam* - ya samu daɗin so da ƙauna da kulawa daga wurin su. A dalilin haka, da ta yaye shi sai ta nemi alfarma daga wurin mahaifiyarsa a dan ƙara ba ta lokaci domin ta ci gaba da kula da shi. Fatarta ita ce, ta ci gaba da riƙon sa har girmansa domin ta ci gaba da cin moriyar albarkokinsa kuma ta gane ma idonta abin da Mai-sama yake nufi da wannan nagartaccen taliki. To, sai dai wannan gurin nata ya yanke tun lokacin da wani abin al'ajabi ya faru wanda ya sanya ta jin tsoro kuma ala tilas ta haƙura ta mayar da shi birni in da mahaifiyarsa da danginsa. Daman kuma haka Mai-sama ya tsara. Lokacin zamansa ƙauye ya zo ƙarshe kenan, duk abin da ake so ya koya daga mutanen karkara ya riga ya gama koyon sa.

Abin da ya faru wanda muka yi nuni zuwa gare shi a sama shi ne, a daidai lokacin da Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake ƙarƙashin kulawarta, yana

kimanin ɗan shekaru huɗu, a wata safiya sai ya fita wajen tunga suna kiwon tumaki tare da abokan renonsa. Kawai sai wasu mutane guda biyu suka zo suka kama shi, suka kwantar da shi, suka fito da wuƙa suka fasa ƙirjinsa, suka fito da zuciyarsa. Ganin haka sai abokan kiwonsa suka ruga zuwa wajen iyayen riƙon sa suna cewa, an kashe Muhammad! An kashe Muhammad!!.

Bayan fitowa da zuciyarsa sai ɗaya daga cikin mutanen nan biyu ya fizge wata baƙar tsoka daga cikin ta ya zubar da ita. Ya ce, wannan shi ne rabon Sheɗan a cikin ka. Sa'annan ya ɗauko wata tasa wacce take cike da ƙanƙara ya wanke zuciyar nan tas, ya mayar da ita kamar yadda take, ya ɗunke. Sannan su biyun suka kama hanya suka yi tafiyar su. Ko da mutanen tunga suka rugo domin su ga abin da yake faruwa sai suka haɗu da shi yana dawowa duk fuskarsa ta canja. Anas ɗan Malik *Radhiyallahu Anhu* ya ce, na kasance ina ganin alamun zaren da aka yi ɗinki da shi a ƙirjin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[69] Ka ji dalilin da ya sa Sheɗan tun asali ba ya da rabo a cikin wannan wankakkiyar zuciya ta Manzon Allah. Don haka bai taɓa fushi don an taɓa shi ba sai dai idan an saɓa ma mahaliccinsa. Kuma shi ne ya sa bai taɓa yi ma gumaka sujuda ba, bai kuma shiga cikin duk wasu wasanni da suka danganci jahiliyya ba.

Allah gwanin sarki! Wannan tiyata ta sake faruwa bayan haka a lokuta guda biyu. Na farko shi ne lokacin samun Annabtarsa.[70] Na biyun kuma shi ne lokacin Isra'i da Mi'iraji kamar yadda zamu gani a nan gaba. Kuma labarin wannan tiyata ta uku ya tabbata a mafi ingancin littafan ruwaya; littafan Bukhari da Muslim. A wannan karon Jibrilu *Alaihis Salam* shi kaɗai ya zo ya yi tiyatar kuma ya yi amfani da ruwan Zamzam wajen wanke zuciyar. Sannan bayan da ya ƙare wanke ta karo na uku sai ya kwarara ma sa hikima a cikin ta. Malamai suka ce, amfanin yin tiyata karo na biyu shi ne sanya rahama da tausayi a cikin zuciyarsa bayan an cire ma sa jin haushi da hasadar jama'a waɗanda al'adance akwai su a cikin zukatan mutane. A karo na uku kuma, an ƙara tsarkake zuciyar ne daidai lokacin da zai gana da mahaliccinsa in da zai karɓo

[69] *Sahih Muslim*, Kitab Al-Iman, hadisi na 261.

[70] Imam Al-Bazzar, ya ruwaito haka a cikin *Al-Musnad* nasa, Hadisi na 4048 kuma Al-Hakim ya inganta shi.

wani muhimmin saƙo; shi ne sallah wacce ba a yin ta sai an yi alwala. A alwala kuma ai sau uku ne ake wanke gaɓɓai. Don haka zuciyarsa ta buƙaci wankewa a karo na uku don kai matuƙa wajen tsarkakewa. Kwarara hikima da aka yi a zuciyarsa a wannan lokaci ya sanya shi shi ne mutum na farko da ya iya isar da saƙon Allah zuwa ga mutane cikin hikima da tsanaki, wanda mutum yakan zo ma sa da nufin ya kashe shi saboda ƙiyayya amma cikin gwanintarsa sai ya ɗauki matakin da nan take wannan mutum zai koma cikin masoyansa, kai ma cikin mabiyansa waɗanda ke iya ba da rayuwarsu kai tsaye don kariyar sa. Nan gaba zamu ga misalai da dama kan waɗannan abubuwa cikin yardar Allah.[71]

## 2.9 Maraya Ɗan Gatan Ubangiji

Faruwar wannan abin al'ajabi ya sa Halima ta mayar da yaron zuwa gidan su saboda firgici da ya kama ta a daidai lokacin yana da shekaru huɗu. Riwayoyin ɗan Ishak - sarkin malaman tarihin ma'aiki - a nan sun ɗan yi tufka da warwara. Wai an ce ya shiga shekara ta uku kenan, kuma an ce ya kai shekara biyar. Mun rinjayar da ruwayar ta tsakiya saboda ta fi kusa da inganci. Amma cewar da aka yi a sannan ya fara shiga shekara ta uku bai yi daidai da hankali ba. Domin kuwa ya za ayi ɗan shekara biyu da watanni ya je kiwo?.[72]

Shekaru biyu bayan haka, sai Amina ta ɗauki yaronta domin ta sadar da zumuncin sa da danginsa na Madina; kawunnen mahaifinsa da zuri'arsu. Bayan da suka kammala wannan zumuncin ne a kan hanyar su ta dawowa gida sai Allah ya karɓi baiwarsa a daidai ƙauyen da ake kira Abwa'u mai nisan kilomita 80 daga

[71] Akwai ruwayar wata tiyata a lokacin da *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya kai shekaru goma. To, sai dai duk da yake Imam Ahmad ya ruwaito ta a cikin Musnad (5/139) amma isnadinta bai inganta ba kamar yadda Sheikh Shu'aib Al-Arna'ut ya tabbatar a cikin nazarinsa.

[72] A samu ƙarin bayani a *Ar-Raheeƙ Al-Makhtum,* na Mubarakfuri, shafi na 68 da *Talƙih Fuhum Ahl Al-Athar* na Ibn Al-Jauzee, shafi na 7.

Madina. A can aka yi jana'izar ta. Ita kuma Ummu Aimana ta ɗauko shi ta dawo da shi Makka.[73]

Abdulmuɗɗalib ya ji zafin mutuwar surukarsa; mahaifiyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* matuƙa, kuma ya fito fili ya bayyana haka.[74] Daga nan kuma ya ci gaba da kula da jikansa har yana fifita shi a kan 'ya'yan cikin sa saboda tausayin sa. Shekaru biyu kacal bayan haka shi ma ajalinsa ya cim ma sa sai ya ce ga garinku.[75]

Haka za mu ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tashi a cikin maraici saboda hikimar da ubangiji gwanin sarki ya tanada ma sa ta hanyar yin haka. Tarbiyya da renon ubangiji sun ishi Manzonsa ba sai ya buƙaci wata kulawa daga mahaifa da kakanni ba. Ashe ba haka Annabi Yusuf *Alaihis Salam* ya tashi da farko a gaban mahaifinsa ba - Annabin Allah Ya'ƙub *Alaihis Salam* - a cikin gatanci da ni'ima da kulawa? To, amma me ya faru bayan haka? Sai Maɗaukakin Sarki ya raba shi da shi, ƙaddara ta ingiza shi zuwa in da bai san kowa ba, kuma ba wanda ya san shi, ya je ya fuskanci ƙalubalen rayuwa iri-iri tun daga jefa shi rijiya, zuwa sayar da shi a kasuwar bayi, zuwa fitinar mata da aukawa gidan kaso, sai kuma babbar jarabawa ta samun mulki. Kai, a taƙaice dai ko da mahaifinsa ya gan shi - bayan sama da shekaru ashirin - ya ga Annabin Allah. A ina ya samu wannan baiwa? Kuma wa ya yi tarbiyyar sa a kan ta? Allah ne da kansa ya jiɓinci wannan lamari kuma a kan haka ya kakkaɓe hannun kowa daga gare shi. Babu sauran wani ya yi tunanin cewa, iyayensa ne suka horar da shi a kan wannan da'awa da yake yi. Babban darasin da ke cikin wannan shi ne, kada mu ɗauka cewa, yi ma yaro gata da sagarta shi shi ne abin da zai ɗaukaka shi ko ya sanya shi a matsayi mai girma. Babu shakka idan iyaye suka kula da tarbiyyar ɗansu, suka koya ma sa ilimi da imani, sannan suka haɗa da roƙon Allah to, ana fatar Allah ya shirya ma su shi. Ya Allah ka shirya mana zuri'armu zuwa ga hanya managarciya.

---

[73] *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Hisham 1/68.

[74] *Sahih As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibrahim Al-Ali, shafi na 56.

[75] *As-Sirah An-Nabawiyyah* na Ibn Hisham 1/169.

## 2.10 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a Gidan Baffansa Abu Ɗalib

A lokacin da ajali ya gabato ma Abdulmuɗɗalibi abu na farko da ya fara mayar da hankali gare shi shi ne wasicci ga wanda zai kula ma sa da jikansa. Wanda ya ɗora ma wannan muhimmin aiki kuwa shi ne dansa Abu Ɗalib. To, sai dai a wancan lokaci Abu Ɗalib yana cikin ƙarancin halin rayuwa. Don haka sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya duƙufa wajen neman abin hannunsa don ya taimaka ma baffan nasa. Ya zaɓi sana'ar kiwon tumaki waɗanda yakan karɓi jinga a kan kiwon su. Wannan ba abin mamaki ba ne domin 'yan uwansa Annabawan Allah duk sun yi kiwo kamar yadda shi da kansa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya faɗa.[76] Kuma Alƙur'ani ya labarta ma na cewa, Annabinsa Musa *Alaihis Salam* ya yi jingar kiwo da surukinsa.[77] Wasu daga cikin su kuma sun yi ƙarin wasu sana'oi daban daban. Alal misali, Annabi Nuhu *Alaihis Salam* ya yi aikin kafinta. Annabi Idris *Alaihis Salam* ya yi saƙar hannu. Annabi Dawud *Alaihis Salam* ya yi sana'ar ƙira. Ashe babu abin mamaki idan muka ga Annabinmu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi kiwon tumaki a lokacin ƙuruciyarsa yana karɓar jinga daga mutanen Makka.[78] Malamai sun zayyana irin ɗabi'un kirki da makiyaya ke samu, musamman kiwon tumaki. Waɗannan ɗabi'u sun haɗa da:

1. Haƙuri
2. Natsuwa
3. Kanƙan da kai
4. Jarunta
5. Tausayi
6. Koƙarin neman abinci. Da sauran su

[76] *Sahih Al-Bukhari* 2262.
[77] Suratul Kasas 25-29.
[78] *Sahih Al-Bukhari*, Kitabul Ijara, Bab Ra'yil Ganam Ala Kararit, hadisi na 2262.

Babu shakka duk wanda ya saba da kiwon tumaki - dabbobin da suka fi ko waɗanne rashin natsuwa da bin oda - ba zai gaza ba wajen kiwon 'yan Adam duk yadda rashin hankalinsu ya kasance. Wani darasi da ya kamata mu koya a nan shi ne, neman abinci shi ne rayuwar Annabawa, ba zama ci-ma-kwance ba. Don haka Musulunci yana ƙarfafa mu mu tashi tsaye domin samun na kanmu. Yin bara da maula da roƙo da banbaɗanci duka ɗabi'u ne na ƙasa da ba su dace da musulmi nagartacce ba.

## 2.11 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a Lokacin Samartaka

Saurayi, a ilimin sanin halayyar ɗan Adam, mutum ne mai wuyar sha'ani. Yana da gaggawa cikin al'amari, da ji-ji-da-kai da son jin daɗi. Ba kasafai kake samun saurayi ba sai ka gan shi da wasu fizge-fizge waɗanda dattawa ke kallo a matsayin kauce ma hanya. Shi kam Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba haka samartakarsa ta kasance ba. Ya yi rayuwa tsaftatacciya abin burgewa wadda ba abin da dattijai zasu ce ma sa sai mashaallahu! Bari mu ɗan kawo wasu abubuwa da suke nuna mana halayyarsa a irin wannan lokaci.

### 2.11.1 Fatauci:

A daidai lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya cika shekaru goma sha biyu ya fita sau ɗaya a tare da baffansa Abu Ɗalib zuwa fatauci a ƙasar Sham. A cikin ayarin da suka tafi kuwa akwai dattawa daga cikin manyan Kuraishawa. An ba da labarin cewa, sun hadu da wani malami daga cikin malaman Nasara mai suna Jarjis, ana kuma kiran sa Bahira wanda ya lura da dukkan alamomin Annabta daga fuskar jikan Abdulmuɗɗalibi, kuma a kan haka ya girmama su, sannan ya hane su da tafiya da shi cikin yankin Rumawa. Ya ce, idan Rumawa suka ƙyalla idon su a kan Manzon Allah za su gane shi kuma za su ƙulla ma sa sharri ko su haɗa

shi da wata cuta.[79] Sai dai akwai jayayya mai ƙarfi a tsakanin masana dangane da ingancin faruwar wannan lamari. Sanin gaibu sai Allah.

### 2.11.2 Yaƙin Rashin Dattaku *"Harbul Fijar"*

Kamar yadda muka faɗi a can baya kafin bayyanar Musulunci an yi yaƙoƙa masu yawa a tsakanin ƙabilun larabawa. Daga cikin fitattun yaƙoƙan su kuwa akwai jerin yaƙoƙa da ake kira "Harbul Fijar" yaƙin fajirci saboda sun saɓa ma ƙa'ida don an yi su a cikin gari mai alfarma. Wannan yaƙi ya kai ƙololuwa ne a lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ke da shekaru goma sha huɗu (14). Yaƙin kuma ya gudana ne a tsakanin ƙabilarsa ta Kuraish tare da haɗin guiwar ƙabilar Kinanata da kuma ƙabilar Hawazin wacce ta kawo ma su takakka har a cikin birnin Makka. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shedi wannan karafkiya a tare da baffanninsa, kuma bai tsaya a matsayin ɗan kallo ba wajen kare alfarmar gari mai albarka duk da yake a lokacin yana matashi ba za a sa shi a cikin sojoji ba. Duk da haka ya ba da tasa gudunmawa domin kuwa shi ya rinƙa kwashe kibau da abokan gaba ke jefowa yana tsara su waje ɗaya ya mayar da su ga 'yan uwansa domin su kuma su yi amfani da su wajen mayar da martani. Babu shakka wannan yana nuna irin jaruntaka da sadaukantakar da ya kasance a kan ta a daidai wannan lokaci.[80]

### 2.11.3 Kungiyar Tabbatar da Adalci da Kariyar Marasa Galihu

Bayan gama wancan yaƙin da muka faɗa ne aka kafa wata ƙungiya a garin Makka domin agaza ma waɗanda suke marasa galihu ne daga cikin mazauna garin Makka da kuma baki masu kawo ziyarar kasuwanci ko ta ibada. Dalilin kafa wannan ƙungiya ya samo asali ne daga wani zalunci da Asi ɗan Wa'il ya yi ma wani baƙo da ya zo da hajarsa daga ƙasar Yemen. Asi ya sayi kayansa ya ƙi biyan sa, ya kuma yi ma sa barazanar cewa, ya je ya kai ƙara duk inda yake ganin za a iya ƙwatar ma sa haƙƙensa. Jin haka da wannan baƙo ya yi sai ya fashe da kuka, ya koma daidai Ka'aba yana kururuwa yana neman mai agaza ma sa. A nan ne baffan Manzon Allah

[79] *Al-Jami'u* na Tirmidhi, hadisi na 3620 da *Sahih As-Sirah An- Nabawiyyah* na Ibrahim Al Ali, shafi na 58-59.

[80] *As- Sirah Al- Halabiyyah*, na Ali Al- Halabi, 1/127-129.

*Sallallahu Alaihi wa Sallam* Zubairu ɗan Abdulmuɗɗalib ya tashi yana neman a haɗa kai don a taimaka ma sa. Mutanen arziki daga gidaje daban daban suka amsa kiran sa, sai suka haɗu a gidan Abdullahi ɗan Jud'an in da suka sa hannu a wata yarjejeniya cewa, daga yau duk wanda aka zalunta za su taimake shi su ƙwato ma sa haƙƙensa. Ba a wayi gari ba sai da suka je da ƙarfin tsiya suka matsi Asi ɗan Wa'il suka amsar ma wannan baƙo haƙƙensa. Daga nan ne kuma suka shiga sa ido ga al'amurran manyan gari domin su tabbata sun hana su yin zalunci. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya faɗi wannan kwamiti da aka yi tare da shi a lokacin yana saurayi. Ya ce bai taɓa nadamar an yi wannan aiki da shi ba, kuma da za a sake kafa irin wannan kwamiti a Musulunci zai zama memba a cikin sa.[81]

Da wannan ne malamai suka fahimci cewa, aikin alheri a ko ina ake yin sa alheri ne. Kuma ya halalta a haɗa kai da ko wane irin mutum a kan manufar da ke kawo ci gaba in dai ba ta ci karo da Shari'ar Musulunci ba. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* yana cewa:

> *".. Kuma ku taimaki juna a kan ayyukan ɗa'a da tsoron Allah, kuma kada ku taimaki juna a kan ayyukan zunubi da ta'adi" Suratul Ma'ida: 2.*

Haka kuma muna iya fahimta daga labarin kafa wannan kwamiti cewa, duk yadda aka lalace ba za a rasa mutanen kirki ba a koda yaushe, masu mutunci kuma masu neman gyara. Tun kafin ya karɓi saƙon manzanci, Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai ware kansa daga jama'a ba, a'a, yana tare da su ga ayyukan alheri masu alfanu da kawo ci gaba.[82]

### 2.11.4 Ginin Ka'aba

Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* shi ne kakan Annabawa kuma wanda ya bi gumaka duk ya rugurguza su.[83] Haka kuma shi ne wanda Allah ya ɗaukaka shi da

---

[81] *As-Sunan* na Baihaki 3/367 da kuma *Fiƙh As-Sirah* na Ghazali, shafi na 72.
[82] *As- Sira An-Nabawiyyah* na Sallabi, shafi na 59-61.
[83] Suratul Anbiya': 48.

ginin ɗakin Allah na farko a bisa doron ƙasa. Allah Ta'ala ya umurce shi da yin ginin wanda ɗansa Isma'il - kakan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* - ya taimaka ma sa a kai.[84]

Tsawon ginin Ka'aba a wancan lokaci kamu tara ne. Faɗinta kuma kamu talatin. A ɗaya gefen kuma kamu ashirin da biyu. Sannan babu rufi a saman ta. Yau da gobe ta sa wannan ginin ya samu matsala musamman bayan wata ambaliyar ruwa da aka yi wacce ta kusa haɗiye ɗakin, amma saboda kwarjinin da ɗakin yake da shi aka rasa wanda zai iya buge bangayensa don a sabunta shi. Daga bisani Kuraishawa suka yanke shawarar sake wannan aiki a lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana da shekaru talatin da biyar (35) suka kuma sa sharaɗi cewa duk wanda zai ba da gudunmawa ya tabbatar ya zo da halas. Kada wanda ya kawo kuɗin sata ko kuɗi da ruwa ko na zalunci ko kuɗin karuwa. Wannan ne ya sa suka rasa wadatar kayan aiki, abin da ya janyo dole suka rage faɗin Ka'aba a ƙasa da kamu shida da rabi bayan sun ƙara ma ta tsawo ninki biyu ta koma kamu goma sha takwas daga kamu tara da take a farko. Kuma a da tana da ƙofofi biyu a ƙasa masu fuskantar juna, sai suka rufe ƙofa ɗaya, ita kuma ɗayar suka ɗaga ta ta yadda ba za a iya shiga ɗakin ba sai da tsani don kauce ma ambaliyar ruwa da kuma wata manufa ta siyasa ita ce, kada wanda ya shiga a cikin ɗakin sai da izininsu. Suka kuma yi ma ɗakin Allah rufi bayan a da a sake yake; ruwan sama na kwarara kai tsaye a cikin sa.

Kuraishawa dai sun raba aikin kashi kashi. Kowa ce ƙabila aka ware ma ta inda ake son ta gina. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ruwa da tsaki a cikin wannan aiki na alheri tare da baffanninsa da sauran danginsa. Ya riƙa ɗauko duwatsu a bisa kansa tare da baffansa - kuma tsaransa - Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib suna kawo wa don taimaka ma magina. Wannan ya ƙara tabbatar da abin da muka faɗi a baya cewa, ayyukan alheri ko da wa ana haɗa kai ayi su. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai rayu daban da mutanensa ba ko a lokacin jahiliyyarsu. Kawai dai ya ƙaurace ma su ne ga abubuwan da suke yi na ma'asi da Shirka. A cikin wannan aikin na ginin Ka'aba ne Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana ma Kuraishawa darajar

[84] Suratul Baƙarah: 127-129.

Manzonsa, alama a kan cewa, lokaci ya yi kusa da wannan taliki zai zo ma su da hanyar warware matsala da duk wani rikici a tsakanin su. Ba da daɗewa ba zai zo ma su da hanya miƙaƙƙiya wadda za ta sa su zauna lafiya, kuma su ci ni'imar duniya da ta lahira idan sun yi ma sa ɗa'a. Abin da ya faru a wannan lokaci shi ne, a lokacin da gini ya iso daidai Hajarul Aswad, baƙin dutsen da Allah ya sauko ma Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* shi daga aljanna[85] sai Kuraishawa suka yi saɓani a kan wanda zai ɗora shi a wurinsa. Kowa ce ƙabila tana ganin za a yi ma ta gori idan ba ita ce ta samu falalar sanya shi ba. Rikici kuwa ya harɗe, abu kaɗan ya rage ya koma yaƙi. Daman da irin haka ne yaƙi yake somawa a cikin su. Ana haka ne, sai Allah ya jefo ma wani dattijo a cikin su tunani cewa, mu sanya alƙali da zai yi hukunci a cikin wannan sha'ani. Kuma idan ya yi hukunci duk mu amince da abin da ya zartar. To, wane ne za a sanya wanda ba zai yi son zuciya ya gabatar da ƙabilarsa ba? Kawai sai suka amince a bar wannan hukuncin ga duk wanda Allah ya jefo shi ya fara shigowa a wannan masallaci. Rufe bakinsu ke da wuya sai ga Muhammad (tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi) ya kunno kai bai san abin da ake ciki ba. Sai ya ji gaba ɗaya an ɗauki shewa da tafi ana cewa, mun amince, mun amince! Ga amintacce!! Da suka yi ma sa bayanin matsalarsu sai Allah ya jefo ma sa hikima, ya sauke mayafinsa ya shimfiɗa shi, ya sa hannayensa masu tsarki ya ɗauko dutsen ya ɗora a mayafin nasa. Sannan sai ya ce ma su, kowa ce ƙabila ta ba ni wakili guda ɗaya. Sai ya umurci wakilan nan da su kama sassan mayafin nan su cira shi daidai wurin da za a ɗora dutsen sannan ya sake sa hannunsa ya ɗauko *Hajarul Aswad* ya ɗora shi a wurinsa.

Allahu akbar! Ashe tuntuni ga wanda ya san makamar zaman lafiya da adalci a cikin su amma ba su sani ba. Da wannan sai ya samu darajoji guda biyu; ga matsayin warware rikici da kwantar da tarzoma, ga kuma darajar ɗora dutsen a wurinsa wadda rigima a kan ta ce ta so ta haifar da yaƙi. Da wannan ya samu ƙarin kwarjini da muhibba a cikin jama'a shekaru biyar kafin Annabtarsa.

---

[85] Allah ya saukar da wannan dutsen fari tas. Zunuban 'yan Adam ne suka dushe haskensa. *Al-Jami'* na Imam at-Tirmidhi, hadisi na 877, kuma Tirmidhi da Albani sun inganta shi

## 2.12 Aure da Gina Iyali

A daidai lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kai shekaru ashirin da biyar ya yi fice a wajen sadaukantaka da halin girma. Ba wani gida daga cikin gidajen Kuraish face suna farin cikin in da zai nemi aure a gidansu. Ba kuma wata mace daga cikin su ƙarama ce ko babba da ba zata yi murna ba idan aka ce Muhammad ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake neman auren ta. A daidai wannan lokacin ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya nemi aure. To, amma abin sha'awa shi ne bai nemi auren ƙaramar yarinya ba. Wacce ya nema bazawara ce 'yar babban gida, sunanta Khadijatu 'yar gidan Khuwailid. Ta yi aure kafin haka har sau biyu kuma tana da 'ya'ya.[86]

A game da dalilin aurensu, da yawan marubuta sun kawo labarin cewa, kasuwanci ne ya fara haɗa su in da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya je birnin Sham tare da bawanta Maisara suka yi fatauci da dukiyarta. Aka ce bayan da ta ga albarkokin wannan bawan Allah ne, da kanta sai ta nemi ƙulla zumuntar aure da shi kuma ta aiki ƙawarta Nafisatu 'yar Munabbihu wadda ta shirya ma sa maganar kuma ya amince da ita.[87]

Babu wani Saɓani cewa, shekarun Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a lokacin aurensu 25 ne. Amma game da shekarun amaryar tasa ruwayoyi sun yi Saɓani. A lokacin da fitaccen malamin nan Waƙidi yake ganin ta kai shekaru 40, shi kuma malam ɗan Ishaƙa na ganin shekarunta 28 ne. Wannan zancen nasa kuwa babu shakka ya fi ƙarfi. Domin ko bayan kasancewar malamai na da shakku wajen karɓar ruwayar Waƙidi, maganar ɗan Ishaƙa ta fi kusa da hankali. Saboda mawuyacin abu ne - a al'adance - maccen da ta kai shekaru 40 ta haifi 'ya'ya har guda 6 bayan haka.

---

[86] *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Sallabi, shafi na 59-61.

[87] Asalin wannan ruwaya ta fito ne daga littafin shaihun malamin nan ɗan Ishaƙa amma fa ba ta da isnadi (madogarar da za ayi hukunci da ita a kan ingancinta ko rashin sa). Don haka malaman ruwaya ba su ƙarfafa ta ba. Shi kam zancen auren tabbatacce ne har a mafi ingancin littafan ruwaya na Bukhari da Muslim.

Musamman in muka yi la'akari da cewa ta haifi ɗanta na ƙarshe; Abdullahi ne bayan bayyanar Musulunci, shekaru sama da 15 kenan bayan wannan aure.[88] A bisa wannan ingantacciyar riwayar Nana Khadija ta girme shi ne da shekaru 3 kacal. Kuma duk 'ya'yan da Allah ya ba shi ita ce ta haife su in ban da Ibrahim wanda kuyangarsa Mariya 'yar asalin ƙasar Masar ta haifa. A cikin ikon Allah kuwa 'ya'yan nasa gaba ɗaya sun riga shi komawa ga Allah in ban da 'yar autar 'ya'ya matansa; ita ce Sayyida Fatima. Ita kam ta rayu ɗan lokaci kaɗan da bai shige wata shida ba a bayansa.[89]

Nana Khadija mace ce mai haƙuri da kaifin hankali da sanin ya kamata. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da kansa ya kan nemi shawararta a wasu al'amurra nasa. Kuma babu shakka cewa, ya ji daɗin zama da ita fiye da yadda za a misalta. Bayan so da ƙauna da ke tsakanin su, Nana Khadija ta taimaki maigidanta matuƙa a lokacin da bai da wata madafa in ba tata ba. Shi ya sa ma bai taɓa tunanin ƙara aure ba duk tsawon rayuwarta. Sun yi shekaru 21 tare da ita sannan Allah ya karɓi ranta. Kuma yakan fadi alherinta ko bayan mutuwar ta har a gaban iyalansa. Abin da Nana A'isha ta ce ya kan motsa kishi a zuciyarta amma ba yadda za ta yi domin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* mutum ne da ba ya manta alheri ko ƙanƙane ne aka yi ma sa ballantana kuma alherin babbar masoyiyarsa uwar 'ya'yansa.[90]

Babu shakka wannan uwa ta mummunai ta karantar da mu abubuwa da dama. Kuma a dalilin aurenta al'ummar musulmi sun karanci darussa da hukunce hukunce masu amfani. Da farko dai mun gano cewa, halas ne ga namiji ya auri matar da ta girme shi, ita ma halas ne ta auri wanda bai kai shekarunta ba. Sannan halas ne mace ta nuna kanta ga mutumin kirki don neman ya aure ta. Kuma ya halasta namiji ya tare da matarsa a gidanta idan shi bai mallaki gida ba. Mun kuma fahimci cewa, auren mace mawadaciya ga namiji talaka ba laifi ba ne kuma ba aibi ba, matuƙar akwai so da ƙauna da mutuntawa. Idan ma har ta taimaka bisa raɗin kanta ta ɗauke ma sa wasu

[88] *Uyun Al-Athar* na Ibnu Sayyid An-Nas 2/363.
[89] Duba: *Rasulullahi fi Makka,* shafi na 79.

[90] *Sahih Muslim*, Kitab Fadha'il As-Sahaba, hadisi na 2437.

nauye-nauyen gida da kuɗinta kuma a haka ta kyautata ba ta yi laifi ba. Mace kuma - bisa ga darasin da Nana Khadija ta koya ma al'umma - ita ce babban jigon ɗa namiji managarci. Shi ya sa masu hikima ke cewa, duk in da ka ga namiji ya gawurta akwai nagartacciyar mace a bayansa.[91]

Nana Khadija dai ba wani mahaluki da Manzon Allah ya amfana da shi a farkon rayuwarsa ta addini kamar ta. Kamar yadda daga bisani babu wata mata da ta zame ma sa sanyin ido kamar Nana Aisha. Shi ya sa da aka tambayi shehin Musulunci ɗan Taimiyya game da matsayinsu sai ya sa hikima. Ya ce, a farkon Musulunci Khadija ita ce mafificiyar macce wacce ta taimaki Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ta hanyar ƙarfafa shi da taimakon da'awarsa. A ƙarshen Musulunci kuma Nana A'isha ita ce mafificiya wacce ta kiyaye ma musulmi ɗaukacin rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da irin basirar da Allah ya ba ta. Har ya kasance ba wani hukunci da ya danganci rayuwarsa face an samo wani ilmi mai albarka dangane da shi a wurin ta. Babban darasi ga malamai magadan Annabawa a cikin wannan lamari shi ne su riƙa yin taka-tsantsan wajen neman aure. A maimakon kyau da ƙuruciya su nemi asuli da tarbiyya da nagarta.

A cikin mutuwar 'ya'yan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* tun a rayuwarsa akwai darasi babba. Manzon Allah ya ɗanɗani zafin mutuwarsu kamar yadda ya ɗanɗani zafin mutuwar iyayensa tun da wuri. Haka ita ma uwargidan tasa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɗanɗani zafin mutuwar ta wacce ta zo daidai da mutuwar baffansa mai kyautata kula da shi da ba shi kariya daga maƙiya. Kada ka taɓa tsammanin idan kana masoyin Allah ba za ka gamu da matsalolin rayuwa ba. Ai duniya ba komai ba ce a wurin Allah. Kuma jarabawoyin rayuwa sukan ƙara ma mumini kaifin hankali da sabawa da haƙuri da tausaya ma jama'a kamar yadda jin daɗin duniya idan ya yi yawa yake sa daƙilewar basira da ƙarancin haƙuri da raina mutane. Ga kuma ɗinbin ladar da Allah ya yi tanadi ga wanda ya yi haƙuri da ɗacin rayuwa ya mayar da al'amari ga Allah. Wani muhimmin darasi kuma a nan shi ne, lura da cewa, addinin Musulunci ba kayan gado ba ne. Domin kuwa da haka ne

91 *Ar-Rahmah Al-Muhdah*, na Sheikh Dr. Ali Muhammad As-Sheikh, shafi na 98.

abu ne mai sauƙi ga Maɗaukakin Sarki ya raya ma Manzo 'ya'yansa maza domin su gaje shi. Allah dai ya yi ma sa ni'imar haifuwa; bai zamo bakarariya ba. Ya jiyar da shi daɗin haifuwa na wani lokaci sannan ya karɓi abinsa. A cikin wannan akwai sanyayawa ga wanda aka ba shi aka amshe, ko kuma wanda ba a ba shi ba ma sam. Sai su yi koyi da ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a cikin haƙurinsa da juriya.

### 2.13 Sanin Matsayin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*

A cikin wannan fasali za mu ɗan tsakuro wasu daga cikin darajojin da ubangijinmu maɗaukaki ya ba Manzonsa a cikin Alƙur'ani:

1. Manzon Allah fitila ne kamar yadda Allah ya kira shi da kansa a Suratul Ahzab da Suratul Ma'ida.[92]
2. Kuma kafin Allah ya aiko shi sai da ya wanke masa ƙirjinsa, ya ɗauke ma sa jin nauyin wahalar kira zuwa ga addini, sannan ya ɗaukaka ambatonsa.[93]
3. Allah da kansa ne ya fara yi ma sa salati, sannan sai Mala'ikunsa. Bayan haka ne ya ce mu ma mu sa baki a cikin wannan aiki mai albarka.[94]
4. Babu wani mahaluki da Allah ya rantse da rayuwarsa in ba Manzon Allah ba, kamar yadda ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhu* ya faɗa.[95]
5. Ban da wannan kuma Allah ya yi ta rantsuwa a kan al'amarinsa. Misali, a Suratul Kalam Allah ya rantse cewa Annabinsa ba mahaukaci ba ne.[96] A Suratud Dhuha kuma ya rantse cewa bai fita batunsa ba kamar yadda wasu suka zata saboda jinkirin wahayi da aka samu.[97] A Suratun Najm Allah ya rantse don kare Annabinsa daga kasancewa a kan ɓata ko furuci da son zuciya kamar yadda mushrikai suke rayawa.[98] A Suratu Yasin Allah ya

[92] Duba Suratul Ahzab: 45-46 da Suratul Ma'ida: 14-16
[93] Suratus Sharh: 1-4
[94] Suratul Ahzab: 56
[95] Suratul Hijr: 72
[96] Suratu Nun: 1-5
[97] Suratud Dhuha: 1-3.
[98] Suratun najm: 1-5.

rantse da Alƙur'ani cewa Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cikin manzanni.[99] Duk bayan wannan kuma sai da Allah ya rantse har da garinsa.[100]

6. Kai, ba wata addu'a fa da Manzo ya ɗaga hannunsa ya yi zuwa ga Allah sai ka ga ya yi gaggawar karɓa ma sa. Wani lokacin ma idan ya yi fata tun bai roƙa ba Allah yake ba shi. Kamar yadda ya faru ga labarin sauya Alƙibla, in da Maɗaukakin Sarki ya ce:

((قد نرى تقلب وجهك في السماء فلنولينك قبلة ترضاها، فول وجهك شطر المسجد الحرام..)) سورة البقرة: ١٤٤

*"Haƙiƙa muna ganin jujjuyawar fuskarka zuwa sama. To, za mu juyar da kai zuwa ga Alƙiblar da kake so. To, ka juyar da fuskarka zuwa masallaci mai alfarma..".*[101]

## 2.14 Wane Annabi ne ya fi?

Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana mana darajar Annabawa a matsayin su na fiyayyu kuma zaɓaɓɓu a cikin bayinsa. Sa'annan kuma ya bayyana mana fifikon manzanni a kan Annabawa waɗanda adadinsu yana da yawan gaske kuma Allah ne kaɗai ya san yawan nasu.[102] Sai kuma fifikon Ulul Azmi guda 5 a kan sauran Manzanni. Su ne: Nuhu da Ibrahim da Musa da Isa da cikamakinsu Muhammad amincin Allah ya ƙara tabbata a gare su gaba ɗaya. Babu shakka cewa, Manzon Allah na ƙarshe Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana da ƙarin matsayi da fifiko da yawan daraja da falala a kan su su duka. Wannan kuwa abu ne da ya fi ƙarfin a buƙaci kafa masa dalili. Amma dai za mu ba da 'yan misalai gwargwadon yadda wanda bai sani ba zai sani, wanda kuwa ya sani zai ƙara tabbatarwa:

---

99 Suratu Ya Sin: 1-3

100 Suratul Balad: 1-2

101 *Suratul Baƙarah: 144.*

102 *Majmu' Fatawa Ibn Baz* 2/66-67.

2. Duk lokacin da Allah zai yi maganar Annabawa da sunansa yake farawa. Wannan shi ne abin da sarkin musulmi Umar ɗan Haɗɗabi *Radhiyallahu Anhu* ya faɗi a lokacin wafatin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* in da ya gurfana a makwancinsa ya ce, kaicona! Na fanshe ka da uwata da ubana ya Manzon Allah. Kai ne wanda matsayinsa ya kai cewa, ka zo a ƙarshe amma a kullum idan Allah zai fadi 'yan uwanka Annabawa da kai yake farawa.[103]

3. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya bayyana cewa, duk Annabawa sai da Allah ya sanya su suka sa hannu ga wani alƙawari; shi ne gaskata Annabi Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da taimakon sa idan ya riske su. Kuma sannan Allah da kansa ya rubuta shedarsa a kan wannan alƙawari da ya yi da su. Duba Suratu Ali Imran: 81 in da Allah ya ce:

((وإذ أخذ الله ميثاق النبيين لما آتيتكم من كتاب وحكمة ثم جاءكم رسول مصدق لما معكم لتؤمنن به ولتنصرنه، قال أأقررتم وأخذتم على ذلكم إصري؟ قالوا أقررنا، قال فاشهدوا وأنا معكم من الشاهدين)) سورة آل عمرن: ٨١

4. A cikin Alƙur'ani ba wani Annabin da Allah ya shaya faɗin sunansa in ba shi ba. Duk Allah ya kira su ɓaro ɓaro. Kamar yadda ya ce:

((قيل يا نوح اهبط بسلام منا..))

*"Sai aka ce ya kai Nuhu.."*.[104]

((وناديناه أن يا إبراهيم))

*"Muka kira shi ya Ibrahim!.."* .[105]

---

[103] Yana nuni da wurare kamar in da buwayayyen sarki yake cewa:

((وإذ أخذنا من النبيين ميثاقهم، ومنك ومن نوح وإبراهيم وموسى وعيسى ابن مريم)) الأحزاب: ٧

A wannan ayar duk *Ulul Azmi* ne; mafifitan annabawa aka kawo. Amma sai da Allah ya fara da shi tukuna.

[104] Suratu Hud: 48

((يا موسى إنه أنا الله العزيز الحكيم))

*"Ya Musa! Haƙiƙa fa Ni ne Allah buwayayye,mai cikakkiyar gwaninta"* .[106]

((يا عيسى بن مريم اذكر نعمتي عليك..))

*"Ya kai Isa dan Maryam ka tuna ni'imomina a kan ka.."* .[107]

((يا داود إنا جعلناك خليفة في الأرض))

*"Ya Dawud! Haƙiƙa mun sanya ka halifa a bayan ƙasa.."*.[108]

Duk da haka a wurare 15 Allah ya yi kiran sa amma ba in da ya kira shi da sunan yanka kamar yadda ya kira su. Sai dai ya ce masa (يا أيها النبي) ko kuma ( يا أيها الرسول). Kai, ko a wuraren da sunansa ya zo a tare da na kakansa uban Annabawa Ibrahim *Alaihis Salam*, Allah ya faɗi sunan kakan, amma sai ya saya nashi suna. Duba Suratu Ali Imran: 68 da Suratul Ahzab: 7

((إن أولى الناس بإبراهيم للذين اتبعوه وهذا النبي..)) آل عمران: ٦٨

**Ma'ana:**

> *"Haƙiƙa mutanen da suka fi cancantar Ibrahim su ne waɗanda suka bi shi da kuma WANNAN Annabi da waɗanda suka yi imani"*.[109]

((وإذ أخذنا من النبيين ميثاقهم، ومنك ومن نوح وإبراهيم وموسى وعيسى ابن مريم)) الأحزاب: ٧

**Ma'ana:**

> *"Ka tuna lokacin da muka riki alƙawari daga Annabawa, da kuma wurin ka da wurin Nuhu da Ibrahim da Musa da Isa dan Maryam.."*.[110]

---

105 Suratus Saffat: 104
106 Suratun Namli: 9
107 Suratul Ma'ida: 110
108 Suratu Sad: 26
109 Suratu Ali Imran: 68.
110 Suratul Ahzab: 7.

3 Allah ya aiko Annabawa zuwa ga jama'arsu ne kawai. Nuhu zuwa ga mutanensa, Hudu zuwa ga Adawa; mutanensa, Salihu zuwa ga danginsa Samudawa, Shu'aibu zuwa ga mutanen garinsu Madyana, Annabi Luɗu ma haka zuwa ga alƙaryun jama'arsa na Sadum. Duk a cikin manzanni ba wanda aka aiko shi ga duniya gaba ɗaya sai Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Allah Ta'ala ya ce: *"Ka ce, ya ku mutane! Haƙiƙa ni, Manzon Allah ne zuwa gare ku gaba ɗaya".*[111]

4 Kuma an aiko shi ne don ya zama rahama ga kowa da kowa, na farko da na ƙarshe. Talikai duka ba yan Adam kawai ba. Kamar yadda buwayayyen sarkin ya ce: *"Ba mu aiko ka ba face sai don rahama ga talikai".*[112]

5 Ko a lahira Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana da ƙarin matsayi a kan sauran 'yan uwansa manzanni da Annabawa. Domin kuwa shi ne wanda ƙabari zai fara tsagewa ya fito, kuma shi ne za a fara bude ma kofar aljanna. Duk Annabawa an ba su damar yin addu'a guda ɗaya da za a karɓa ma su, amma shi sai ya ajiye tasa sai ranar alƙiyama. Don haka shi kaɗai ne zai yi babban ceto (don neman Allah ya yi wa bayi hisabi), shi ke da tafkin Alkauthar, shi ne mai *Liwa'ul Hamd* tutar da duk Annabawa zasu shiga a cikin ta. Ga shi kuma duk ya fi su yawan mabiya a ranar alƙiyama. Sannan zai wanke al'ummarsa ya yi ma ta sheda gaban Allah, cewa al'ummar kirki ce, don ita kuma ta yi ma sauran Annabawa sheda cewa, sun isar da manzanci. Sai Allah ya karɓi shedun al'ummarsa ya yi hukunci a tsakanin Annabawa da waɗanda suka karyata su daga cikin mutanen su.[113]

Waɗannan dalilai da ire-iren su masu tarin yawa sun tabbatar cewa, Manzon Allah Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cikamakin Annabawa shi ne limaminsu kuma shugabansu, sa'annan mafifici a cikinsu. Kuma ma dai

[111] *Suratul A'raf: 158*
[112] *Suratul Anbiya': 107*
[113] Suratul Bakara: 143.

da bakinsa mafi tsarki da albarka ya faɗa cewa "Ni ne shugaban mutane a ranar alƙiyama".[114]

Ya Allah muna godiya da ka sanya mu cikin al'ummarsa. Ya Allah ka sanya mu a cikin cetonsa. Maganar darajojinsa tana da saura. Bari mu ƙara gyara zama. Bismillahi:

## 2.15 Mu'ujizojinsa[115]

Ma'anar Mu'ujiza ita ce yin duk wani abin da yake a al'adance ɗan Adam bai iya yin sa don nuna Annabta.

Mu'ujizojin Annabawa na da yawa, ko wanne Allah yakan ba shi tasa daidai yanayi da zamani da mutanensa don sawwaƙe ma su fahimtar cewa, shi jekada ne daga wurin Allah. Misali, Annabi Musa *Alaihis Salam* ya yi amfani da sandarsa wacce ta koma macijiya da izinin Allah, ta haɗiye macizan da bokaye suka ruɗi mutane da su, sai nan take suka gane shi ba boka ne irin su ba, aikakken Manzo ne daga Maisama. Haka kuma ita wannan sandar ita ce wadda ya yi amfani da ita da izinin Allah ya tsaga teku ya fita tare da jama'arsa suka kuɓuta daga sharrin ayarin Fir'auna, a yayin da jama'ar Fir'auna suka nutse, Allah ya halakar da su a tekun Maliya bayan wucewar musulmi. Ita dai wannan sandar har wayau ita ce Allah ya ba shi umurnin amfani da ita don samar da ruwan sha ga Banu Isra'ila; mutanensa. Ya bugi wani dutse da ita sai dutsen ya fitar da idanuwan ruwa har goma sha biyu, kowace ƙabila daga cikin su ta riƙa ɗaya suka sha suka ƙoshi. Shi ma Annabi Isa *Alaihis Salam* akwai irin tasa Mu'ujiza wadda ta haɗa da warakar da makafi da kutare da kuma raya wanda ya mutu cikin izinin Allah wanda ya aiko shi. Annabi Salihu *Alaihis Salam* shi kuma Taguwa aka ba shi (Maccen raƙumi) wadda take shayar da mutanen garin dukkansu daga nononta.

114 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 4435 da *Sahih Muslim*, hadisi na 287 daga Abu Huraira *Radhiyallahu Anhu*.

115 An wallafa littattafai da dama a kan wannan batu. *Dala'il An-Nubuwwa* na Baihaƙi na daga cikin mafi kyawonsu da tsaruwarsu.

Sau da yawa Mu'ujiza takan kasance taimako ga Annabawan Allah don fid da su daga wani hali mawuyaci kamar yadda Allah ya taimaki Manzonsa Ibrahim *Alaihis Salam* a lokacin da mutanensa suka yanke shawarar halaka shi, suka tara busasshin itatuwa iyakar iyawarsu, suka cinna ma su wuta ta hauhawa sannan suka ɗora shi a kan bindo suka jefa shi cikin ta, amma Allah ya hana wutar ta taɓa kome a jikinsa, ya fito lafiya sumul kamar bai shiga cikin ta ba.

Irin waɗannan Mu'ujizoji da aka bai wa Annabawan Allah shi ma Manzonmu an ba shi su, kuma an tara ma sa duka na'uoinsu. Babu wata kala ta Mu'ujiza face Manzonmu an ba shi irinta. Wasu malamai sun bibiyi yawan Mu'ujizojinsa suka tarar sun kai dubu.[116] Kasancewar Mu'ujizoji irin waɗannan duk suna wucewa su koma labari abin taɗi ga wanda bai gane su ba, sai Allah ya keɓanci Fiyayyen Halitta da tasa Mu'ujiza wadda ba ta wucewa, ita ce Mu'ujizar Alƙur'ani. Don haka da ita za mu soma. Amma za mu taƙaita mu jejjero wasu daga cikin fitattun Mu'ujizojinsa ne kuma mafiya inganci. Domin wallafa Mu'ujizojinsa gaba ɗaya sai babban kundi wanda ba shi ne maƙasudinmu ba a wannan littafi.

1. Mu'ujizar Alƙur'ani

Ita dai Mu'ujizar Alƙur'ani a fili take, tun da shi tun asali Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba wanda ya iya karatu ko rubutu ba ne amma ya zo da littafi wanda ya gagari duk duniya ta kwaikwayi irin sa, ko ta zo da kwatankwacinsa ko ma wani ɓangare daga cikin sa. Ga shi kuma ya tara ilmoma waɗanda har duniya ta ƙare ba a kai ƙarshensu.

Wannan littafi mai albarka ya tara labaran Annabawa da Manzanni waɗanda suka gabata da abin da ya faru ga kowannensu tsakanin sa da jama'arsa, ta yadda kai ka san tarihi ne da Annabin Allah bai karanto shi wurin wani mutum ba, bai kuma ƙirƙiro shi da tunaninsa ba. Allah ne ya saukar ma sa da shi domin ya zamo darasi ga mutane. Duba yadda Maɗaukakin Sarki ya fayyace labarin Annabi Adamu tun daga halittarsa har zuwa gwagwarmayarsa da Iblisu wanda ya samu sa'ar fitar da shi daga

[116] Ba duka suka inganta ba. Amma ingantattun ma suna da yawa matuƙa. Kuma ya kamata a kullum in za mu yi magana mu tsaya ga abin da ya inganta. Ya ishe mu daga wanda ba shi ba.

cikin aljanna, da tarihin Annabi Nuhu da tsawon shekaru da wahalhalun da ya yi da mutanensa har aka yi ma su ruwan Ɗufana, zuwa ga labarin Annabi Ibrahimu da kiran mahaifinsa da ya yi zuwa ga Musulunci da halin da ya shiga na fuskantar ƙone shi da wuta wadda Allah ya tsirar da shi daga gare ta duniya da lahira, zuwa tarihin 'ya'yansa Annabi Isma'ila mai haƙuri da cika alkawari da Ishaƙa da zuriyyarsa Annabawan Allah; Yaƙubu da Yusufu da cikakken labarinsu tun daga ƙuruciyarsa da ƙaunar da mahaifinsa yake yi ma sa da hasadar 'yan uwansa zuwa matakin da suka ɗauka na jefa shi a cikin rijiya da sayar da shi har zuwa rayuwarsa a gidan sarauta in da aka girmama shi da wata manufa da Allah ya bayyana ta, ya kuɓuta daga wannan makirci zuwa gidan fursuna, da rayuwarsa a can zuwa fitowarsa da samun muƙaminsa, sannan haɗuwarsa da 'yan uwansa da tabbatuwar mafarkinsa. Sai tarihin Annabi Musa tun daga haifuwar sa da yadda Allah ya hana Fir'auna ya kashe shi, a maimakon haka ya ɗauki nauyin renon sa, da hijirarsa daga Masar zuwa ƙasar Madyana da yadda ya yi aure, ya dawo aka ba shi Annabta ya yi arangama da Fir'auna har Allah ya tserar da shi kuma ya gadar ma sa da mulki da dukiyoyin Fir'auna da jama'arsa. Sai tarihin Annabi Isa da mahaifiyarsa wadda uwarta ta sanya ta a hidimar masallaci don neman yardar Allah, da yadda ta haife shi ba tare da uba ba kuma ya yi magana yana jariri don ya wanke ta daga zargi da sauran labarinsa har sadda Yahudu suka yi niyyar kashe shi ubangiji ya ɗauke shi zuwa sama. Da tarihin Annabi Zakariyya da addu'ar da ya yi Allah ya ba shi ɗa mai cikakkiyar ɗa'a da biyayya shi ne Annabi Yahya wanda Allah ya ce bai taɓa sa ma wani ɗa irin sunansa ba, kuma ya ba shi Annabta tun yana yaro ƙarami. Da tarihin Annabi Yunusa wanda ya yi fushi da mutanensa ya yi hijira kafin ya nemi izini sai Allah ya jarabce shi; kifi ya haɗiye shi, amma albarkacin istigfarin da ya yi Allah ya fid da shi ya sake aikinsa zuwa ga mutanensa kuma suka yi imani. Sai kuma Annabawa irin su Dawuda da Sulaimana da mulkin da Allah ya ba su, ya sawwaƙe ma wancan sarrafa ƙarfe da hannunsa ya hore ma wannan tafiya a cikin iska shi da 'yan majalisarsa. Da tarihin Annabi Hudu da Adawa mutanen ƙasar Yaman da Annabi Shu'aibu wanda aka aike shi ga mutanen Madyana 'yan kasuwa masu algussu. Da tarihin Annabi Salihu da Samudawa mutanensa da na Annabi Luɗu da gwagwarmayar isar da saƙon Allah da ya yi ga ƙazaman mutanensa da tarihin Annabi Ayyuba da cutar da ta same shi kuma bayan ya

yi addu'a Allah ya yaye ma sa da sauran Annabawa amincin Allah ya ƙara tabbata a gare su.

Haka kuma a cikinAlƙur'ani akwai labarin matasan nan *Ashabul Kahafi* waɗanda suka yi baccin sama da shekaru ɗari uku a cikin kogo kuma Allah ya tashe su, da labarin Zulƙarnaini wanda ya yawace gabashin duniya da yammacinta kuma Allah ya hore ma sa ayyuka har ya gina babban bango tsakanin mutane da Yajuju wa Majuju. Da Luƙumana da hikimominsa da Karuna da yawan dukiyarsa da Khadir da ilimominsa da mutanen Saba'i waɗanda Allah ya ni'imta su suka yi butulci sai ya tarwatsa su, ya ruguza arzikinsu da labarai na gaskiya iri iri makamantan waɗannan waɗanda babu su a yadda suke a kowane littafi a duniya. Allah Ta'ala ya ce:

((تلك من أنباء الغيب نوحيها إليك ما كنت تعلمهـــا أنـــت ولا قومك من قبل هذا فاصبر إن العاقبة للمتقين)) سورة هود: ٤٩

**Ma'ana:**

> *Waɗancan na daga cikin labaran gaibi waɗanda muke yin wahayin su gare ka, ba ka kasance kana sanin su ba kai da mutanenka a gabanin haka, to, ka yi haƙuri, lalle ƙarshen ƙwarai yana ga masu tsoron Allah.*[117]

Babbar Mu'ujizar Alƙur'ani ita ce kiyaye shi da Allah ya yi; babu mai iya canja kome a cikin sa ko ya ƙara ko ya rage daga ranar da Allah ya saukar da shi kuwa har *Yaumut-tanadi.* Kuma Buwayayyen Sarki ya sawwaƙe shi ta yadda miliyoyin mutane suke iya hardace shi daga *Baƙara* har *Birabbin Nasi* suna karanta shi babu tuntuɓe babu inda-inda.[118]

2. Akwai abubuwan ban mamaki a cikin halittun Allah waɗanda ke nuna Mu'ujiza mai tabbatar da Annabtarsa:

---

117 Suratu Hud: 49

118 Alƙur'ani shi kaɗai ne littafin da ya kai shafi 600 amma ƙaramin yaro ɗan ƙasa da shekaru goma yakeiya hardace shi.

I. Akwai wani dutse da ya kasance yana gai da shi idan ya wuce a Makka yana cewa, *"Amincin Allah gare ka ya kai Annabin Allah!"*

II. Iccen da yake hawa a kan sa ya yi huɗuba ya yi kuka a lokacin da aka yi ma sa Mimbari ya daina hawa a kan sa, sai da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya rarrashe shi sannan ya yi shiru.

III. Tsagewar wata ya rabu biyu a lokacin da kafiran Makka suka ƙalubalance shi da yin haka.

IV. A lokacin bayyanar sa an hana aljanu leƙen asirin da suka saba yi a sama.

V. Jabir *Radhiyallahu Anhu* ya gane ma idonsa wani lokaci da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya nemi wurin biyan bukatarsa ya rasa sai ya kira wasu bishiyoyi guda biyu suka haɗe suka suturta shi har ya yi buƙatarsa sa'an nan suka koma wurinsu.

3. Allah ya sanar da shi wasu abubuwa na gaibi da suka faru waɗanda ɗan Adam bai sanin su sai ta hanyar sanarwar Allah. Ga 'yan misalai kaɗan:

   i. A lokacin da aka kama baffansa Abbas, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya nemi ya fanshi kansa sai ya raya cewa ba shi da kuɗi. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce ma sa: *"To, ina kuɗin da kuka rufe kai da Ummul Fadhli ka ce ma ta, idan an kashe ni wannan kuɗin na 'ya'yan Fdhlu ne da Abdullahi da Kusam?".* Abbas ya ce, na yi amanna kai Manzon Allah ne, domin wallahi ba wanda ya san wannan magana bayan ni da ita.

   ii. Ya ba da labarin cikawar Najjashi a lokacin da yake Madina shi kuma Najjashi yana Habasha.

   iii. Kamar yadda a Madina ya ba da sanarwar yadda yaƙi ya kaya a Mu'uta da kuma yadda kwamandoji uku; Zaidu da Ja'afar da Abdullahi ɗan Rawahata suka samu shahada sannan Khalid ya ja ragamar yaƙi Allah ya ba shi nasara a ranar da abin ya faru.

   iv. Ya gaya ma Umairu ɗan Wahabu ganawar da ya yi a Makka tare da Safwanu ɗan Umayyata da yadda suka shirya kisan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* A dalilin wannan Umairu ya musulunta.

v. Ya ba da labarin wasiƙar da Haɗibu ɗan Abu Balta'ata ya aike ma kafiran Makka yana sanar da su shirin yaƙin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Manzon Allah ya aiki Ali da Zubairu su ƙwato wasiƙar daga hannun tsohuwar da Haɗibu ya aika da ita.

4. Haka kuma ya ba da labarin wasu abubuwa da za su faru kuma suka faru daidai yadda ya faɗe su a bayan rayuwarsa. Ga misalai:

i. A lokacin da Sarki Sabur – wakilin Farisawa - ya ci biranen Sham da sauran yankunan Rumawa har zuwa iyakokin Kusɗanɗiniya, Allah Maɗaukakin Sarki ya yi ma musulmi bushara a cikin Alƙur'ani da cewa, bayan 'yan shekaru kaɗan Rumawa za su mayar da martani su ci galaba a kan Farisawa. Kuma haka abin ya kasance.

ii. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ba da labarin cewa, Umar da Usmanu da Aliyu duk za su yi shahada kuma suka yi ta.

iii. Ya faɗa ma 'yarsa Fatima cewa, ita ce ta farkon da za ta cika daga cikin iyalansa. Kuma haka lamarin ya kasance.

iv. Kamar yadda ya yi nuni ga Zainab daga cikin matansa cewa ita za ta riga su cikawa kuma haka ɗin Sarkin Sarauta ya hukunta.

v. Ya sanar da matarsa A'isha cewa za ta halarci yaƙin basasar raƙumi, kuma ba ta so ba amma sai da aka yi shi a gaban ta.

vi. Ya bayyana cewa, Sayyidi Ali zai yaƙi Khawarij har ya wasafta Dhul Khuwaisira wanda za a kashe daga cikin shugabanninsu. Da aka yi yaƙin sai da Sayyidi Ali ya sa aka nemo shi a cikin gawawwaki.

vii. Ya yi bushara da cewa, jikansa Alhasan zai sasanta rigimar da ke tsakanin musulmi. Aka yi wannan a shekara ta arba'in bayan Hijira.

viii. Ya sanar da Ummu Haram cewa, za ta halarci yaƙin farko da musulmi za su yi a kan teku, amma za ta halarci na biyun ba. Ta je na farkon tare da mijinta a ƙarƙashin jagorancin Sayyidi Mu'awiya kuma ta cika kafin Yazid ya jagoranci na biyun.

ix. Ya sanar cewa Abu Zarri zai cika shi kaɗai ba a cikin jama'a ba kuma haka ta kasance a shekara ta 32H. Sayyidi Ibnu Mas'ud ya biyo ya yi ma sa sallah.

5. Albarkacin addu'oinsa abubuwa na alheri da dama suka faru masu ban mamaki:

i. Ya yi ma Sayyidi Ali addu'a a wani ciwo da ya yi wanda ya yi tsammanin ajalinsa ne. Nan take ya warke kuma bai sake irin wannan ciwon ba. Kamar yadda ya yi ma sa tawada a idonsa mai ciwo a lokacin da za aje yaƙin Kahibar nan take ta warke ya yi ma sa kwamandan kuma ya tafi ya samu nasara da izinin Allah.

ii. Ya mayar da idon Katada ɗan Nu'umanu da ta faɗo a yaƙin Uhud sai ta koma daidai har ta fi ɗaya idon tasa lafiya. Haka shi ma Rifa'atu ɗan Rafi'u idonsa ɗaya ta faɗo a yaƙin Badar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya mayar ma sa da ita ta koma garau.

iii. Albarkacin addu'arsa Allah ya saukar da ruwan sama mai yawa ba lokaci guda ba.

iv. Albarkacin addu'arsa da ya yi ma Anas Allah ya yawaita dukiyarsa da 'ya'yansa har sai da ya yi jana'izar sama da mutum ɗari daga cikin 'ya'ya da jikokinsa da ransa da lafiyarsa. Haka kuma gonarsa tana ba da amfani rani da damana tana kuma fitar da wani ƙamshi da babu shi a sauran gonaki.

v. Shi kuma Ibnu Abbas albarkacin addu'arsa ya zama hamshaƙin malami wanda ba a iya karawa da shi ta fagen ilimi.

vi. Shi kuma Abu Huraira albarkacin addu'ar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* Allah ya azurta shi harda mai ƙarfi a kan Hadisi kuma ya jefa son sa a zukatan musulmi duk inda suke.

vii. A wata kwanciya da Abu Ɗalha ya yi da matarsa Ummu Salama bayan sun rasa yaronsu, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma su addu'a sai suka haifi ɗa mai albarka suka zo da shi ya sa ma sa suna Abdullahi. Wannan yaron cikin albarkar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai da ya haifi 'ya'ya tara mahardatan Alƙur'ani.

viii. As-Sa'ibu ɗan Yazidu ya tsufa sosai har ya zarce shekaru tis'in da huɗu amma da jinsa da ganinsa na ƙalau albarkacin addu'ar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ya yi ma sa.

ix. Abu Zaidi ɗan Akhɗabu wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shafi fuskarsa ya rayu shekaru ɗari da ashirin amma fuskarsa kamar ta matashi; babu alamun tsufa ko kaɗan a cikin ta don tubarrakin hannunsa.

x. A lokacin da Abdullahi ɗan Atiƙu ya kashe Abu Rafi' wanda yake cutata ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bisa ga umurninsa, ya dawo da ƙafarsa a kariye sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shafe ta nan take ta koma daidai kamar ba ta samu matsala ba.

6. Ban da waɗannan akwai kuma abubuwa da dama da Ma'aikin Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sa albarka a cikin su ta bayyana kamar hasken safiya ga mai lafiyayyen idanu:

   i. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sa albarka ga ruwa kaɗan Allah ya yawaita shi har ya wadaci mutane masu ɗinbin yawa, a Tabuka da kuma a Hudaibiya. Akwai ma lokacin da ruwa ya ɓulɓulo ta cikin hannayensa mutane da yawa suka sha suka yi alwala suka yi guzuri.

   ii. Haka kuma ya sa albarka ga abinci a wasu lokuta ɗan kaɗan ya wadaci mutane masu tarin yawa aka ci aka bar shi a yadda yake.

   iii. Ya sanya albarka ga akuya busasshiya wadda take cikin yunwa da wahala nan take nononta ya kawo ya cika hantsarta, ya sha daga ciki kuma ya shayar da jama'a.

7. Allah Maɗakakin Sarki ya taimake shi da wasu Mu'ujizoji a wurare da dama a kan sha'anin da'awarsa:

i. Allah ya kare shi daga harin mazaje jarumawa a lokuta daban dabankamar yadda ya faru ga Abu Jahali da Kindatu ɗan Asad Ma'amaru ɗan Yazidu da Suraƙatu ɗan Malik kuma a lokacin Hijira. Ko wannen su ya yi niyyar halaka shi sai Mu'ujiza ta bayyana wadda Allah ya yi ma sa shamaki da ita zuwa gare shi.

ii. Allah ya aiko Mala'iku sun yi yaƙi don kariyar sa, musulmi da kafirai duk sun gan su da fararen kaya suna kisan kafirai a yaƙin Badar.

iii. Irin haka ne kuma Allah ya ba shi kariya daga rundunar mushrikai ta hanyar korar su da iska mai tsanani wanda ya hana su saƙa, ya kashe wutar da suka hasa, ya tayar da hemominsu a lokacin da suka riski Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a birnin Madina bayan sun yi ma sa taron dangi. Allah Tabaraka wa Ta'ala ya ba da labarin wannan a cikin Suratul Ahzab.[119]

iv. Haka kuma Ubangiji Maɗaukakin Sarki ya taimake shi da halaka gungun 'yan ta'adda masu yi ma sa izgili[120] su biyar a garin Makka: Walid ɗan Mughira[121] da Asi ɗan Wa'il[122] da Aswad ɗan Abdulmuɗɗalib ɗan Harith[123] da Aswad ɗan Abdu Yaguth[124] da kuma Harisu ɗan Ƙaisu.[125] Su kuma sauran masu cutata ma sa sai Allah ya yi maganin su a Badar da takubban musulmi da na Mala'iku. Cikin su har da Abu Jahali da Utbatu da Shaibatu 'ya'yan Rabi'ata da Walidu ɗan Utbatu da Umayyatu ɗan Khalaf da Uƙbatu ɗan Abu Mu'aiɗ. Su ne waɗanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sa aka jefa gawawwakinsu suka ruɓe a cikin rijiyar Badar.

8. Tafiyar dare ɗaya wacce aka yi da shi zuwa masallacin Baitul Maƙdis da ke ƙasar Sham. Daga can kuma ya taka cikin rakiyar Mala'ika Jibrilu ya keta sararin samaniya, suka haura har sama ta bakwai. Daga nan ya je fadar Ubangiji ya gana da shi. Allah ya ba shi lambar yabo, sannan ya dawo ma na da saƙon Sallah kamar yadda za mu gani a nan gaba.

---

119 Suratul Ahzab: 9-11

120 Kamar yadda Allah Ta'ala ya faɗi a cikin Suratun Nahli: 95-96.

121 Su biyar duka sun zo cikin Harami a lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* yake ɗawafi, sai Mala'ika Jibril *Alaihis Salam* ya nuna Walid ga ƙafarsa. Sai ya je wata kibiya ta shiga a ƙafarsa ta halaka shi.

122 Shi ma JIbril *Alaihis Salam* ya nuna ƙafarsa sai ƙaya ta shige ma sa a ƙarƙashin ƙafar ta zamo ajalinsa.

123 Shi kuma Jibril *Alaihis Salam* ya jefa ma sa wani ganye a fuska sai makanta ta kama shi da wani matsanncin ciwon kai, ya rinƙa buga kansa a kan gini har Allah ya kashe shi.

124 Jibril *Alaihis Salam* ya nuna cikinsa, sai cikin ya kumbura ya zama ajalinsa.

125 Jibril *Alaihis Salam* ya nuna kansa sai ya ruɓe har ya fara fitar da wani ruwa mai wari, daga ƙarshe ya cika a wulaƙance.

9. A ranar Uhud Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya bai wa Ukashatu ɗan Muhsan Karen gamba sai ya koma takobi zararre. Daga nan kuma Ukashatu bai sake neman takobi ba, ya ci gaba da yaƙi da wannan kansakali har bayan cikawar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* musamman a lokacin da ya halarci yaƙoƙin Ridda zamanin halifa Abubakar.

10. Akwai alamomin tashin alƙiyama da yawa da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya faɗa. Kananan daga cikin su duk sun bayyana sai ƙalilan ake jira. Manyan kuma idan lokacinsu ya yi babu shakka za su bayyana.[126]

[126] Duba littafin *Ashraɗ As-Sa'a,* na Yusuf Al-Wabil da *Sahih Ahdath An-Nihaya wa Fitan Akhir Az-Zaman,* na Abu Umar Az-Zagbi, bugun Dar Al-Gad Al-Jadid, Alƙahira, 2012M/1433H.

## 2.16.0 Daga Cikin Fifikonsa

Babu wani mahaluki da Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya girmama matsayinsa kamar wannan bawan Allah da muke cikin tarihinsa. Kuma ya keɓance shi da wasu darajoji da ba shi tarayya da kowa a cikin su. Za mu zayyana kaɗan daga cikin su:

### 2.16.1 Fifikon Shiriyarsa

Daga cikin darajojin Ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam* akwai kasancewar shiriyarsa ita ce mafificiya a kan ta kowa. Kuma duk abin da ya saɓa ma umurninsa ko ya kauce daga tafarkinsa sunan wannan abin ɓatacce. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* da kansa ya ba shi shedar cewa, ba shi furuci da son zuciya.[127] Haka kuma Maɗaukakin Sarki ya shedi harshensa da zuciyarsa da ganinsa, ya tabbatar ma sa da mafi kyawo da nagartar halaye. Sanin wannan wajibi ne domin shi ne haƙiƙanin ma'anar shedar da muke yi *Muhammad Rasulullah* a cikin kalmar shahada.

Bisa ga haka, duk wanda yake da wani abin biya wanda yake saɓa ma Manzon Allah, ko yake neman raba gardama a wurin wani ba shi ba, ko yake tafiya kan wani tafarki da ya yi hannun riga da nasa to, wannan bai darajanta Manzon Allah yadda ya dace da matsayinsa ba. Ba ka gani ba, a kullum Allah ya ce a yi ma sa biyayya ko a mayar da al'amari gare shi sai ya mayar da mu ga Manzon nasa? Wane ne yake tarayya da shi a wannan matsayi?

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* shi ne samfurin ɗan Adam wanda Allah yake son ya zame ma na madubi, abin koyi a cikin duk sha'anin rayuwa. Kuma a cikin rayuwarsa ba abin da kake buƙata da zai shiryar da kai sai ka same shi. Da haka ne ya zama addinin Allah ya kammala ba shi buƙatar

[127] Suratun Najm: 1-4.

sabuntawa. Har Allah Maɗaukakin Sarki ya ba da shelar haka a cikin Alƙur'ani.[128]

Sanin haka ne ya sa malaman Sunna tuni suka duƙufa wajen tattara sunnoninsa na addini da na rayuwa. Idan ka samu littafin *Zad Al-Ma'ad Fi Hadyi Khair Al-Ibad* na shaihun malami Al-Hafiz Ibn Kayyim Al-Jauziyya; babban almajirin ɗan Taimiyya, ba abin da zai kuɓuce ma ka ta wannan fannin in Allah ya so. Za ka samu tafarkinsa na cin abinci, da zama, da tafiya, da kwanciya, da magana, da sa tufafi, da alwala, da sallah, da addu'oi da hulɗoɗin zamantakewarsa da masoya da maƙiya da ma kome da kome. Haka kuma zai yi kyau ka nazarci littafin Shehun Malamin na Alƙali Iyadh Al-Yahsubi mai suna *As-Shifa bi Ta'rif Huƙuƙ Al-Musɗafa* za ka ƙara so da sanin fiyayyen halitta. Ina gwanin wani? Ga namu!.

### 2.16.2 Albarkacin Sawunsa

Daga cikin darajojin fiyayyen halitta akwai bayyanar albarkacin sawunsa. Abin nufi, duk abin da Manzon Allah ya dafa hannunsa a kan sa, ko ya jiɓince shi da wata gaɓa daga cikin gaɓɓan jikinsa, wannan abin ya zama mai albarka kuma wanda ake iya samun albarkaci daga cikinsa. Wannan kuwa a rayuwarsa ko bayan cikawarsa. Sahabbai sun nemi albarkar zufansa (guminsa) da yawunsa da sauran abincinsa ko ruwan alwalarsa. Haka kuma sun nemi tubarraki ta hanyar zobensa da tufan jikinsa da takobinsa da gashin kansa da ƙwaryar ruwansa da takalminsa da sauran abubuwan da suka dangance shi. Bari mu ba da wasu 'yan misalai a kan wannan batu daga cikin ingantattun hadisai da ruwayoyin magabata don kar a samu mai jayayya:

i. Sahabbai sun kasance suna neman albarka da waraka ta hanyar wasu sassan jikin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kamar yadda wanzaminsa Abu Talha *Radhiyallahu Anhu* ya

[128] Suratul Ma'ida: 5.

rinƙa ajiye gashin da ya cire daga kansa saboda wannan manufa.[129]

ii. Lamarin fa ba na wasa ba ne a wurin Sahabbai. Anas ɗan Malik *Radhiyallahu Anhu* yana cewa, na fi son a ba ni gashi ƙwara ɗaya daga jikin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a kan a haɗa min duniya da abin da ke cikinta.[130]

iii. Haka kuma suna neman albarka da sauran ruwan alwalarsa kamar yadda Saa'ib ɗan Yazid *Radhiyallahu Anhu* ya yi a gabansa.[131]

iv. Shi kuma Abu Juhaifa *Radhiyallahu Anhu* cewa ya yi: "Na ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a cikin wata jar hema ta kaba, kuma na ga Bilal ya ɗauko ruwan alwalar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* mutane suna ta goggoriyo don samun wannan ruwa. Wanda duk ya samu sai ya shafi fuskarsa da shi, wanda kuwa bai samu ba sai ya shafi damshin hannun wanda ya samu".[132]

v. Abdullahi ɗan Mas'ud *Radhiyallahu Anhu* ya ce, mun kasance tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a wurin tafiya sai ruwa ya ƙaranta, sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, ku nemo sauran ruwa. Sai suka zo da wata ƙwarya da 'yan ruwa kaɗan a ciki. Sai ya shigar da hannunsa a cikin ƙwaryar, sannan ya ce, ku zo ga tsarkakakken ruwa mai albarka. Albarka daga Allah take. Mai ruwaya ya ce: Wallahi na ga ruwa yana ɓuɓɓuga daga yatsun Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Kuma mun kasance muna jin abinci yana tasbihi a yayin da ake cin sa".[133]

---

[129] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 171.
[130] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 170.
[131] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 190.
[132] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 376 da *Sahih Muslim*, hadisi na 1100.
[133] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3579.

vi. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kasance a kan zo ma sa da jinjiri sabuwar haifuwa sai ya sa a kawo ma sa dabino ya tauna shi sannan ya tofa a bakinsa don ya kasance shi ne farkon abin da ya fara shiga a cikinsa. Kamar yadda ya yi wa Abdullahi ɗan Zubair - jinjiri na farko da aka haifa ma musulmi a Madina bayan da musulmi suka tare a cikin ta - lokacin da mahaifiyarsa Asma'u ta zo da shi bayan ta haife shi.[134]

vii. Sawad ɗan Gaziyya *Radhiyallahu Anhu* wani Sahabi ne da ya halarci yaƙin Badar kuma ya yi kwaɗayin haɗa jiki da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* don neman tubarraki da yin haka. Sai ya samu sa'a bisa kuskure Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya soke shi da wani karen itace da ke hannunsa. Don haka, sai ya nemi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ba shi dama ya rama tun da ya ji ma sa ciwo a cewarsa. Mutane suna mamakin irin wannan lamari. Shi kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* saboda tawali'unsa sai ya amince ma sa. Da samun wannan dama sai Sawad ya rungume Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana mai shafa jikinsa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tambaye shi, me ya sa ka yi haka? Ya ce, ya Manzon Allah! Ka ga halin da ake ciki na yaƙi. Akwai yiwuwar ko wane lokaci in bar duniya. Ni kuma ina sha'awar in tafi lahira da jikin da yake ɗanye game da shafar jikinka. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma sa addu'a ya sa ma sa albarka.[135]

---

[134] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3909 da 3910.

[135] Wannan labari na cikin *Al-Musannaf* na Imam Abdurrazzaƙ 3/184 da kuma *Al-Isaba* na Al-Hafiz Ibn Hajar 3/181 daga ruwayar ja'afar ɗan Muhammad As-Sadiƙ daga babansa Muhammad ɗan Ali ɗan Al-Husain ɗan Ali ɗan Abu Ɗalib *Radhiyallahu Anhuma*. Wannan ruwayar ta inganta daga wannan Alami na Ahlulbaiti Muhammad ɗan Ali amma kuma bai faɗi isnadinsa ba. Irin wannan ruwaya ita ake kira *Mursala*. Malaman Hadisi ba su inganta irin ta. Amma na kawo ta ne don mai karatu ya sani cewa, akwai ruwayoyin Ahlulbaiti a cikin littattafan Sunna. Kuma don tana nuna yadda malaman Ahlulbaiti suke ruwaito

viii. Irin wannan ta faru ga Usaid ɗan Hudhair - shugaban ƙabilar Ausu *Radhiyallahu Anhu* kamar yadda ya zo a cikin *As-Sunan Al-Kubra* na Imam Al-Baihaƙi.[136]

ix. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yakan shafi maras lafiya ya yi ma sa addu'a sai ya samu waraka nan take. Misali, a wani lokaci da Jabir ɗan Abdillah ya yi rashin lafiyar da ta tsananta har ta gusar da hankalinsa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ziyarce shi tare da Sayyidi Abubakar *Radhiyallahu Anhu*, sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sa aka kawo ma sa ruwa ya yi alwala sannan ya zuba ma sa saura. Take sai Jabir ya farka. Ya ce, ya Manzon Allah! Me kake umurni na yi a game da dukiyata? Sai Allah ya saukar da ayoyin gado da ke cikin Suratun Nisa'i: 11-14.[137]

x. Haka kuma a lokacin yaƙin Khaibar, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi tofi a idon Sayyidi Ali *Radhiyallahu Anhu* nan take idonsa suka warke bayan da farko bai ko iya fitowa yaƙin ba saboda ciwon da suke yi ma sa.[138]

xi. Wanda ya fi wannan ma shi ne idon Katada ɗan Nu'uman da ta darare har ana son a cire ta. Amma da *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sa hannunsa ya mayar da ita kuma ya yi ma sa tofi a kai nan take sai ta warke har ta fi ɗayar ƙarfin gani da lafiya.[139]

xii. Ya isa abin farin ciki ga duk wani Sahabi ya samu tufan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* don ya yi amfani da shi wajen neman waraka daga wurin Allah. Sayyida Asma'u 'yar Abubakar Siddiƙu *Radhiyallahu Anhu* ta taɓa fitar da wata rigar Manzon

darajojin sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam,* saɓanin yadda 'yan Shi'a; masu da'awar bin su suke yi, na suka da tozartawa a gare su.

[136] *As-Sunan Al-Kubra* na Imam Al-Baihaƙi, hadisi na 13292.

[137] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 194 da kuma na 4577.

[138] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 2847.

[139] *Dala'il An-Nubuwwa* na Imam Al-Baihaƙi 3/251-253.

Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ta samu daga wajen ƙanwarta A'isha suka rinƙa wanke ta ana shayar da ruwan ga marasa lafiya.[140]

xiii. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba kawai ya yi kawaici a kan neman tubarraki da sawunsa da Sahabbai ke yi ba, a'a, ya ma ƙarfafa su a kan haka. Misali, a lokacin da ya kammala hajjinsa na bankwana, an yi ma sa aski sannan sai ya bayar da gashin kansa aka raba ma mutane. Sannan ya yanke ƙumba ita ma ya sa aka raba ma mutane.[141]

xiv. A wuraren yaƙi da makamantansu Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yakan ƙarfafa ma Sahabbai neman albarkacinsa don razana maƙiya ta hanyar nuna ma su girman matsayinsa a wurin musulmi. A Hudaibiya, lokacin da mushrikai suka hana musulmi shiga Makka, jekadan Kuraishawa Urwatu ɗan Mas'ud ya ga abin mamaki matuƙa da ya zo taron sasantawa tsakanin su da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Idan ya bas u umurni suna gaggawa wajen cika shi. Idan ya yi alwala suna ribibi wajen wasashe ruwan su shanye. Idan kuma ya yi kakin majina sai sun yi wuf su sharɓe ta su goge jikinsu da ita. Idan suka yi magana a gabansa kuwa sukan sassauta murya, kuma ba su ɗaga kai su kalle shi saboda girmamawa. Ga abin da Urwatu ya ce ma Kuraishawa da ya koma a wajen su:

"أي قوم، والله لقد وفدت على الملوك، ووفدت على قيصر وكسرى والنجاشي، والله إن رأيت مليكا قط يعظمه أصحابه ما يعظم أصحاب محمد – صلى الله عليه وسلم – محمدا...".

[140] *Sahih Muslim*, hadisi na 5310.

[141] *Al-Musnad* na Imam Ahmad, hadisi na 16521, kuma Sheikh Shu'aib Arna'ut ya inganta shi.

*"Ya ku jama'a! Wallahi na je wajen sarakuna. Na ziyarci sarkin Ruma da na Farisa da na Habasha. Wallahi ban taba ganin sarkin da jama'arsa ke girmama shi irin girmamawar da mutanen Muhammadu suke yi ma sa ba".*[142]

xv. A lokacin da Salman Al-Farisi ya shirya biyan maigidansa da itace 300 na dabino waɗanda zai dasa su don ya fanshi kansa daga ƙangin bauta, ba abin da ya cece shi sai sanya albarka da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ga wannan aiki.[143]

Wannan shi ne Manzon Allah kamar yadda Sahabbansa suka fahimce shi. Haka kuma almajiransu na farko da na ƙarshe mabiya Sunna suka ƙudure matsayinsa a cikin zukatansu. Kuma suka rubuta a cikin littafansu. Wannan ne kuma suke karantar da almajiransu. Akwai abin da Maɗaukakin Sarki ya gani ya ɓatar da waɗannan ababe daga al'ummar musulmi bayan can a da ana samun su jefi-jefi. A shekarar 656H ne da Tattar suka ƙona birnin Bagadaza tare da haɗin guiwar 'yan Shi'a, shugabansu Holaku ya fito da sanda da rigar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ƙona su, ya warwatse tokarsu kamar yadda Imam Suyuti ya faɗa a cikin *Tarikh Al-Khulafa'* da Bagadadi cikin *Khizanat Al-Adab* da Kirmani a cikin *Tarikh Ad-Duwal* da sauran su. A yau akwai wasu ƙwarorin gashi da ake jingina su ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a Istanbul ta ƙasar Turkiyya amma malaman tarihi ba su tabbatar da sahihancinsu ba. Muna burin da za a samu tabbacin ƙwayar gashi

---

142 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 2732 da 2731. Shaihin malami Muhammad Hassan ya bibiyi riwayoyin tarihi, ya ce, bai taɓa ganin sahabbai sun yi ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* a wani wuri ba irin abin da suka yi ma sa a wannan ranar, abin da ya nuna cewa, sun yi haka ne da gangan don isar da wani saƙo na musamman zuwa ga Kuraishawa musamman bayan da Kuraishawan suka zarge su da cewa, ƙauyawa ne kawai da za su gudu su bar shi idan sun ga abin tsoro. Duba: *Al-Fitna Bain As-Sahaba,* na Muhammad Hassan, shafi na 28.

143 *Musnad Ahmad*, hadisi na 23788. Kuma Sheikh Al-Arna'ut ya kyautata shi.

guda ɗaya ta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai mu neme ta mu jiƙa a ruwa mu sha, mu nemi albarkarsa. Matsalarmu da mafiya yawan masu jayayya da mu ba a nan take ba. Son suke yi wannan matsayi na Annabi mu bai wa wasu Shaihunai da suke girmamawa. Mu kuma sam ba mu ajiye kowa a irin wannan matsayin in ba *Sayyidul Wara* ba *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Domin ba a ƙiyasta kowa a kan sa. Ba ka ganin duk Khulafa'u guda huɗu ba su kai kan su a wannan matsayi ba? Ina! Ko alama. Babu wanda ya ce sun yi kafaɗa da kafaɗa da fiyayyen halitta a cikin tsaransu ko mabiyansu ko almajiransu. Don haka, ba ka samun ingantacciyar ruwaya guda ɗaya da ta nuna sun nemi albarkacin rigar ɗayansu ko shantalinsa ko takalmansa. Daga nan ne duk wani zargi ko zagi da ake yi ma malaman Sunna yake samun asali ta ɓangaren waɗanda suke kai wasu a matsayin shugaban halitta, suna ba su matsayin jagoranci da jingina kansu zuwa gare su. Suna neman tubarraki daga sawunsu, suna neman biyan buƙatu daga wurin ƙaburburansu. Dalili na biyu kuma shi ne ƙin bin umurnin shugaban halitta da wasu ke yi sai su saɓa ma Ahlus Sunna. A wurin mabiya Sunna babu wanda ya isa ya tsallake umurnin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bisa ga ko wane irin dalili. Kuma babu wanda ya isa ya haifar da wani abu na bautar Allah ko neman kusanci zuwa gare shi sai shi kaɗai ma'aikin Allah. Don haka, ba su ƙirƙira kome a cikin addini na buki ko murna ko baƙin ciki ko zikiri ko ibada kowa ce iri sai fa abin da shi farin jakadan ya karantar da su. Sun tsaya ga Annabi Muhammadu ba su tsallake shi ba. Shi kaɗai ne limaminsu, kowa ma sai dai ya zama ladan mai jiyarwa. Shi ya sa ba su jinginuwa ga kome sai Sunnarsa. Daman kuma shugaban halitta cewa ya yi: *"Duk wanda ya aikata wani aiki ba bisa umurninmu ba, an mayar ma sa da aikinsa".* Ma'ana ba zai samu lada daga ubangiji a kan wannan aikin ba.[144]

Ya Allah! Ka raya mu a kan tafarkin Manzonka, ka karɓi rayukanmu a kan sa, ka tashe mu a ƙarƙashin tutarsa.

[144] Duba *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 2499 da *Sahih Muslim*, hadisi na 3242 da 3243.

### 2.16.3 Matsayin Iyalansa

Iyalan ko wane mutum su ne adireshinsa. Ma-so-uwa kuwa dole ne ya so ɗanta. Ko a lahira mutane na samun ƙarin daraja a cikin aljanna idan suna cikin iyalan mutumin kirki.[145] To, ina ga iyalan fiyayyen halitta? Kafin mu je ga zancen darajoji da matsayinsu a addini bari mu fara sanin ko su wa ye su. Bismillah:

#### 2.16.3.1 Su Wane ne Iyalansa?

Su wane ne iyalan Manzon Allah? Amsa mafi sauƙi ga wannan tambaya ita ce, iyalansa su ne matansa da kuma waɗanda zumuncinsu da shi ya kai a hana su cin sadaka. A maimakon haka sai aka ce a ba su daga cikin khumusin ganima. Waɗannan sun haɗa da, 'ya'yansa da duk musulmin da ya fito daga zuri'ar Abdulmuɗɗalib kakan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Ga hujjojinmu a kan wannan bayani:

1. **Matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam***

Matan aure a ko wane gida su ne asalin iyali. Kamar yadda Allah ya kira matar Annabi Ibrahim a matsayin iyalinsa.[146] Ita ma matar Annabi Musa ya kira ta a matsayin iyalinsa.[147] Matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* su ma ayoyin da muka kawo na suratul Ahzab sun tabbatar ma su da wannan suna. Kasancewar su cikin iyalansa ya sa ba a ba su sadaka sai dai a ba su daga cikin khumusin ganima. Wannan ne ya sa a lokacin da gwamnan Madina Khalid ɗan Sa'id ɗan Al-Ass ya aika ma Nana A'isha da Sanuwa daga cikin Shanun sadaka sai ta maida ma sa, ta ce ai mu iyalan Muhammad

[145] Suratut Tur: 21.
[146] Suratu Hud: 73
[147] Suratul Kasas: 29

*Sallallahu Alaihi wa Sallam* sadaka ba ta halalta a gare mu.[148] Ya kuwa za ayi dauɗar dukiyar jama'a ta halalta ga matan Manzon Allah alhalin ko 'yantaccen bawan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ya so ya raka wani ma'aikacin zakka dan ƙabilar Bani Makhzum don a raba da shi, Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ce ma sa ya yi *"Ka yi haƙuri. Ba zaka iya cin sadaka ba saboda "'Yantaccen bawan mutane a cikinsu ya ke. Mu kuma sadaka "Zakka" ba ta halalta a gare mu".*[149] Wannan kuma shi ne dalilin da ya sa matan Annabi suka shiga a cikin salati kai tsaye kamar yadda ya zo a wasu ruwayoyi.[150]

Kuma da Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce "Ya Allah! Ka sanya arzikin iyalan Muhammadu ya zamo sese-da-sese". Ai matansa yake nufi. Allah yana cewa:

> *"Ya ku matan Annabi! Ba ku kasance kamar kowa daga cikin mata ba".*[151]

Saboda me ba su daidai da sauran mata? Amsa ita ce, saboda sun zama iyalan gida mafi daraja.

2. **Mutanen *Kisa'i***:

Su ne mutane huɗu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shigar da su a cikin bargonsa a yayin da Allah ya saukar da waccan ayar kan matansa, kuma ya roƙi Allah ya shigar da su a cikin ta. Su ne, Sayyidi Ali da matarsa Nana Fatima da 'ya'yansu biyu; Hasan da Husain *Radhiyallahu Anhum*. Da wannan su ma nassi ya tabbatar da kasancewar su cikin iyalan Annabi.

---

148 *Al-Musannaf* na Ibn Abi Shaiba 3/214.

149 *As-Sunan* na Abu Dawud, hadisi na 1650 da *As-Sunan*, hadisi na 657 da *As-Sunan* na Nasa'i, hadisi na 2611.

150 Duba: *Jala'ul Afham* na Ibn Al-Kayyim, shafi na 331-333.

151 *Suratul Ahzab: 32.*

**3. ƙYa'yansa da Zuriƙarsa**

Waɗannan sun haɗa da; Al-Kasim da Ɗayyib da Ibrahim da Zainab da Ruƙayya da Ummu Kulthum da kuma zuri'arsu gaba ɗaya. Idan Durratu 'yar Abu Lahabi - baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* - tana cikin iyalansa kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da kansa ya faɗa[152] to, ina kuma ga 'ya'yan cikinsa?!

**4. Jikokin Abdulmuɗɗalib:**

Sai kuma sauran dangin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* 'ya'ya da jikoki da zuri'ar Abdulmuɗɗalib. Akwai hadisai da dama da suke tabbatar da kasancewar su Ahlulbaiti, kamar hadisin Durratu da muka kawo a baya. Amma bari mu ƙara guda ɗaya a nan shi ne hadisin 'ya'ya biyu na baffannin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* waɗanda suka nemi ya sanya su a cikin aikin zakka domin su samu abin yin aure, sai ya ce ma su *"Ai zakka ba ta halalta ga iyalan Muhammad, domin ƙazantar mutane ce".* Sannan ya yi umurni aka ba su kuɗin aure daga cikin Khumusin ganima. Waɗannan matasan kuwa su ne Abdulmuɗɗalib ɗan Harith ɗan Abdulmuɗɗalib da kuma Fadhlu ɗan Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib.[153]

Wannan ya nuna ƙarara cewa, duk dangin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* na kusa, waɗanda suka haɗa kaka da shi suna cikin iyalansa. Sharaɗi babba a wannan babi shi ne kasancewar mutum musulmi bayan zaman sa ɗa ko jika ga Abdulmuɗɗalib. Ka ga shi Abu Lahabi bai samu wannan falala ba. Ba don kome ba sai don ya kafirce ma ɗan baffan nasa da Allah mahalicci ya aiko. Amma 'yarsa Durratu da ta miƙa wuya ta bi gaskiya kuma har ta yi hijira, sai Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya hana a cuta

152 *Majma' Az-Zawa'id* na Haithami, hadisi na 15402,
153 Duba *Sahih Muslim*, hadisi na 1072.

ma ta ta hanyar yin maganar mahaifinta da ayoyin da suka sauka a kan sa. Kuma a kan ta ya hau mimbari ya yi huɗuba yana cewa, *"Me ya sa ake cuta min a cikin iyalaina"?!* Su ma 'yan uwanta guda biyu; Utbatu da Mut'ib duk sun musulunta, kuma suna cikin iyalan fiyayyen halitta. Sai ɗan uwansu guda ɗaya shi ne Utaibatu Allah bai yi ma sa rabo ba. Shi ne kuma wanda ya saki Ummu Kulthum -'yar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* - bisa ga umurnin babansa.

Yanzu dai, ka ji su wane ne iyalan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, a mahangar mabiya tafarkin Sunna. Su kam 'yan sha biyu sun jajirce ne cewa mutanen Kisa'i su huɗu ne kawai iyalan Annabi. Suka fitar da matansa da ma sauran 'ya'yansa da duk danginsa daga cikin iyalan babban gida. Sa'an nan suka zaɓi wasu guda tara daga cikin zuri'ar Husaini suka ƙara da su. Sauran dangi kuma duk suka yi watsi da su. A haka kuma suke ganin su ne masoyan Ahlulbaiti! Gidan da suke cin zarafin matansa suna yi ma su ƙage da ƙazafi. Ka samu littafinmu *Su Wane ne Masoyan Ahlulbaiti?* Za ka sha mamaki matuƙa idan ka ga irin cin zarafin da suke yi ma sauran 'ya'yan Annabi da danginsa bayan sun kore su daga zama cikin Ahlulbaiti. Ya Allah muna sheda ma ka cewa, mun barranta daga duk wanda ya cutata ma Manzonka a game da iyalansa ko almajiransa.

### 2.16.4 Darajojin Iyalansa

Idan muna maganar matsayi da darajojin iyalan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* za mu kasa su kashi biyu ne:

1. Darajojin da suka shafi duk membobin wannan babban gida.
2. Sai kuma darajojin da suka keɓanci wasu ɗaiɗaiku daga cikin su.

#### 2.16.4.1 Darajojinsu na Tarayya

Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya kira iyalan gidan Annabawa da sa albarka a gare su. Kamar iyalan Annabi Nuhu[154] da na Annabi Ibrahim[155] da na Annabi Musa[156] da na Annabi Isma'il[157] da na Annabi Lut[158] da na Annabi Ya'ƙub[159] da sauransu. Iyalan Annabinmu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba a bar su a baya ba. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya kira su a cikin Suratul Ahzab[160] a tsakiyar magana a kan wasu membobi masu alfarma a wannan gida su ne matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Allah ya ware ayoyi 7 a cikin wannan sura don magana a kan su. A cikin su ne Maɗaukakin Sarki yake cewa:

**((يا نساء النبي لستن كأحد من النساء إن اتقيتن، فلا تخضعن بالقول فيطمع الذي في قلبه مرض وقلن قولا معروفا * وقرن في بيوتكن ولا تبرجن تبرج الجاهلية الأولى، وأقمن الصلاة وآتين الزكاة وأطعن الله ورسوله، إنما يريد الله ليذهب عنكم الرجس أهل البيت ويطهركم تطهيرا * واذكرن ما يتلى في بيوتكن من آيات الله والحكمة، إن الله كان لطيفا خبيرا* )) سورة الأحزاب: ٣٢-٣٤.**

*"Ya ku matan Annabi! Ba ku zama kamar ko wace ɗaya daga cikin mata ba, idan kun ji tsoron Allah, kada ku sassauta magana sai wanda ke da cuta a cikin zuciyarsa ya yi kwaɗayi (zuwa gare ku), kuma ku faɗi magana wadda ta dace. Ku kuma zauna cikin gidajenku, kada ku yi tsiraici rin na jahiliyyar farko, kuma ku tsayar da salla kuma ku ba da zakka, kuma ku yi ɗa'a ga Allah da Manzonsa. Haƙiƙa, kawai,*

154 Suratul Anbiya': 76
155 Suratu Hud: 73 da Dhariyat: 26
156 Suratun Naml: 7 da Suratu Taha: 10 da Suratul Kasas: 29
157 Suratu Maryam: 55
158 Suratul A'raf: 83 da Suratus Shu'ara': 170
159 Suratu Yusuf: 62
160 Suratul Ahzab: 33

*Allah yana son ne ya tafiyar da ƙazanta daga gare ku ya ku mutanen babban gida, kuma ya tsarkake ku tsarkakewa. Kuma ku tuna abin da ake karantawa a cikin ɗakunanku na ayoyin Allah (Alƙur'ani) da hikima (Hadisi). Tabbas, Allah ya kasance mai luɗufi ne, mai cikakken sani".*[161]

Waɗannan ayoyi sun nuna yadda Maɗaukakin Sarki yake son tsarki ga iyalan Annabinsa gaba ɗaya. A nan gaba za mu yi maganar su wane ne iyalan nasa.

## 2.16.4.2 Darajojin Ɗaiɗaikun su

Akwai darajoji da suka keɓanci wasu daga cikin iyalansa ban da waɗancan darajoji nasu na tarayya. Za mu ba da misalai ɗaya ɗaya kawai saboda takaitawa.

1. Sayyidi Abbas baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ɗan uwan mahaifinsa kuma tsaransa (An haifi Abbas shekaru biyu kafin Manzon Allah). Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kasance tare da kusancin shekarunsu yana darajanta shi a matsayinsa na ƙanen mahaifinsa wanda ya musulunta kuma ya taimaka ma sa. A kan sa ne ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake cewa: "Ashe ba ku san baffan mutum irin babansa ne ba?"[162] Ma'ana, yadda za ku darajanta mahaifina da Allah ya ƙaddari rayuwar sa zuwa yau, haka ya kamata ku darajanta ma ni baffana wanda yake ɗan uwansa.
2. Sayyidi Ali ɗan Abu Ɗalib. Mahaifinsa shi ne wan mahaifin Manzon Allah. Kuma wanda ya kula da shi cikakkiyar kulawa a

[161] Suratul Ahzab: 32-34

[162] *Sahih Muslim*, hadisi na 983.

lokacin da ya rasa kakansa da mahaifiyarsa. Darajojinsa suna da yawa. Cikin su har da faɗin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa, ba mai son sa sai mumini, kuma ba mai ƙin sa sai munafuki.[163]

3. Matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: Ya ishe su daraja cewa, Allah ya ce su iyayen mummunai ne.[164] Kuma ba musulmin da ke shakka cewa, su matayensa ne a duniya da lahira. A kan haka ne ma Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya hana a aure su bayan sa.[165]
4. Nana Fatima: 'Yar autan 'ya'yan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* mata. Daga cikin falalarta akwai cewar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: "Fatima tsoka ce daga jikina. Abin da ya dame ta ya dame ni". A wata ruwaya: "Duk wanda ya fusata ta ya fusata ni".[166] Duk da kasancewar sauran 'ya'yan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* duk suna shiga a cikin wannan magana amma furta sunanta a nan, da kasancewar maganar an yi ta ne saboda ita yana ba ta ƙarin matsayi da daraja. Sai kuma 'ya'yanta:
5. Hasan da Husain: Daga cikin falalarsu akwai faɗar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*: "Al-Hasan da Al-Husain su ne farin cikina na duniya".[167]
6. Abdullahi ɗan Abbas: Kanen Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ta wajen baffansa Abbas. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma sa addu'a a kan Allah ya ilmantar da shi addini, ya sanar da shi fassarar Kur'ani.[168] Babu shakka kuwa wannan addu'a Allah ya karɓe ta. Domin kuwa ɗan Abbas yaro ne ƙarami da ƙalilan ne ilmin da ya ɗauka daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi*

[163] *Sahih Muslim*, hadisi na 113.
[164] Suratul Ahzab: 6.
[165] Suratul Ahzab: 53.
[166] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3437 da 3483 da *Sahih Muslim* hadisi na 4482.
[167] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3470 da na 5535.
[168] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 75. Duba kuma tafsirin Ibn Kathir (1/115).

*wa Sallam*, amma ya bibiyi magabatan Sahabbai yana darajanta su, yana ɗaukar karatu a wurin su har Allah ya kai shi matsayin da ya fice na kowa a bayan rasuwar su. Dubi abin da Imam As-Sha'abi yake cewa: "An yi jana'izar mahaifiyar Zaidu ɗan Thabit *Radhiyallahu Anhu*. Da aka ƙare sai aka janyo ma sa alfadararsa zai hau. Sai ɗan Abbas ya zo ya riƙa ma sa linzaminta. Sai Zaidu ya ce, haba ɗan baffan Manzon Allah! Ka saki kawai. Sai ɗan Abbas ya ce, ai haka aka ce mu yi wa malamanmu. Shi kuma Zaidu sai ya sauko ya sumbaci hannun ɗan Abbas ya ce, mu kuma haka aka ce mu yi ma iyalan Annabinmu.[169]

Wannan na nuna ƙarara irin mutunta juna da ke tsakanin iyalan Annabi da Sahabbansa. Saɓanin tatsuniyoyin da 'yan Shi'ah suka kitsa kuma wasu littattafan tarihi na ruwaya suka ɗauko. Masu raunin imani da ƙarancin sanin waɗannan bayin Allah su ke gina aƙidunsu a kan irin waɗannan ruwayoyi. In da za su koma ga Alƙur'ani abin da ya faɗi a kan su kawai ya ishe su. Mutanen da Allah ya ce, masu jinƙan junan su ne, ina zaka gaskata mai cewa suna gaba da juna?!

### 2.16.4.3 Matsayin *Ahlulbaiti* a Wurin Musulmi

Sanin duk mai bibiyar tarihin musulmin farko ne cewa, iyalan Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sun kasance abin girmamawa da darajantawa matuƙa a tsakanin musulmi, musamman ma dai Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Wannan ya sa al'ummar musulmi ta shiga wani hali mawuyaci a lokacin da ƙaddarar Allah ta gudana, 'yan Shi'a suka gayyaci Sayyidi Husaini kuma suka tozarta shi, suka miƙa shi aka kashe shi a cikin

[169] Duba: *At-Tabaƙat Al-Kubra* na Ibn Sa'ad 2/370 da *Siyar A'lam An-Nubala'* na Dhahabi 2/437. Kuma shaihun malami Ibnu Hajar ya karfafa isnadin wannan labari a cikin *Fath Al-Bari* 11/57.

garinsu tare da danginsa; jikokin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Al'ummar musulmi ta girgiza matuƙa da wannan al'amari.

## 2.17 Darajar Sahabbansa

Babu wani zamani da ya kai alherin na Manzon Allah. Babu kuma wasu mutane da suka kai alherin mutanensa, waɗanda suka ba da gaskiya gare shi, suka taimake shi. Su ne abokan rayuwarsa, abokan hulɗarsa, maƙwautansa, surukansa, almajiransa, sojojinsa. Da su ne ya yaƙi duniya har ya isar da saƙon Allah. Babu yadda za ka iya raba rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ta Sahabbansa. Domin kuwa ba zai kasance liman ba in ba don suna bayansa ba. Ba zai zama kwamanda ba in ba don sojojinsu suna kewaye da shi suna yaki ƙarƙashin tutarsa ba. Ba zai zama malami ba in ba don sun gurfana suna ɗaukar karatu a wurinsa ba.

Idan akwai wani mahaluki wanda zama da shi yake janyo kusanci zuwa ga Allah. Idan akwai wani mahaluki wanda haɗa hannu da shi yake sa a samu matsayi a wurin Allah. Idan akwai wani bawan Allah wanda taimakonsa yake sa a samu yardar Allah. To, babu shakka duk musulmi sun sani wannan mutum shi ne ɗan Amina fiyayyen halitta. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya sanar da Sahabbai cewa, kasancewar su a zamanin Manzo ba al'amari ne na wasa ba. Allah ya ce:

> *"Kuma ku sani a cikin ku akwai Manzon Allah. In da zai biye ma ra'ayinku a cikin al'amurra da yawa da zaku wahala. Amma Allah shi ne ya soyar da imani a gare ku, kuma ya ƙawatar da shi a cikin zukatanku, kuma ya ƙyamatar da kafirci da fasiƙanci da saɓo zuwa gare ku. Waɗancan su ne shiryayyu. Falala ce daga Allah (wadda ya*

*yi ta a gare ku) da ni'ima. Kuma Allah mai cikakken sani ne, mai cikakkiyar gwaninta".*[170]

To, ka ji fa. Allah yana ba da sheda a kan su kamar haka:

1. Zama da suka yi da Manzon Allah babbar daraja ce da babu irin ta

2. Sahabbai masu ƙoƙarin bautar Allah ne har sai Annabi ya taka ma su birki don gudun wahala ta cim ma su.

3. Allah ya sanya ma su son imani kuma ya ƙawata shi a zukatansu, babu abin da suke sha'awa kamar sa. Don haka ne ma suke sadaukar da kome nasu a kan sa.

4. Sahabbai ba su son kafirci ko fasiƙanci ko saɓo. Suna gudun waɗannan ababe iya ƙoƙarinsu.

5. Wannan kuma aikin Allah ne da ya zaɓe su don sahibtar Manzonsa sai ya sa suka zamo haka. Kuma wata falala ce da ni'ima daga wurin sa.

6. Allah cikin cikakken saninsa da gwanintarsa ne ya yi haka. Don haka, da ya san za su canja ko ba su cancanta ba tun farko ba zai zaɓe su ba. Ya kuwa za ayi mutanen da tun ba a halicce su ba Allah ya ba da bushara da su a cikin At-Taura da Linjila, sannan za su canja addini ko su lalace bayan shiriyarsu?![171]

Duk wanda zai zo bayan Sahabbai sai dai ya riski wata falala amma su kam sun kwashe kashin farko. Tun da ba zaka iya taimakon Annabi da kariyar sa da yin hijira zuwa gare shi da miƙa masa sadakarka hannu da hannu ba. Ballantana ace ka nemi shawararsa ko ka yi fatawa a wurin sa ko kuma ya nemi shawara a wurin ka, ko ka auri 'yarsa ko ka aura ma sa taka. Kai, ko ma ya shedi ɗaurin aurenka ko ya yi addu'a a gare ka ko ya halarci jana'izarka. Wannan duk yana cikin rabon da Sahabbai sun riga sun yi gaba da shi. Ya za

[170] *Suratul Hujurat: 7-8.*

[171] Duba Suratu Muhammad: 29 ka ga busharar da muka fada ma ka.

ayi ka cim ma mutanen da fatawoyinsu da amsoshin da Allah ya ba su suna cikin Al-Kur'ani?[172] Kuma waɗanda suka yi yaƙi sahu ɗaya da Mala'iku, a ƙarƙashin jagorancin fiyayyen halitta?[173] Kuma waɗanda Allah ya umurci Annabinsa ya yi shawara da su?[174] Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya kasa musulmi kashi uku; Muhajirai da Ansarai da waɗanda suka bi su da kyakkyawar addu'a.[175] Ashe kenan ba shi a cikin musulmi wanda ke bin dugadugansu don ya fito da laifinsu ko kuskurensu.

Darajar Sahabbai ta kai su keta doka - bisa halayyar 'yan Adam ta kasawa - amma a cikin lumana da rarrashi ubangijinmu ya ba da shelar ya yafe ma su. Kamar abin da ya faru a Uhud lokacin da baraden Musulunci suka kasa jure wahalar da ta kewaye su bayan nasara ta juya zuwa gefen abokan gaba. Suka kuwa rinƙa zurawa da gudu a cikin firgici da tashin hankali. Wannan zunubin kuwa - gudu a fagen jihadi - babbar kaba'ira ce da Allah ya yi ƙyaci mai tsanani a kan ta. Kuma ya ce, duk wanda ya yi haka zai gamu da fushin Allah, ya ɗanɗani ƙunar azabar wuta.[176] To, amma su da yake 'yan gata ne, dubi abin da Allah ya ce mu su:

> *"Haƙiƙa waɗannan da suka juya (suka gudu) daga cikin ku a ranar da rundunoni biyu suka hadu (Ranar Uhud) Shaiɗan ne ya ribace su da sashen abin da suka yi na zunubi, kuma haƙiƙa, wallahi Allah ya yafe ma su. Haƙiƙa Allah mai yawan gafara ne, mai yawan haƙuri"*[177]

A ɗaya ayar kuma ya ce:

---

[172] Duba misali a Suratul Baƙarah kawai waɗannan ayoyi: 189, 215, 217, 219, 220 da 222.
[173] Duba Suratu Ali Imran: 124-126 da Suratul Anfal: 12.
[174] Suratu Ali Imran: 159.
[175] Suratul Hashr: 8-10.
[176] Suratul Anfal: 16-17.
[177] *Suratu Ali Imran: 155.*

*"Sannan sai Allah ya juyar da ku daga gare su domin ya jarabce ku. Kuma haƙiƙa, wallahi Allah ya yafe ma ku. Haƙiƙa, Allah mai baiwa ne a kan mummunai".*[178]

Duk da wannan laifin nasu ga shi dai Allah yana kiran su mummunai kuma yana shelanta ya yafe ma su har da rantsuwa da ƙarfafawa.

### 2.17.1 Me ya Banbanta Sahabban Annabi?

Akwai abubuwan da Sahabban Manzon Allah suka keɓanta da su waɗanda suka fifita su a kan sauran musulmi da ke bayan su:

1. Zamantakewarsu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ganin mu'ujizoji da karamomin da Allah ya darajanta shi da su, sun sanya ma su tsarkin zuciya game da son Allah da Manzonsa. Duba a Suratun Nisa'i yadda Allah yake ba da shaidar kyakkyawar niyyar da suke da ita wurin jihadi. Allah ya ce:

(( وَلا تَهِنُوا فِي ابْتِغَاءِ الْقَوْمِ إِنْ تَكُونُوا تَأْلَمُونَ فَإِنَّهُمْ يَأْلَمُونَ كَمَا تَأْلَمُونَ وَتَرْجُونَ مِنَ اللَّهِ مَا لا يَرْجُونَ وَكَانَ اللَّهُ عَلِيماً حَكِيماً )) سورة النساء: ١٠٤

**Ma'ana:**

*"Kuma kada ku yi rauni wajen neman mutanen (kafirai). Idan har kuna jin zafi to, su ma fa suna jin sa kamar yadda kuke ji, sa'annan kuna da wata fata daga Allah wacce su ba su da ita".*[179]

A Suratul Fathi, Maɗaukakin Sarki ya ba da irin wannan sheda in da yake cewa:

[178] *Suratu Ali Imran: 152.*
[179] *Suratun Nisa'i: 104.*

((لقد رضي الله عن المؤمنين إذ يبايعونك تحت الشجرة فعلم ما قلوبهم

فأنزل السكينة عليهم وأثابهم فتحا قريبا)) سورة الفتح: ١٨

*Ma'ana:*

> *"Haƙiƙa, Allah ya yarda da mummunai a lokacin da suke yi ma ka mubaya'a a ƙarƙashin bishiyar nan, sai ya dubi abin da ke cikin zukatansu sai ya saukar ma su da natsuwa kuma ya saka ma su da buɗi kusa-kusa".*[180]

Ka ga a nan ga yardar da Allah ya yi da su, ga kuma shaidar gaskiyar imanin da ke cikin zukatansu.

2. Suna da gaggawa wajen bin umurnin Allah da Manzonsa da kai matuƙa wajen ibada tare da yin ta bisa koyarwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Misali, a cikin 'yan ƙalilan shekaru ne suka karɓi canjin da Manzo ya zo ma su da shi daga ilahirin al'adun da suka gada daga iyaye da kakanni. Sai suka koma wata al'umma daban bisa samfurin ɗan Adam da Allah yake so. Kuma a cikin shekaru 10 kacal suka yi jihadi da yaɗa da'awar Musulunci suka ci nasarorin da a shekaru 100 aikin yana da wuya in ba don ƙarfafawar Allah da taimakonsa a gare su ba. Don haka ne Maɗaukakin Sarki ya ce:

((لكن الرسول والذين آمنوا معه جاهدوا بأموالهم وأنفسهم في سبيل الله، وأولئك

لهم الخيرات وأولئك هم المفلحون * أعد الله لهم جنات تجري من تحتها الأنهار

خالدين فيها، ذلك الفوز العظيم)) سورة التوبة: ٨٨-٨٩

3. Ga su da cikakkiyar fahimtar Musulunci bisa karantarwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Don haka, ba su faifayewa ba su kasawa. Shi ya sa Allah ya ce ma *Ahlulkitabi*, *"Idan sun yi imani da*

[180] *Suratul Fath:18. Duba kuma Suratu Ali Imran: 154*

*irin abin da kuka yi imani da shi to fa sun shiriya".*[181] Ashe imaninsu ma shi ne samfurin imanin da Allah ya amince da shi. Ba mamaki, Sahabbai ba su yi bidi'a ba. Duk bidi'oi sun bayyana ne a ƙarshen zamaninsu kuma su ne suka yi faɗa da su, suka kare sunnar da baban Kasim ya bar su a kan ta. Har malamai suka sheda cewa, babu sunan Sahabi ko ɗaya a cikin mabiyan aƙidu daban daban da suka ɓulla a cikin Musulunci daga baya.

4. Suna sadaukar da duk abin da suka mallaka tun daga kuɗi har lokaci da ƙarfin jiki zuwa jininsu da rayuwarsu don ɗaukakar addini. Dubi irin yabon da Allah ya yi ma su bayan ya kasa su kashi biyu; Muhajiruna da Ansar.[182] Ya yabi waɗancan a kan hijirarsu da haƙuri a kan cutarwar mushrikai da tsarkin zukatansu wajen neman yardar Allah. Su kuma waɗannan ya yabe su da taimakon Allah da Manzo da karɓar baƙuncin 'yan uwansu Muhajirai da ƙaunar su da karrama su da fifita su a kan kawunansu. Sannan ya sifaita waɗancan da "masu gaskiya", waɗannan kuma da "masu rabauta". A Suratut Taubah[183] kuma sai Allah ya shelanta cewa, ya yarda da su duka kuma sun yarda da shi.

A ranar da Sayyidi Umar ɗan Haɗɗabii ya musulunta, adadin Sahabbai ya cika 40 cif, sai Allah ya ce ma Manzonsa:

(( يَا أَيُّهَا النَّبِيُّ حَسْبُكَ اللَّهُ وَمَنِ اتَّبَعَكَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ )) سورة الأنفال: ٦٤

*"Ya kai Annabi! Allah ya ishe ka, kuma ya ishi waɗanda suka bi ka daga cikin mummunai".*[184]

5. Suna da kyawawan ɗabi'u da suka koya daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Don haka suka fi kowa adalci da karimci da gaskiya da jarunta da riƙon amana. Ita kam ƙarya ba a

181 Suratul Baƙarah: 137.
182 Suratul Hashr: 8-10
183 Suratut Taubah: 100
184 *Suratul Anfal: 64.*

san ta ba ma sam, sai bayan zamaninsu. Domin ko kafin su musulunta babbar abin kunya ce a wurin su kamar yadda muka gani a can baya. Ba mamaki a samu ɗaya ko biyu daga cikinsu Sheɗan ya samu sa'ar su sun yi ƙarya sannan suka tuba. Amma ba dabi'arsu ce ba. Ba ka ji Allah ya yabe su ba da cewa:

((أولئك هم الصادقون))

*"Waɗancan su ne masu gaskiya"*[185]

Don haka, gaskiya ita ce siffarsu ba ƙarya ba. Da waɗannan kyawawan ɗabi'un ne, gami da jihadi da son Allah da Manzo suka zamo *"mafificiyar al'ummar da aka fitar ma mutane"*.[186]

**2.17.2 Darajojin Ɗaiɗaikunsu:**

1. Akwai wanda Mala'ika Jibril *Alaihis Salam* yake saukowa a cikin siffarsa. Shi ne kuma jekadan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* Dihyatu ɗan Khalifa Al-Kalbi.

2. Akwai wanda Allah ya kira shi abokin Manzon Allah. A ranar hijira shi Allah ya zaɓa ma Manzonsa don ya abokance shi. Shi ne Abubakar Siddiƙ.[187]

3. Akwai wanda ya sha nono tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, uwa ɗaya ta yi renon su. Shi ne Usmanu ɗan Maz'un.

4. Akwai waɗanda suka limanci Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a sallah. Su ne Abubakar Siddiƙ[188] da Abdurrahman ɗan Auf[189].

---

[185] Suratul Hujurat: 15 da Suratul Hashr: 8.
[186] Kamar yadda Allah ya faɗe su a Suratu Ali imran: 110.

[187] Suratut Taubah: 40.
[188] *AS-Sunan* na Tirmidhi, hadisi na 362
[189] *Sahih Muslim,* hadisi na 274

5. Akwai wanda ya yi aiki da wata aya shi kaɗai kafin a shafe hukuncinta. A ranar hijira kuma shi ya kwanta a kan gado madadin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Shi ne Ali ɗan Abu Ɗalib.

6. Akwai wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce Allah ya yi magana da shi gaba da gaba. Shi ne Abdullahi ɗan Haram; mahaifin Jabir.

7. Akwai cikin su wanda Mala'iku suka gaisa da shi; suka yi ma sa sallama. Shi ne Imran ɗan Husain.

8. Akwai kuma wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce Mala'iku suna jin nauyin sa. Shi ne surukinsa Usmanu ɗan Affan.

9. Sai wanda Mala'iku suka yi ma sa wankan janaba bayan ya yi shahada yana ɗauke da ita. Shi ne Hanzalatu ɗan Abu Amir.

10. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, al'arshin Ubangiji mai rahama ya girgiza saboda mutuwarsa. Shi ne Sa'adu ɗan Mu'azu.

11. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, Allah ya sanya ma sa fukafukai biyu cikin aljanna. Shi ne Ja'afar ɗan Abu Ɗalib.

12. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, ya ji sawun tafiyarsa cikin aljanna. Shi ne Bilal ɗan Rabah.

13. Akwai wanda Manzon Allah ya fanshe shi da iyayensa. Shi ne Sa'ad ɗan Abi Waƙƙas.

14. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, shi ne sakataren wannan al'umma: Abu Ubaidata ɗan Jarrahi.

15. Akwai wanda Annabi ya ce shi ne farkon wanda zai shiga aljanna daga cikin wannan al'umma. Shi ne Abubakar Siddiƙu.[190]

[190] *Sunan Abi Dawud*, Littafin Sunna, Babin Halifofi, hadisi na 4652 da *Al-Mustadrik* na Hakim (3/73) kuma Hakim da Dhahabi sun inganta shi.

16. Akwai waɗanda Manzon Allah ya ce, su ne shugabannin matasan aljanna: Al-Hasan da Al-Husain 'ya'yan Ali.

17. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, zan ba da tutar yaƙi gobe ga wanda Allah da Manzo ke so kuma yana son su, sai ya ba da ita gare shi. Shi ne baban waɗancan matasa; Ali ɗan Abu Ɗalib.

18. Akwai wanda yawun Manzon Allah ne suka fara shiga cikin sa tun zuwan sa duniya. Shi ne: Abdullahi ɗan Zubair.

19. Akwai wanda shi ne ƙarshen wanda ya haɗa jiki da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a nan duniya. Shi ne Mughira ɗan Shu'uba.

20. Akwai wanda Allah ya faɗi sunansa ƙarara cikin Alƙur'ani. Shi ne Zaidu ɗan Haritha.[191] Shi ne kuma wanda ya raka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zuwa wajen wa'azi a garin Ɗa'if aka yi ma su ruwan duwatsu har suka yi jina-jina.

21. Akwai wanda Allah ya faɗi imaninsa a cikin Alƙur'ani. Shi ne Abdullahi ɗan Salam.[192]

22. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, zai shiga aljanna babu hisabi. Shi ne Ukasha ɗan Muhsan.

23. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, Allah yake yi ma sa ilhami. Shi ne Umar ɗan Haɗɗabi. Shi ne kuma wanda ya sha ba da shawara sai Allah ya saukar da Alƙur'ani a kan amincewa da ita.

24. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, shi ne shugaban makarantan Al-Kur'ani na wannan al'umma: Ubayyu ɗan Ka'ab.

25. Akwai wanda ya karanta ma Manzon Allah Alƙur'ani bisa ga umurninsa. Manzon Allah ya saurare shi har ya yi kuka. Shi ne Abdullahi ɗan Mas'ud.

---

[191] Suratul Ahzab: 37
[192] Suratul Ahƙaf: 10

26. Akwai wanda Manzon Allah ya tsaya bayan gidansa yana sauraren karatunsa, kuma ya yaba ma karatun nasa, har ya ce, “Lallai an ba ka molo daga cikin molayen Annabi Dawud” saboda daɗin karatunsa. Shi ne Abu Musa Al-Ash'ari.

27. Akwai wanda Manzon Allah ya ɗauki shawararsa a yaƙin Hunain. Shi ne Al-Hubab ɗan Al-Mundhir.

28. Akwai kuma wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi aiki da ra’ayinsa a yaƙin Khandaƙ. Shi ne Salman al-Farisi.

29. Akwai wanda yake abokin sirrin Manzon Allah ne. Shi ne Huzaifa ɗan Al-Yamani.

30. Akwai wanda Manzon Allah ya amince ma sa a kan iyalansa. Shi ne Abdurrahman ɗan Auf.

31. Akwai wanda Manzon Allah ya ce, shi ne ya fi kowa sanin ilimin halal da haram a cikin wannan al'umma. Shi ne Mu'azu ɗan Jabal.

32. Akwai shugabar matan aljanna. Kamar yadda Manzon Allah ya faɗi. Ita ce 'yarsa Nana Fatima.

33. Akwai wacce Allah ya gina ma ta gida a cikin aljanna. Kuma ya ce Manzon Allah ya yi ma ta bushara. Ita ce uwargidansa Nana Khadija.

34. Akwai kuma wacce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce ya shiga aljanna sai ya gan ta a ciki. Ita ce Rumaisa'u ‘yar Malhan.

35. Sai wacce Allah ya ɗaura aurenta a sama. Ita ce, Zainab ‘yar Jahsh.[193]

36. A cikin su akwai wacce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, ta yi tuban da, da an raba shi ga mutane 70 daga cikin mutanen Madina ya ishe su. Ita ce Al-Ghamidhiyya.

[193] Suratul Ahzab: 37

37. Akwai wacce a bisa cinyarta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya cika. Kuma yawunta ne ƙarshen abin da ya shiga cikin cikinsa kafin ya bar duniya. Ita ce babbar masoyiyarsa, budurwar matarsa Nana A'isha.

38. Akwai a cikin matan Manzo wacce suka samu yamutsi da ita irin wanda aka saba har ya yi fushi da ita. Allah ya umurci Jibrilu *Alaihis Salam* ya ce ma sa ya dawo da aurenta, domin tana yawan azumi da sallar dare, kuma matarsa ce a duniya da lahira. Ita ce Hafsa 'yar Umar ɗan Haɗɗabi.

39. Akwai wacce take ciwon fyarfyaɗiya Annabi ya ce ta yi haƙuri zata shiga aljanna. Tarihi bai riƙe ma na sunanta ba.

40. Akwai waɗanda Manzon Allah ya yi ma su addu'a kamar Mu'awiya da ya ce, *"Ya Allah ka sanar da shi littafi da lissafi kuma ka kare shi daga azaba"* da Ibnu Abbas da Manzon Allah ya roƙa ma sa Allah ya sanar da shi fassarar Alƙur'ani.

Sannan akwai jekadun Manzon Allah[194] da wakilansa[195] da masu hidimarsa[196] da bayinsa waɗanda ya ɗiyauta[197] da masu gadinsa[198] da

[194] Misali, akwai Amru ɗan Umayyata jekadansa zuwa ga Najashi da Abdullahi ɗan Huzafata jekadansa zuwa Kisran Farisa da Haɗibu ɗan Abu Balta'ata jekadansa zuwa Muƙauƙis na Iskandariyya da Dihyatu Al-Kalbi jekadansa zuwa Sarkin Ruma da dai sauransu. Duba: *Sufara' Ar-Rasul,* na Mu'ayyidh bn Muslih Al-Karani a www.manhal.net.

[195] Akwai wakilansa na karɓar Zakka irin su Abu Huraira, akwai kuma wakilansa wajen neman aure kamar Maulansa Abu Raafi' wanda ya wakilta wajen neman auren Sayyida Maimunatu *Radhiyallahu Anha.*

[196] Suna da yawa matuƙa cikin maza da mata. Daga cikin su akwai Anas ɗan Malik da Ibnu Mas'ud da Maimun Al'a'raji da Ruzainatu da Khaulatu da Radhwa da Maimunatu 'yar Sa'ad.

[197] Bayin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya mallaka kuma ya ɗiyauta su saboda Allah suna da yawa. Sarkin Musulmi Umar ɗan Abdulaziz na yawan kula da su har ma ya sa an yi ma su rajista ta musamman a zamaninsa. A cikin su akwai Safina da Aslam Abu Raafi' da Aiman Al-Habashi da Thauban. Duba: *As-Sirah An-Nabawiyya wa Al-Mu'jizaat,* na Muhammad ɗan Ahmad Kan'aan, shafi na 361.

[198] irin su Mughira ɗan Shu'uba da Kaisu ɗan Sa'ad

kwamandojinsa[199] da marubutansa[200] da masu masaukinsa[201] da surukansa[202] da maƙwautansa da wanzamansa[203] da ladanansa[204] da sauransu.

Dubi yadda Allah cikin ikonsa ya ɗaukaka waɗannan bayi nasa, ya fifita su da darajoji iri-iri ko wacce kana sha'awar ace kai ne ka same ta. Amma sai 'yan Shi'a suka sanya wariya a tsakanin su; su yaba ma wannan, su kushe ma wannan. Suka ƙago labarai marasa tushe da inganci suka jingina ma su suna yaudarar jahilai da su. Suka yi fatali da duk yabon da Allah ya sha yi ma su a cikin Alƙur'ani, da cewar da ya yi a kan su *"Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waɗanda ke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, masu jinƙayi ne a tsakanin junansu".*[205] Suka sanya wata irin gaba da ƙiyayya a tsakaninsu wadda babu ta sai a cikin ƙwaƙwalensu. Ya Allah! Muna godiya gare ka da ka ba mu hasken sanin littafinka, muka gano matsayin waɗannan mutane da ka zaɓa daga cikin maganarka. Muka so su, muka ƙaunace su, muka yi uzuri ga waɗanda ka jarabce su daga cikin su. Muka ce ma su gaba ɗaya "*Radhiyallahu Anhum*" kamar yadda ka ce ma su.[206] Allah! Muna tawassuli da imanin da muka yi da Alƙur'ani ka shiryi masu tsarkin zuciya daga cikin 'yan uwanmu waɗanda wancan santsi ya kwashe su, ka haɗe mu da su gaba ɗaya a tafarkin gaskiya don mu haɗu a cikin gidan rahamarka. Ya Allah! Kai mai ji ne, mai karɓawa.

---

199 Suna da yawa matuƙa kamar yawan yaƙoƙinsa.
200 Irin su Abaan Al'umawi da Mu'awiya ɗan Abu Sufyan da Ubayyu ɗan Ka'ab da Hanzalatu At-Tamimi daKhalid ɗan Sa'id da Zaid ɗan Thabit
201 Irin su Arƙam ɗan Abul Arƙam da Ubayyu ɗan Ka'ab
202 Surukansa da ya aurar ma 'ya'ya su uku ne: Abul Asi ɗan Rabi'u da Usmanu ɗan Affana da Ali ɗan Abu Ɗalib. Surukansa Musulmi waɗanda ya auri 'ya'yansu sun haɗa da: Sayyidi Abubakar – Mahaifin A'isha, da Umar – Mahaifin Hafsa, da Abu Sufyan – Mahaifin Ummu Habiba, da Harith ɗan Abu Dhirar – Mahaifin Juwairiya. Akwai kuma surukai mata irin su Sayyida Ummu Ruman 'yar Amir mahaifiyar A'isha da Hindu mahaifiyar Ramlatu 'yar Abu Sufyan
203 Irin su Abu Musa Al-Ash'ari
204 Irin su Bilal da Abu Mahdhura da Ibn Ummi Maktum da Sa'ad Al-Karz
205 Suratul Fathi: 29
206 Suratut Tauba: 100

Za mu rufe wannan magana da kalaman Sayyidi Abdulƙadir Al-Jailani jikan Sayyidi Al-Hasan ɗan Ali ɗan Abu Ɗalib yardar Allah ta tabbata a gare su a cikin littafinsa Jagoran Masu Neman Gaskiya[207]. Ga abin da ya ce:

*"Kuma Ahlus Sunna sun haɗu a kan wajabcin kamewa daga abin da ya gudana a tsakanin su, da barin faɗin kurakuransu, da bayyana kyawawan ayyukansu da darajojinsu, da barin lamarinsu ga Allah Maɗaukakin Sarki, tare da duk abin da ya faru a tsakaninsu na saɓani tsakanin Ali da Ɗalha da Zubairu da Nana A'isha da Mu'awiyah, yardar Allah ta tabbata a gare su gaba ɗaya, bisa bayanin da muka gabatar. Kuma wajibi ne a bai wa ko wane mai girma girmansa kamar yadda Allah Buwayayyen Sarki ya ce:* ***"Kuma waɗanda suka zo a bayan su suna cewa, ya Ubangijinmu! Ka yi gafara gare mu da kuma ga waɗanda suka riga mu yin imani, kuma kada ka sanya jin haushi a cikin zukatanmu ga waɗanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu! Haƙiƙa kai mai jinƙayi ne, mai tausayi"*** *Kuma ya ce:*

***"Waccan al'umma ce da ta shuɗe, abin da suka aikata nasu ne, wanda kuka aikata ku ma naku ne, kuma ba za a tambaye ku game da abin da suka kasance suna aikatawa ba".*** *Kuma Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam ya ce: "Idan aka ambaci Sahabbaina ku kame bakinku (daga shiga cikin lamarinsu)".*

*A wani lafazin cewa ya yi:*

*"Ku yi hattara da faɗin abin da ya gudana a tsakanin Sahabbaina, domin da ɗayanku ya yi sadakar kimanin dutsen Uhud na zinari ba zai kai mudun ɗayansu ko rabinsa ba".*[208]

[207] A larabce sunan littafin: *Al-Gunya li Ɗalibi Ɗariƙ Al-Haƙƙ*

[208] Duba littafinsa: *Al-Gunya li Ɗalibi Ɗariƙ Al-Haƙƙ,* na sayyidi Abdulƙadir Al-Jailani, bugun kamfanin Mustafa Al-Babi na ƙasar Masar, shafi na 79.

Sannan Shehin malamin ya ci gaba da kawo hadisai masu tarin yawa a kan darajojinsu. Ya Allah ka isar da rahamarka da jinƙayinka da kyautatawarka zuwa ga ƙabarin Sayyidi Abdulƙadir Al-Jailani, ka yi jagora ga mabiyansa zuwa ga hanyar gaskiya.

Daga cikin darajojin fiyayyen halitta akwai:

### 2.18 Ɗaukakar Al'ummarsa

Karara yake a cikin Alƙur'ani mai albarka cewa al'ummar Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ita ce mafificiya a cikin al'ummomi, wacce ta fi adalci da gaskiya, wacce kuma a kan haka ita ce zata yi sheda ga Annabawan Allah idan jama'arsu sun ƙaryata su bayan ita kuma ta samu sheda daga Annabinta na kasancewar ta al'umma adila, mai gaskiya.[209]

Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kasance mai tsananin tausayi da ƙauna da kyakkyawar kulawa ga al'ummarsa. Har ma wani lokaci yakan yi kuka saboda sha'anin da ya dame shi na wannan al'umma. Duk wani abin da yake wahalar da mu Annabinmu yana kauce ma sa. Allah da kansa ya ba da wannan sheda gare shi a cikin *Laƙad Ja'akum.*[210]

Ba ka lura salloli 50 aka fara faralta mana ba, sai shi ya riƙa nema ma na sauƙi sai da aka dawo da su salloli 5, kuma aka ce ladar sallah 50 ake riƙa ba mu?[211]

Sau da yawa yakan fasa yin ibada don gudun a wajabta ta a kan mu, yana tsoron ta wahalshe mu. Kamar a cikin watan azumi da ya fara sallar tarawihi sai mutane suka zo suka yi dafifi a bayansa, abin gwanin ban sha'awa.

[209] Suratul Baƙarah: 143, Suratu Ali Imran: 110 da Suratul Hajj: 78.
[210] Suratut Taubah: 128.
[211] Duba: *Sahih Muslim*, hadisi na 162.

A rana ta huɗu kawai sai aka ga bai fito ba. Saboda me? Ya ce, "Saboda na ji tsoron a wajabta ma ku wannan sallah ta zamo nauyi a gare ku".[212]

Haka kuma don irin wannan dalili ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi nadamar shigar da ya yi a cikin Ka'aba, kamar yadda ya faɗa ma Nana A'isha uwar mummunai, gudun al'ummarsa ta ɗora ma kanta shiga ciki wahala ta same ta.[213]

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sassafta umurninsa game da yin aswaki wanda ya so mu riƙa yin sa a lokacin kowa ce sallah, amma sai bai wajabta ma na ba don gudun wahala a gare mu.[214]

A game da sallar isha'i ma ya so ya sanya lokacinta a tsakiyar dare sai ya ji tsoron wannan ya kuntata ma al'ummarsa. Musamman saboda marasa lafiya da masu rauni.[215]

Yakan kuma nema mana sassauci a cikin ibada kuma ya yi addu'a *"Ya Allah! Ka matsanta ma duk wanda ya matsanta ma al'ummata".* A lokacin da Mu'azu ɗan Jabal ya tsawaita sallah har aka kawo ƙarar sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* fusata ya yi, ya yi ma sa faɗa mai tsanani yana cewa, *"Mu'azu kai mai fitinar mutane ne?"*.[216]

Duk wani ɓangare na al'ummar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da ya sifaita da rauni da gajiyawa zamu tarar Annabi ya ba shi kulawa. Shi ya sa ya yi umurni da dubiyar maras lafiya, da taimakon gajiyayye da halartar jana'iza da sauran su.[217]

Da farko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yakan ƙaurace ma jana'izar duk wanda ake bin sa bashi daga cikin musulmi. Amma saboda

---

212 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 924.
213 *Al-Jami'* na Imam Tirmidhi, hadisi na 873, kuma ya kyautata hadisin, ya inganta shi.
214 *Sahih Muslim*, hadisi na 252.
215 *Sahih Ibn Majah* na Albani, hadisi na 567.
216 *Sahih A-Bukhari*, hadisi na 705.
217 Duba *Manhaj Al-ƙur'an fi Ri'ayat Ad-Du'afa* na Imad Hafiz.

rahamarsa daga bisani sai ya shelanta cewa: *"Na fi muminai cancanta a kan kawunansu. Don haka, duk wanda ya cika daga cikin muminai kuma ana bin sa bashi, to, ni zan biya ma sa".*[218]

Wata alama ta rahama da ƙauna da Manzonmu yake yi mana ita ce, kwaɗayin da ya nuna na samun ladar layya ga dukkanin al'ummarsa. Don haka, a ranar babbar sallah sai ya zo da raguna biyu, ya yanka na farko ya ce, ya Allah! Wannan layyar Muhammadu ce da iyalansa. Ya yanka na biyu ya ce, ya Allah! Wannan kuma ta Muhammadu ce da duk wanda bai samu damar yin layya ba daga cikin al'ummarsa.[219]

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yakan nuna damuwa a kan abubuwan da Allah ya ƙaddara faruwarsu na fitinu da za a jarabci al'ummarsa da su. Yana yawan jan kunne a kan duk wata fitina da za ta bayyana a cikin al'ummarsa musamman kuma ƙarshen zamani. Yakan lurar da al'ummarsa irin matakan da ya kamata su ɗauka idan fitinun sun faru. Misali, a hadisin Irbad ɗan Sariya, lokacin da *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma su wasici cewa ya yi, *"Duk wanda ya yi tsawon rai a cikinku to, zai ga Saɓani mai yawa".* Yana nuni zuwa ga rabuwar kan al'umma ta hanyar bayyanar bidi'oi da ƙungiyoyi masu kawar da al'umma daga tafarkinsa. Don haka sai ya ba da mafita: *"Ina umurnin ku da bin Sunnata da Sunnar halifofina shiryayyu".* Saboda waɗannan halifofin nasa sun kwankwaɗi Sunnarsa kuma ba za su kauce ma ta ba ko da taki ɗaya. Sannan ya ce, *"Ku yi hattara da fararrin abubuwa. Domin duk abin da aka farar a cikin addini bidi'a ne, kuma dukkan bidi'a ɓata ce".*

Jinƙayin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ga al'umma bai tsaya a nan duniya ba. A lahira ma al'ummarsa za ta gamu da shi. Abdullahi ɗan Amr ya ruwaito hadisi cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya karanta faɗar Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* in da yake cewa: *"Ya*

---

[218] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 2398.

[219] *Sunan Abi Dawud*, hadisi na 2810 da *Al-Jami'* na Tirmidhi, hadisi na 1521. Al-Haithami ya nuna rashin gamsuwa da isnadin wannan hadisi. Majma' Az-Zawa'id 4/22.

*Ubangijina! Haƙiƙa waɗannan gumaka sun ɓatar da mutane da yawa. To, duk wanda ya bi ni yana tare da ni, wanda kuma ya saɓa ma ni kai mai gafara ne, mai jinkai".* Da kuma faɗar Annabi Isah *Alahis Salam*: *"Idan ka yi ma su azaba to, su bayinka ne. Idan kuma ka gafarta ma su to, kai Buwayayye ne, mai cikakkiyar gwaninta".* Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɗaga hannayensa yana cewa, "Ya Allah! Al'ummata! Al'ummata!" Sai ya rinƙa kuka. Maɗaukakin Sarki sai ya ce da Jibril *Alaihis Salam*, ka je wurin Muhammad - Ubangijinka shi ne ma fi sani - ka tambaye shi me yake yi wa kuka? Sai Jibril *Alaihis Salam* ya zo ya tambaye shi. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, sha'anin al'ummata ya dame ni. Jibril *Alaihis Salam* ya koma ya sanar da Ubangiji - Ubangiji kuwa shi ne ma fi sani. Sai ya ce ma sa, ka koma ka gaya ma Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam "Haƙiƙa, Mu, za mu yardar da kai game da al'ummarka. Ba za mu ɓata ranka ba".*[220]

Wannan alƙawari da Maɗaukakin Sarki ya yi ma Annabinsa babu shakka zai cika shi. Babbar hanyar da Allah zai cika ma sa wannan alƙawari kuwa ita ce ta hanyar ba shi ceto. Kuma tun a nan duniya Allah ya bai wa Manzonsa zaɓi tsakanin a shigar da rabin al'ummarsa aljanna ko kuma a ba shi damar yin ceto. Amma sai ya zaɓi na biyun don ya tabbatar zai fi zama rahama ga al'ummar tasa. Don haka, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, duk muminin da ba ya Shirka lalle ne cetona zai riske shi.[221]

A lokacin da kowa yake ta kansa a filin alƙiyama, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zai je ya surmuyar da kansa a gaban al'arshi yana sujada ga ubangijin girma da ɗaukaka, ya rinƙa ganawa da shi yana fadanci. Zai yabi Allah da wasu kalmomi da Allah ne zai yi ma sa ilhamar su. Sannan idan Allah ya ce ma sa *"Ya Muhammad! Ka ɗaga kanka. An yi ma ka izini ka nemi duk abin da kake so za a ba ka".* Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zai tashi ya yi godiya ga Allah yana mai cewa, "Ya Allah! Ni dai al'ummata! Ya Allah! Ni dai al'ummata!!." Za a ba shi dama ya yi ceto ga

220 *Sahih Muslim*, hadisi na 202. Duba kuma sharhin Imam Nawawi 3/79.
221 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 6305.

kowa daga cikin al'ummarsa sai wanda Alƙur'ani ya ɗaure, wanda ya zama wajibi ya tabbata a wuta".[222]

Kada mu manta cewa, tun a duniya Allah ya bai wa ko wane Annabi addu'a karɓaɓɓiya, sai Manzonmu ya ajiye tasa saboda mu a wannan rana. Kafin haka, duk Annabawa da manzannin Allah (Amincin Allah ya daɗa tabbata a gare su gaba ɗaya) sun amince ba wanda zai nemi ceton mutanen duniya, ya nemi Allah ya yi ma su hisabi sai Annabi Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam*.[223]

Kafin mu dakata da zancen darajojin fiyayyen halitta zai yi kyau mu faɗi wasu daga cikin darajojin da ake jingina ma sa bisa jahilci ko son zuciya, domin nasiha gare mu da tsarkake addinin Allah daga gurɓata. Bayan haka sai mu koma kan sha'anin rayuwarsa mai albarka. Allah ga mu gare ka.

### 2.19 Ɗarwaya, Shanya da Naɗewa:

### Har Yanzu Dai a Kan Maganar Darajojinsa

Akwai wasu abubuwan da aka ƙago na darajoji aka jingina ma fiyayyen halitta amma ba su da tushe daga littafin Allah da ingantacciyar Sunna. Kai, wasu ma ƙarara sun saɓa Alƙur'ani ko kuma Sunna ingantacciya. To, ka ga duk da waɗannan ɗinbin darajoji da Maɗaukakin Sarki ya keɓanci Manzonmu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da su waɗanda kuma muka fayyace su a baya, wasu masu curuta a zukatansu sai da suka ƙago wasu darajoji na daban suka jingina ma sa. Kamar suna ganin duk waɗannan darajojin ba su ishe shi ba, ko kuma ba su kammala matsayinsa yadda ya dace ba. Suka ƙirƙiro hadisai na ƙarya suka jingina ma sa, wai, don kai matuƙa ga bayyana darajarsa. Wannan ya yi mummunan tasiri wajen gurɓata akidun musulmi musamman in muka yi

[222] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 4476.

[223] Duba karin bayani a cikin *Fath Al-Bari* na Ibn Hajar 12/374-375 da Sharhin Nawawi a kan *Sahih Muslim* 3/75.

la'akari da jahilci da ya dabaibaye jama'a ya kasance ba a iya rarrabe gaskiya da karya daga cikin abin da ake ruwaitowa. Ga wasu daga cikin darajojin ƙarya da aka jingina ma sa:

1. Cewa, shi ne farkon halitta. Ko kuma an halicce shi ne tun kafin halittar al'arshi.

2. Cewa, Allah ya yi duniya domin sa. Ko kuma domin sa ne aka halitta kowa.

3. Cewa ba domin sa ba da Allah bai halicci Annabi Adam ba.

4. Cewa, an halicce shi daga hasken Allah, sannan aka halicci sauran halittu daga cikin haskensa.

5. Cewa, ya kasance haske ne a gaban Allah kafin a halicci Annabi Adam da shekaru dubu goma sha huɗu.

6. Cewa, shi ba mutum ba ne.

7. Cewa, Annabi Adam ya ga sunansa rubuce a al'arshi har ya yi tawassuli da shi wajen neman yafe laifinsa.

8. Cewa, an aiko shi zuwa ga Annabawan da suka gabata da jama'arsu.

9. Cewa, duk Annabawa sun yi tawassuli da shi don neman biyan buƙatunsu daga wurin Allah.

10. Cewa, ya san gaibi kai tsaye, bayan kuwa Maɗaukakin Sarki ya kore ma sa sanin gaibi a wurare da dama cikin Alƙur'ani. Kuma duk rayuwarsa tana nuna cewa, bai san gaibi ba sai abin da Allah ya ga dama ya sanar da shi kamar yadda muka kawo a wajen maganar Mu'ujizoji.[224]

A dalilin wannan wuce gona da iri, Allah kaɗai ne ya san irin sakin layin da aka yi wanda wani lokaci yakan kai har ga Shirka da sanya Manzon

[224] Alal misali, in da fiyayyen halitta ya san gaibi kowane iri ya za ayi ya rasa gano ƙazafin da aka yi ma iyalinsa har sai bayan kwana arba'in da Allah ya so ya sanar da shi?

Allah a wurin da Allah ne da kansa ya cancanta kamar yin rantsuwa da shi ko ɗaukar alwashi (yin bakance/garawa) a wurin sa ko neman agaji daga wurinsa ko kiran sa a lokacin sabkar musiba ko roƙon sa biyan buƙata idan an je wurin ƙabarinsa. Waɗannan kuwa duk sun saɓa ma karantarwarsa da ta zo daga Alƙur'ani da Sunna. Kamar yadda suka saɓa ma tarbiyyar Sahabbansa. Bisa haƙiƙani ma dai, masu wannan azarɓaɓi suna ƙara gishiri a kan matsayin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* na gaskiya ne kawai don biyan wasu bukatunsu ba domin sa ba. Kuma daga ƙarshe wasu ne ke cin moriyar wannan wuce gona da iri. Waɗanda suka fi kowa faɗawa a wannan tarkon na Sheɗan su ne mawaƙan yabo waɗanda ba su san littafin Allah da Sunnar Ma'aiki ba. Kuma sun ɗauka in dai za ka yabi Manzon Allah, to duk abin da ka faɗi ba zaka yi laifi ba. Da ɗai kuwa, abu biyu ne suke halaka bil adama cikin sha'anin addini; kasawa ko zurfafawa da sa-ni-in-fi-ka.

Akwai wani kyakkyawan littafi a wannan fanni da ya kamata mu yi nuni zuwa gare shi, shi ne, *Khasa'is Al-Musɗafa Sallallahu Alaihi wa Sallam Bain Al-Guluwwi wa Al-Jafa'*[225] A cikinsa an kawo *Khasa'is* na Ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ingantattu kuma an ware babi na musamman a kan irin waɗannan da muka kawo waɗanda ba su inganta ba, an yi fashin baƙi na ilmi sosai a kan su. Kuma an faɗaɗa magana a kan waƙoƙin yabo da yadda suke wuce makaɗi da rawa saboda jahiltar su ga addini da kuma wasu dalilai na daban.

Yanzu kam sai mu koma bisa babban godaben tarihin da muka ɗauko daga zancen aiko fiyayyen halitta har iya in da Maɗaukakin Sarki zai ba mu iko. Gare shi ne muke neman taimako.

[225] Littafin wallafar wani shehin malami ne As-Sadiƙu ɗan Muhammad. Asalinsa kundin neman digiri na biyu ne da ya rubuta a ƙarƙashin kulawar Farfesa Sheikh Ali Abdurrahman Al-Hudhaifi babban limamin masallacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam*. Ya gabatar da shi ga jami'ar musulunci ta Madina a shekarar 1415H.

# FASALI NA UKU

## 3.0 Tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* Daga Farkon Annabta Zuwa Hijira

### 3.1 Gari ya Waye

Kafin cikar shekarun Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* arba'in halin da duniya take ciki ya ƙara rikicewa. Jahilci ya yi kanta a cikin mutane domin sun dimauta daga bin mahaliccinsu. Amma shi kam ya kasance mafi tsarkin mutane, kuma mafi nisantar su daga aikin assha. Bai taba halartar wani buki na addinin gumaka ba. Bai taba sha'awar giya ba balle ya kurba ta. Haka kuma bai taba shiga caca ba duk da kasancewar mutane a lokacin ba su ganin illar ta. A daidai wannan lokacin ne ya rinƙa yin mafarki, idan aka tashi da safe sai abin da ya gani a cikin mafarki ya faru kamar an kifa kwarya a kan 'yar uwarta. Daga bisani sai aka sanya ma sa sha'awar keɓanta da nisantar jama'a saboda tunaninsa da nasu ya banbanta. Ra'ayinsu ya yi hannun riga. Al'adunsu na jahiliyya kuma sam ba su burge shi. Saboda haka sai ya zaɓi wani wuri nesa da mutane, can a kan hanyar garin Ɗa'if, a kan wani dutse mai suna *Jabal An-Nur*. Ya samu wani kogo ana ce da shi *Hira* ya raɓa cikin sa yana bautar ubangiji mahalicci bisa iya abin da ya sani a wancan lokaci daga *Hanifiyya*; addinin Annabi Ibrahim *Alaihis Salam*. Wani abin da ya rinƙa ba shi mamaki a wannan lokaci shi ne, jin gaisuwar girma ta musamman wacce bai saba da irin ta ba daga wani dutse da yake shudewa kusa da shi.[226]

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kan yi wannan khalwa ne a cikin ko wane watan Ramadhan shekaru uku a jere kafin samun Annabtar sa. Idan ya samu wasu 'yan kwanaki guzurinsa ya kare sai ya dawo gida ya sake shirin komawa. A shekarar sa ta uku ne, sa'ad da yake kusan cika shekaru

[226] *Sahih Muslim*, littafin Fadha'il, babin falalar nasabar Manzon Allah da gaisuwar dutse gare shi. Da kuma *As Sirah An-Nabawiyyah,* na Ibn Hisham 1/234-235.

arba'in a duniya yana cikin wannan kogo sai baƙon arziki, wato (Jibril *Alaihis Salam*) ya same shi da saƙon Allah duk da yake a lokacin bai san abin da saƙon yake nufi ba. Mu bari Nana Aisha -uwar muminai- ta ci gaba da ba mu wannan labari..

### 3.2 Nana Aisha ta Sifaita Yadda Wahayi ya Fara Zuwa

"... Kwatsam! Yana a cikin kogon Hira sai Mala'ika Jibrilu *Alaihis Salam* ya ɓullo ma sa, ya ce ma sa: "Yi karatu". Sai ya amsa ma sa da cewa, "Ni ban iya karatu ba". Faɗar haka da ya yi sai Jibrilu *Alaihis Salam* ya kama shi ya matse shi da ƙarfi sai da ya sha wahala sosai sannan ya sake shi yana cewa: "Yi karatu". Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya sake maimaita amsarsa "Ni ban iya karatu ba". Jibrilu kuwa sai ya sake damƙar sa kamar yadda ya yi da farko. Sai da suka yi haka har sau uku sannan ya karanta ma sa ayoyin farko na Suratul Alaƙ".[227]

Wannan lamari ya faru a talatainin daren litinin 21 ga watan Ramadhan shekara ta 40 daga yaƙin Giwaye, wanda ya yi daidai da 6 ga watan Agustan shekara ta 610 Miladiyya.[228] Lamarin ya tada hankalin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* matuƙa. Bai wayi gari ba sai a wurin iyalinsa, jikinsa yana ɓari yana cewa, ku lullube ni. Da Nana Khadija ta ga haka sai ta bi duk hanyar da za ta iya don ta kwantar da hankalinsa, sannan ta tambaye shi labarin abin da ya faru. Ya kwashe duka ya faɗa ma ta. Sannan ya ce, haƙiƙa na ji tsoro a kan kaina. Yana nufin ya ji tsoron ko na-ɓoye ne suka shafe shi. Sai ta kada baki ta ce ma sa, ina! Ba zai taɓa yiwuwa Allah ya tozarta ka ba. Kai ne fa mai sada zumunta, mai ɗaukar nauyin gajiyayye, mai tufata huntu,

---

227 *Sahih Al-Bukhari*, farkon littafin yadda aka fara wahayi, shafi na 2.

228 Duba: *As-Sira An-Nabawiyya*,na Nadwi, shafi na 102 da kuma *Ar- Rahiƙ Al- Makhtum,* na Mubarakfuri, shafi na 80.

mai karbar baƙi, mai kuma taimakon wanda ya kasa. Ina zai yiwu aljani ya shafe ka?![229]

Daga nan sai ta yanke shawarar zuwa da shi don neman fatawa da taimako wurin wani fitaccen malamin addini da ya karanta Linjila kuma ya iya yaren Ibraniyyanci wanda aka saukar da Linjila da shi. Ga shi kuma ɗan uwanta ne na jini, ana ce da shi Waraƙatu ɗan Naufal. Da suka je suka same shi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kwashe duk labarin ya gaya ma sa. Da Waraƙatu ya ji wannan labari sai ya yi rantsuwa cewa, Jibrilu ne ya zo da manzanci zuwa gare shi. Ya ƙara da cewa, zan yi fatar Allah ya tsawaita rayuwata domin in taimake ka duk ranar da za a kore ka daga garinku. "Kora ta?!. Haka kawai za a kore ni?" Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tambaye shi. Waraƙatu ya ce, ƙwarai kuwa. Ai wannan saƙon da ka zo da shi ba wanda ya taɓa zuwa da shi ba a cuta mai ba.[230]

Wannan fata da Waraƙatu ya yi ta taimakon Manzon Allah ta tabbatar da kasancewar sa shi ne mumini na farko a cikin wannan al'umma. To, sai dai Allah bai tabbatar ma sa da fatar ba. Domin ba a daɗe da yin haka ba Allah ya karɓi ransa. Daman dai ya riga ya tsufa har ya makance. Amma ko ba a faɗa ba mun san shi musulmi ne. Kai, shi ne ma musulmin farko wanda ya bayyana imaninsa ga ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Kuma Manzon Allah ya tabbatar da ganin sa a cikin fararen kaya cikin aljanna.[231]

Daga cikin darussan wannan karatu mun gane cewa, hanyar Allah ba sumul take da kwalta ba. Hanya ce mai wahala da ake jarabtar masu bin ta, ballantana kuma jagorori a cikin ta. Duk yadda ka gane gaskiya ka rungume ta wani zai yi maka kallon karkatacce wanda ya cancanta a yaƙe shi. Waraƙatu ya yi hasashen irin jan aikin da ke gaban Manzon Allah ne duba ga irin tirjewar da magabatansa suka gamu da ita daga mutanensu tun daga Annabi

[229] *Sahih Al-Bukhari*, farkon littafin yadda aka fara wahayi, shafi na 2.
[230] Duba: *Sahih Al-Bukhari*, a wurin da muka faɗa a sama.
[231] *Al-Mustadrik* na Hakim (2/666) da kuma *Zad Al-Ma'ad* na Ibn AlKayyim (3/21).

Nuhu zuwa su Hudu da Salihu da Shu'aibu da lut da Musa da Isa da sauran jekadun ubangiji, amincin Allah ya daɗa tabbata a gare su baki ɗaya.

### 3.3 Wahayi ya Tsinke, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Shiga Damuwa

Tun daga wancan lokacin da muka faɗa a baya Jibrilu *Alaihis Salam* sai ya ɗaga ƙafa bai sake ziyartar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba. Har sai da Manzo ya fara shauƙin dawowar wannan baƙon arziki. Sai bayan da watan Ramadhan ya shuɗe ne sannan Jibrilu *Alaihis Salam* ya sake zuwa da Suratul Muddassir wadda a cikin ta Allah ya ke ba Manzonsa umurnin ya tashi ya fara wa'azi. Zama ya ƙare kenan, babu sauran hutawa. Zai shiga gwagwarmayar kira zuwa ga gaskiya da tabbatar da ita, aikin da ba zai ƙare ba sai ran da rayuwarsa ta ƙare. Manzon Allah kuwa bai yi ƙasa a guiwa ba, ya tashi tsaye haiƙan wajen kira zuwa ga Musulunci. Amma fa sai da ya natsu ya karanci halayyar mutanensa. Domin kuwa yana sane da cewa, akwai masu sauƙin kai da saurin fahimta da janyuwa zuwa ga gaskiya, akwai matsakaita. Sannan akwai masu taurin kai kamar daga ƙashi aka halicci zukatansu. Don haka, sai ya shirya tsarinsa na kira a sirrance da bin ɗaiɗaikun mutane waɗanda ya tabbatar za su iya haɗa sahun farko na muminai.

### 3.4 Harsashin Musulunci

Ba sai mun faɗa ba, Nana Khadija tayi amanna da abin da mai gidanta ya zo da shi. Haka ma 'ya'yanta. A daidai wannan lokacin dai sun haifi 'ya'ya biyar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, su ne: Al-Kasim da Abdullahi da Zainab da Rukayya da Ummu Kulthum. Biyu na farkon sun cika suna ƙanana.[232] Muna iya cewa kenan, Khadija da 'ya'yanta uku; Zainab da

[232] Ba a haifi sayyida Fatima ba a daidai wannan lokaci. An haife ta ne bayan bayyanar musulunci a ranar 20 ga Jimadal Akhira, shekara ta biyar bayan manzanci. Haka shi ma

Ruƙayya da Ummu Kulthum sun musulunta daga cikin gidan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[233] Sai kuma wasu yara ƙanana da suka yi gaggawar karɓa kira daga cikin wannan babban gida. Su ne:

1. Ali dan Abu Ɗalib wanda yake da shekaru takwas a daidai wannan lokaci. Sayyidi Ali dai ya tashi a wannan tsarkakakken gida bayan da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya karɓo shi daga mahaifinsa Abu Ɗalib yana kula da shi domin ya taimaka ma sa kamar yadda shi ma ya kyautata ma sa sadda yana ƙarami.

2. Sai kuma Zaidu ɗan Haritha wanda yake ɗan asalin ƙabilar Ɗayyi' ta ƙasar Yaman. Mahafiyarsa ta mutu tun a zamanin Jahiliyya, ta bar shi yana yaro tare da 'yan uwansa Jibilatu da Asma'u. Daga baya wasu mayaƙa 'yan ƙabilar Fizarata suka kai hari a ƙauyensu kuma suka ribace shi a matsayin fursunan yaƙi. Yana cikin ƙangin bautar ne ya faɗa a hannun Nana Khadija wadda ita kuma ta ba da kyautar sa ga maigidanta *Sallallahu Alaihi wa Sallam.* Daga bisani mahaifinsa ya zo domin ya fanshe shi daga wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* tare da baffansa da Jibilatu; ɗan uwansa. Saboda girmama Manzon Allah Zaidu ya kasa tashi ya gaishe su har sai da ya samu izinin Manzon Allah. Da suka nemi Manzon Allah fansarsa sai suka ce ya faɗi duk abin da yake so su ba shi don su fanshi Zaidu. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai ya gitta ma su Musulunci ya ce, idan sun musulunta za su karɓi ɗan uwansu amma suka ƙi. Sai ya ce da su to, ya ba Zaidu zaɓi idan yana so ya bi su an sallame shi. Amma saboda kyakkyawar mu'amalar da Manzon Allah yake yi ma sa da yadda yake jin daɗin zama wurinsa sai ya ce faufau shi ba zai iya rabuwa da wannan gida mai albarka ba. Don haka sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ‘yanta shi har ma ya jingina shi

Ibrahim a Madina aka haife shi a cikin watan Dhul Hajji na shekara ta takwas bayan Hijra kuma ba ita Nana Khadija ce ta haife shi ba, Mariya ce; kuyangar Manzon Allah, 'yar ƙasar Masar ta haife shi.

[233] Nana Fatima ba ta zo duniya ba a wannan lokacin da muke magana a kai. Su kuma Al-Kasim da Abdallah an haife su amma suna cikin ƙuruciya.

ga kan sa aka rinƙa ce ma sa Zaidu ɗan Muhammad.[234] Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da aya ta 36-40 a Suratul Ahzab domin ya rusa waccan al'ada ta mai-da-ɗan-wani-naka da larabawa suke yi. Don haka aka kira shi da sunansa na haƙiƙani Zaidu ɗan Haritha. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kasance yana son sa matuƙa. Ya naɗa shi ɗaya daga cikin kwamandoji uku a yaƙin Mu'utah inda can ne ya samu shahada kamar yadda zamu gani a nan gaba.

Fara karɓar kiran Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* daga cikin gidansa shi ne babbar nasarar da ya samu wadda ta sawwaƙe ma sa ci gaba da isar da saƙon Allah a cikin natsuwa da kwanciyar hankali. Dole ne mai da'awa ya fara daga gidansa in yana son samun nasara a sauran duniya ta waje.

## 3.5 Ayarin Farko

### 3.5.1. Musuluntar Sayyidi Abubakar Siddiƙu

Bayan da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya isar da saƙon Allah ga iyalinsa, mutum na farko da ya tuntuɓa shi ne amintaccensa kuma na hannun damansa Abubakar. Abubakar ya san aminin nasa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* fai da ɓoye. Domin kuwa fara ɗaya suke rabawa tun a zamanin ƙuruciya. Bai taɓa sanin sa da harkar wasa ba ko a wancan lokaci ballantana yanzu da ya tsufa ayi tuhumar ya shara ma Allah ƙarya. Saboda haka da jin cewa Allah ya aiko shi, Abubakar bai yi jinkiri ba ya amsa kiransa, kamar yadda Manzon Allah da kansa ya bayyana.[235]

Babu shakka cewa, musuluntar Abubakar ta faranta ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* rai matuƙa kasancewar sa dattijo ne mai kwarjini da muhibba wanda jama'a suke ƙimantawa kuma suke ƙauna. Ga shi duk a cikin Kuraishawa ba wanda ya kai shi zama malami. Domin ba wani ilmi a

---

234 *Al-Mustadrik Ala As-Sahihain* na Hakim 3/214.

235 Duba: hadisin Abud-Darda'i a *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3461

wurin su - kafin bayyanar Musulunci - wanda ya wuce tarihi, musamman na "Ansab" sanin dangantakar larabawa da gidajensu da kuma tarihin kakanninsu da yaƙoƙansu da sanin halin girma ko na tsiya da suka aikata. A cikin su kuwa babu wanda ya kai Abubakar sanin waɗannan tarihohi da muka ambata. Ban da haka kuma shi ɗan kasuwa ne mai wadataccen jari, mai sakin hannu sosai. Kuma an shede shi da kamun kai matuƙa. Yana cikin 'yan ƙalilan mutanen da ba su taɓa shan giya ba. Ko ba a faɗa ba kai ma ka san mai irin wannan hali shi ke iya zama abokin Manzon Allah tun a ƙuruciya.

2. Musuluntar Abubakar ke da wuya sai ya fara kiran muƙarrabansa da wasu abokanen huldarsa da ya amince da hankalinsu da kyakkyawar fahimtarsu. Take sai suka karɓa ma sa suka musulunta. Waɗannan sun haɗa da: Sayyidi Usmanu ɗan Affana, wanda yake dattijo ne ɗan shekaru 34, da Abdurrahman ɗan Aufu, mai shekaru 30, da Sa'adu ɗan Abu Waƙƙas mai shekaru 17, da Dalhatu ɗan Ubaidullahi mai shekaru 13 da kuma Zubairu ɗan Awwam mai shekaru 12.

Waɗannan su ne ayarin farko da suka gaskata Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a asirce ko iyalansu a daidai wannan lokaci ba su sanar ma ba domin an ce mai haƙo ba ya ɗaga hannu.[236]

### 3.6 Ayari na Biyu

A hankali ayarin farko suka ci gaba da janyo mutane asirce suna kawo su wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana yi masu sharhin da'awarsa suna ba da gaskiya da shi. Babu kamar Abubakar a wannan fage, kasancewar sa babban mutum mai matsayi wanda jama'a ke taruwa a gidansa kuma wanda ya yi imani mai ƙarfi da wannan sabon kira da ya bayyana a hannun amintaccensa wanda ba ya da shakku a kan sa. A daidai wannan lokacin ne Sayyidi Bilal ya musulunta. Sai kuma Abu Ubaida ɗan Al-Jarrah

[236] Duba: *As-Sirah An-Nabawiyyah* na Sallabi, shafi na 90.

daga gidan Harith ɗan Fihru da Abu Salamata ɗan Abdul Asad[237] da Arƙamu ɗan Abul Arƙam - su biyun daga gidan Makhzum - da Usmanu ɗan Maz'un[238] da ƙannensa biyu; Kudamatu da Abdullahi. Da Abidatu ɗan Harith ɗan Muɗɗalib da matarsa Fatima ‘yar Khaɗɗab (ƙanwar Sayyidi Umar). Da Khabbabu ɗan Arat. A haka dai sai da suka kai mutane 40 daga gidaje daban daban. Daga nan kuma Musulunci ya zamo shi ne labarin da ake taɗi a kan sa duk inda aka zauna a garin Makka.[239]

Amma fa yana da matuƙar wuya manazarcin tarihi ya iya tantance jerin musuluntar jama'a a wancan lokaci. Dalili kuwa shi ne, duk wanda ya musulunta a wancan hali da ake ciki ba lalle ne ya san sauran waɗanda suka musulunta ba kai tsaye. Iyakar hulɗarsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ne da mutum ɗaya ko biyu, domin ba maslaha ba ne a bayyana ma sa sunayen sauran jama'a da ake tare da su. Wannan zai fassara maka saɓanin da aka samu wajen jerin sunayensu, kodayake duk an haɗu a kan cewa, su ne *"As-Sabiƙun Al-Awwalun"*.

Sa'adu ɗan Abu Waƙƙas yana cewa, ni ne na uku a musulunta kuma a ranar da na musulunta ba wanda ya sake musulunta har sai da aka yi sati ɗaya[240]. Abdullahi ɗan Mas'ud *Radhiyallahu Anhu* shi kuma cewa ya yi, ni ne na shida a shiga Musulunci.[241] Ammar ɗan Yasir ya ce, na musulunta ne a lokacin da ba kowa tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai wasu bayi guda biyar (yana nufin Bilal, da Zaid, da Amir ɗan Fuhairata - bawan Abubakar - da Yasir da ɗansa Ammar) da mata biyu da Abubakar.[242] Abdullahi ɗan mas'ud yana cewa, mutum bakwai ne aka fara sanin

---

237 Ɗan gwaggon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam*; Barratu 'yar Abdulmuttalib kuma abokin shan nononsa.

238 Shi ma abokin shan nono ne ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam*

239 *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Hishamu 1/245-262.

240 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3737

241 *Al-Mustadrik* na Hakim (3/313).

242 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3660.

Musuluncinsu; Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Abubakar da Ammar da Sumayya matarsa da Suhaibu da Bilal da Miƙdad.[243]

Ala kulli halin, waɗannan bayin Allah sun rungumi addinin Musulunci da wuri, kuma sukan haɗu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a wasu lokuta don samun ƙarin haske da sauraron karatun Alƙur'ani. Sukan kuma yi sallah sau ɗaya ko sau biyu amma fa asirce ta yadda sai an fita bayan gari a tsakanin duwatsu in da ko tsuntsu bai iya samun labari. Jibril *Alaihis Salam* ya zo da kansa ya koya ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* tsarki da alwala da sallah. Kuma ya sanar da shi lokutanta[244]

Da farko duk da yaɗuwar labarin Musulunci a cikin garin Makka ba wata tsangwama da musulmi suka gamu da ita saboda ba a tuhumar su da zagin gumaka ko sukar addinin iyaye da kakanni. Amma daga bisani sai labarin ya canja kamar yadda zamu gani a nan gaba.

### 3.7 Makarantar Farko: Dar Al-Arƙam

Wata rana bisa ƙaddarar Allah wani gungu na Sahabbai sun shiga cikin sunƙurmin jeji a tsakanin duwatsu suna ibadarsu, sai kawai wasu mushrikai suka yi kiciɓis da su. Suka kuwa shiga zargin su a kan wannan ibada da suke yi suna sa-in-sa har ɗaya daga cikin musulmi; Sa'adu ɗan Abu Waƙƙas ya fusata ya sa igiyar raƙumi ya make wani daga cikin su har jini ya kwarara daga jikinsa. Wannan lamarin ya sa musulmi suka ji tsoro a kan ci gaba da buya a irin waɗannan wurare, yiwuwar a kai ma su hari bagatatan ba su shirya ba. A nan ne suka fara tunanin wani amintaccen wurin haɗuwa saboda kauce ma irin wannan tsotsayi. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Sahabbansa

243 *Subul Al-Huda Wa Ar-Rashad fi Sirati khairil Ibad,* na Salihi, 2/306.

244 *Mukhtasar Sirat Ar-Rasul* na Abdullahi An-Najdee, shafi na 88. Duba kuma *Al-Muwaɗɗa*, na Imam Malik, hadisi na ɗaya.

sai suka yanke shawarar su rinƙa haɗuwa a gidan wani saurayi da ake ce da shi Al-Arƙam ɗan Abul Arƙam.[245]

Shi dai Arƙam matashi ne ɗan shekaru 16 wanda ya musulunta a asirce. Kuma ya fito daga gidan abokan gabar Banu Hashim; su ne Banu Makhzum, waɗanda ke ƙarƙashin jagorancin Abu Jahali ɗan Hishamu. Da haka aka kawar da hankalin mushrikai domin suna neman wuta ne a maƙera, amma tana can a masaƙa ana hura ta ba su sani ba har sai da Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya cika haskensa kamar yadda ya yi alƙawari.

A cikin wannan makarantar ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya rinƙa haɗuwa da Sahabbansa, suna sauraron wahayin da Maɗaukakin Sarki yake aiko ma su - ta hanyarsa - dare da rana. Kuma sukan shiga ne da ɗai-ɗaya, a lokacin ɗaukewar ƙafafun jama'a. Shi ya sa da ɗai rana babu wani mushriki da ya taɓa gano muhallin da wannan makaranta take ballantana a shirya farmaki don ganin baya gare ta.[246]

A cikin wannan makarantar ne Sahabbai suka samu isasshiyar tarbiyya a kan imani wanda ya ratsa zukatansu matuƙa. Suka cika da son Allah da Manzonsa. Babu abin da yake faranta ransu sai sauraren littafin Allah daga bakin Manzonsa. A nan ne aka sanar da su sunayen Allah da siffofinsa, da arzikin aljanna da azabar wuta . Aka koyar da su sanin ƙaddara da yadda Allah yake hukunta al'amurra, suka sakankance ba abin da zai same su a rayuwa sai bisa ga izinin Allah. Tarihin Annabi Adam da arangamarsa da Shaiɗan tun karon farko na cikin darussan wannan makaranta. Haka kuma Sahabbai sun samu horarwa a cikin wannan makaranta a kan tsayar da ibada da tsarkake zuciya domin Allah. Suka karanci asirran Fatiha wacce da ita musulmi yake ganawa da mahaliccinsa kullum safiya. A nan ne aka wanke tunaninsu tsaf daga duk wata dauɗar Jahiliyya da nau'oin tunanen da suke da su gurɓatattu

---

245 *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Hishamu 1/236.
246 *Al-Manhaj Al-Haraki li As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Munir Gadhban 1/49.

game da rayuwa ta yau da ta gobe. A nan ne kuma suka koyi halayen kirki kamar haƙuri da taimako da tausayi da sadaukantaka da barin son zuciya.

Alƙur'ani ya yi amfani da wani irin yare mai ƙarfin tasiri da jan zukata a cikin lafuzza gajeru ba masu gajiyarwa wajen karatu ba. Abin da duk ya shige ma su duhu a wannan lokaci Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kan warware ma su shi. Da haka, aka gina wata al'umma a sirrance wacce ta ƙalubalanci kafurcin mutanen Makka kafin daga bisani Maɗaukakin Sarki ya ba da umurnin a fito fili da da'awar Musulunci.[247]

## 3.7 Da'awar Musulunci ta Fara Fitowa Fili

Shekaru uku kenan cif aka yi ana sirranta da'awar Musulunci tare da kiran ɗaiɗaiku waɗanda ake ganin dacewar su da shiga Musulunci a irin wannan lokaci mai tsanani. Kuma sama da mutane 40 ne suka samu horarwa ta musamman daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* waɗanda suka haɗa da iyalansa da mafi kusancin mutane zuwa gare shi. Sai kuma waɗanda Allah ya zaɓe su don shiga cikin wannan ayari mai albarka daga cikin waɗanda su waɗannan bayin Allan makusantan Manzon Allah suka janyo. Sun kasance cikin wani yanayi na baƙunta a cikin mutanensu, kasancewar su a kan wani addini da wata aƙida da take baƙuwa a cikin al'ummarsu. Amma kuma sun yi riƙo ƙam-ƙam da addininsu, suna ji da shi matuƙa, kuma a dare da rana tunaninsu shi ne ta wace hanya ne za su nusar da mutanensu a kan gaskiya?[248]

Waɗannan bayin Allah da suka samu horaswa a wannan lokaci sun kasance daga gidaje daban daban, mafi yawansu kuma manyan mutane ne da matasa 'yan gata da 'ya'yan masu iko. Akwai kuma wasu masu rauni waɗanda ke cikin ƙangin bauta ko kuma cikin halin ƙuruciya kamar su 13. Su ne kuma

---

[247] *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Sallabi, 94-95.
[248] *Al-Guraba' Al-Awwalun,* na Salman Al-Auda, shafi na 133.

suka zama tubalin Musulunci na farko wanda aka gina fadarsa a kan su. Su ne masu zurfin ilmi a cikin Sahabbai, masu bayar da fatawa, masu yanke hukunci. Kuma duk wata arangama da ɗauki-ba-daɗi da aka yi a bayan haka su ne suka zamo a sahun gaba.[249] Bayan wannan lokacin ne Allah ya sauko da umurninsa zuwa ga Manzonsa *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana cewa:

> *"Ka yi gargaɗi ga danginka mafiya kusanci"* Yana nufin ƙabilun Kuraishawa da suke a Makka.[250]

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* take ya yanke shawarar matakin da zai ɗauka. Ya nemi kafar sadarwa mafi ƙarfi ta wancan zamani da salo mafi kaifi wajen isar da saƙo zuwa ga mutane. Sai ya hau kan dutsen Safa yana cewa, "Ya Sabahah! Ya Sabahah!!" Irin kiran da masu shelar yaƙi suke yi don yekuwa da gargaɗi. Kafin ka ce me ye wannan, duk cikar Makka da batsewarta sun haɗu a gabansa don jin abin da yake yekuwa a kan sa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai ya yi shimfiɗa mai ƙarfi wadda ta zarge su, ta hujjace su. *"Idan na ce maku a nan saman dutsen nan ina hangen ƙurar wata runduna da za ta kawo hari zaku gaskata ni?"* Manzon Allah ya tambaye su. Suka ce, ƙwarai kuwa. Ai kai ba maƙaryaci ba ne. Ba mu taɓa sanin an zarge ka da ƙarya ba. Sai ya ce: "To, ni mai gargaɗi ne daga Allah don ku bi shiriyarsa, ku kama godaben gaskiya kafin wata azaba mai tsanani - in kun ƙiya - ta cim ma ku". A nan ne fa suka yi cirko-cirko, suna kallon juna. Ba wanda ya iya buɗa baki ya ce uffan, sai mafi ƙarancin arzikin wannan al'umma shi ne Abu Lahabi. Shi ne ya furta mummunar magana ga ma'aiki, yana mai cewa, "Tir da halinka ya Muhammad! Yanzu a kan wannan ne kake kiran mu?!" Daga nan kuma taro ya watse. Wannan haɗuwa ta zamo ita ce ajandar tattaunawar jama'a na cikin gida da ƙasashen waje a tsawon wannan shekarar. Kuma a kan abin da ya faru a wannan wurin ne Maɗaukakin Sarki ya saukar da Suratul Masad wadda ya fallasa Abu Lahabi a cikin ta gami da

---

249 *Rasulullahi Fi Makka,* na Al-Yahya, shafi na 111-112 da kuma *As-Sirah An-Nabawiyyah* na Sallabi, shafi na 102-103.

250 Suratus Shu'ara': 214.

mugunyar matarsa. Kuma Allah ya kama sunansa ɓaro-ɓaro a cikin wannan sura domin ya tozarta shi kamar yadda ya tozarta fiyayyen halitta.[251]

Abu Lahabi dai mutum ne da Allah ya tara ma sa ni'imomi da dama. Domin kuwa kamilin mutum ne, kyakkyawa, mai girman matsayi da wadatar arziki. Ga shi kuma baffan ma'aikin Allah. Amma kash! Duk waɗannan abubuwan ba su amfane shi ba, shi da muguwar matarsa Ummu Jamil. Maganar Allah ta tabbata a kan su suka mutu tozartacci, suna makamashin Jahannama. A cikin 'ya'yansu huɗu Utbah da Mut'ib da Durratu duk Allah ya yi masu arzikin musulunta. Sai Utaiba ne ya mutu kafiri. Dalili kuwa, lokacin da mahaifin nasu ya umurce su da sakin auren 'ya'yan Manzon Allah mata da aka ɗaura ma su sai Utbatu ya saki Rukayya a mutunce. Shi kuma wannan shaƙiyyin sai da ya zo ya tozarta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sannan ya zartar da muradin mahaifinsa; ya shelanta sakin Ummu-Kulthum. Ashe daman Allah ya yi ma su zaɓin wani nagartaccen bawa nasa shi ne Usmanu ɗan Affan wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɗaura ma sa auren su ɗaya bayan ɗaya. Sannan Allah ya yi ma Utbah tukuicin cikawa da imani shi da ƙannensa biyu; Mut'ib da Durratu. Utaiba kuma Allah ya tozarta shi ya yi mutuwar ƙasƙanci a kan kafirci.

Ya Allah muna roƙon ka ka yi mana arzikin gamawa lafiya da mutuwa cikin masoyan Manzonka masu kariya ga addininsa da tafarkin shiriyarsa.

### 3.8 An Fara Kai Ruwa Rana Tsakanin Musulunci da Kafirci

Fara bayyana da'awar Musulunci ke da wuya sai duk inda hankalin shugabannin Kuraishawa yake ya tashi, suka kalli Musulunci a matsayin wani gungu na 'yan tawaye da ya zo ya tarwatsa tarayyar ƙasarsu, ya wautar da hankalinsu da na iyayensu, a yayin da zukata masu tsarki daga cikin jama'a suka riƙa shiga ɗaya ɗaya a cikin addinin. Da lokacin aikin Hajji ya gabato sai suka ji tsoron Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya samu damar

251 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 4971 da *Sahih Muslim*, hadisi na 208.

tallata da'awarsa ga baƙi 'yan ƙasashen waje da zasu halarci aikin Hajji. Don haka, sai suka haɗu a gidan Walid ɗan Mughira domin su shawarta. A nan ne fa Allah ya tona asirinsu. Domin kuwa da aka haɗu sai gaba ɗaya suka ce, to, Walid kai ne dattijo mai yawan shekaru da gogewa ga al'amurran rayuwa a cikinmu. Don haka ya kamata mu san ra'ayinka a kan wannan sabon abu da Muhammadu ya zo da shi don mu san abin da za mu faɗa ma baƙi idan suka gabato. Sai Walid ya ce, a'a. Ai ni mai yanke hukunci ne. Don haka ku faɗa sai in ji naku ra'ayi tukuna. Sai wasu suka ce, to mu muna ganin boka ne kawai. Walid ya ce, haba! Yaushe za a haɗa kalaman Muhammadu da na boka? Suka ce, to mahaukaci ne. Ya ce, ai duk mai hankali ya san bai fi Muhammadu ba. Suka ce, to mawaƙi ne. Ya ce, tun yaushe muke jin mawaƙa da zizar maganarsu? Wane nau'i ne na waƙa da ma'aunanta ba mu saba da shi ba? Suka ce, to kenan dai dabo yake yi yana sihirce mutane. Ya ce, anya! A dai sake dubawa. Wallahi wannan abin da Muhammadu yake karantawa wani irin ɗanɗano yake da shi. In ji shi. Ya ce, akwai kuma wata irin nakiya a samansa. Kasansa gwanin daɗi ne. Rassansa kamar nunannun 'ya'yan itace ne. Duk abin da ka faɗi game da shi don ka aibata shi take ana gane ƙaryarka. Amma dai kawai mu tsaya a kan cewa dabo ne yake yi tun da mun ga yana raba ɗa da mahaifi, ya shiga tsakanin wa da ƙanensa ko mata da mijinta, kuma ya raba mutum da danginsa.

Da haka suka tashi zukatansu a cike da ruɗuwa domin sun san ba su yi ma hankulansu adalci ba. Da mahajjata suka gabato sai kuwa suka shiga kamfen ɓatunci a kan da'awar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* tsakanin gaskiya da ƙarya. Abinka da sha'anin gaskiya wannan yekuwa tasu ba abin da ta ƙara ma wannan kira sai karɓuwa da shiga zukatan jama'a. Aka watse daga aikin Hajji duk in da ka je ba abin da ake yi sai taɗi a kan wannan sabon addini. Babu abin da ya fi ba mutane mamaki kamar matsayin da Abu Lahabi ya ɗauka wanda shi ne baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* na bin sa a duk in da ya shiga yana kiran mutane "Ya ku mutane! Ku sheda babu wanda ya cancanci bauta sai Allah don ku samu babban rabo". Shi

kuma sai yana faɗin "Ku fita batunsa ƙarya yake yi"! Daga wannan shekarar ne fa labarin Musulunci ya yaɗu a cikin sassan duniya. Ba in da zaka je ba ka ji ana tattaunawa a kan sa ba.[252]

To, ko waɗanne irin matakai ne Kuraishawa suka ɗauka don ganin sun daƙile hasken Musulunci? Wannan shi ne abin da zai zo a cikin darasi na gaba.

### 3.9.0 Matakan Faɗa da Musulunci

A lokacin da Kuraishawa suka lura da ci gaban Musulunci da yaɗuwarsa sun bi dukkan hanyoyin da suke iyawa don ganin sun daƙile shi. Daga cikin matakan da suka ɗauka har da:

### 3.9.1 Koƙarin Rage ma sa Karfin Tsaro

Babu wani mutum da Allah ya taimaki Manzonsa da shi a wannan lokaci kamar Abu Ɗalib; baffansa. Dalili kuwa, Kuraishawa na jin nauyin sa matuƙa. Shi kuma yana ba Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cikakken goyon baya da kariya ta yadda ba su iya cutata ma sa da kome don jin nauyin baffan nasa. Saboda haka sai suka fara matsa ma sa lamba don ya hana ɗansa ci gaba da wannan kira da yake yi. Ko kuma alal aƙalla ya janye goyon bayan da yake ba shi, alabashi su kuma su far ma sa su yi ma sa duk abin da suka ga dama. Amma Abu Ɗalib bai ba su haɗin kai ba. Sai dai ya gaya ma su kalamai masu daɗi don hana ɗumamar yanayi da yamutsa hazo a tsakanin su.

### 3.9.2. Barazanar Taɓa Lafiyarsa

A wannan karon ne baffansa Abu Ɗalib ya ji ma sa tsoro sosai har ya kira shi yana rarrashinsa a kan kada ya janyo ma kansa matsala. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɗaga kansa sama ya ce ma sa, "Ka ga

252 *Raudhat Al-Anwar Fi Sirat An-Nabiy Al-Mukhtar,* na Mubarakfuri, shafi na 30-31.

wannan rana"? Ya ce, eh. Ya ce: "To, ko daga can za su ɗosano zafi su cinna man ba zai hana ni isar da saƙon Allah ba".[253] A nan ne Abu Ɗalib ya haƙura kuma har ya ƙara da cewa, jama'a wannan ɗan nawa kun san fa bai taɓa ƙarya ba. Don haka kawai ku fita batun sa.

Allah gwanin hikima! Duk wannan ɗauki ba daɗi da ake yi fa shi Abu Ɗalib bai karɓi Musulunci ba. Iyaka dai Allah ya jarabce shi da son ɗansa ne so irin na halitta, ba irin son da musulmi suke yi ma sa a matsayinsa na masoyin Allah kuma jekadansa ba. Kuma da a ƙaddara a wannan lokacin Abu Ɗalib ya musulunta to, da Kuraishawa sun haɗe su gaba ɗaya sun saukar da fushinsu a kan su.[254]

A nan za ka gane cewa, kafirci ma aji aji ne. Ina za a haɗa kafircin Abu Ɗalib da na Abu Lahabi! In da akwai wani kafiri da zai shiga aljanna to, da Abu Ɗalib ne. Amma hukuncin Allah ya zarata a kan haramta ko ƙamshinta a kan kafirai.[255] Amma da yake Allah mai cikakken adalci ne zai sassafta ma Abu Ɗalib azabar wuta har ya kasance a cikin wani kududdufi na wuta wanda shi ne ma fi sassafcin wuri a cikin Jahannama da ceton Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*[256]

### 3.9.3. Soke-soke Da Tuhumce-tuhumce

Mushrikai sun duƙufa sosai wajen ɓata sunan wannan taliki da Allah ya zaɓe shi ya aiko shi don ya isar da saƙo. Suka ce ma sa mahaukaci, boka, maƙaryaci. Kuma wai, ba wani abu ne yake yi ba sai zuƙi-ta-mallau! Amma a banza. Mutane sai ƙara fahimtar gaskiya suke yi suna rungumar ta. Daga bisani sai suka duƙufa wajen ɗaukar matakin izgili da tozartawa.

---

253 *Silsilat Al-Ahadis As-Sahiha,* hadisi na 92.

254 *Nabiyyur Rahmah,* na abokinmu Dr. Muhammad Sani Umar Musa Rijiyar Lemu, shafi na 30.

255 Suratul A'raf: 50.

256 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3670 da *Sahih Muslim*, hadisi na 209.

### 3.9.4 Matakin Izgili da Tozartawa

Babu wani musulmi da bai gamu da wani nau'i na muzgunawa da cutarwa ba a daidai wannan lokaci. Akwai har waɗanda suka yi fice da sunan "'Yan izgili" saboda yadda suka duƙufa wajen cin zarafin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da jama'arsa. Waɗannan mutane sun haɗa da wasu maƙwautansa irin su Uƙbatu ɗan Abu Mu'ait da Adiyyu ɗan Hamra'u da Al-Hakam ɗan Abul Ass da Ibnul Asda'i Al-Huzali da sauransu. Shi Abu Lahabi kam ba a ko maganar cutawar sa shi da muguwar matarsa Ummu Jamil. In sha Allahu za mu kawo wasu daga cikin miyagun ayyukansu don su zama wa'azi da jan hankali a gare mu.

### 3.9.5 Wasu Daga Cikin 'Yan Kungiyar "Izgilawa"

A can baya mun ga irin matakan da arna suka ɗauka don daƙile addinin Musulunci amma ba su ci nasara ba. Don haka sai suka koma ga cin zarafi da amfani da ƙarfin tuwo. Mun ga kuma matsayin da Abu Lahabi ya ɗauka na bayyananniyar adawa shi da muguwar matarsa. To, bari mu ga halin wasu daga cikin fitattun mushrikai - ban da shi - waɗanda suka taka muguwar rawa irin tasa wajen muzguna ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Sahabbansa da kuma irin haƙurin da waɗannan bayin Allah suka yi, sannan daga bisani mu ji umurnin da Allah ya ba su.

**1. Abu Jahali ɗan Hishamu:**

Zanannen sunansa shi ne Amru ɗan Hishamu ɗan Mughira. Ɗan babban gida ne daga yankin Makhzumawa; gidan da ke jayayyar matsayi da Banu Hashim tun kafin bayyanar Musulunci. An yi ma sa laƙabi da Abul Hakam saboda baiwar da Allah ya yi ma sa ta kaifin wayo, wanda a kan sa kawai Kuraishawa suka keta dokar kwamitinsu na dattawa wanda ba a bari kowa ya halarci zaman sa sai ya kai shekaru 50. Amma shi da shekaru 25 aka nemi ya fara halartar sa, don irin kaifin basirarsa. Musulmi sun canja ma sa

wannan laƙabi na *Abul Hakam* (mai wayo) zuwa Abu Jahali (ɗibgagge) kasancewar basirarsa ta daƙile daga bin gaskiya a lokacin da Manzo ya zo da ita.

Abu Jahali na cikin waɗanda ba su jin kunyar cutata ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har a bainar jama'a. Imamul Bukhari ya ruwaito irin wulaƙancin da Abu Jahali ya taɓa yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a cikin ɗakin Allah mai alfarma inda ya yaɓa ma sa mahaifar raƙumi a kan wuyansa tana tsiyaya da jini da ƙazanta a daidai lokacin da Manzon yake sujuda. Kuma aka rasa wanda zai ɗauke ma sa ita har sai da Allah ya kawo 'yarsa Fatima wacce ba wani dattijon da ke iya yi ma ta kome saboda ƙanƙantarta.[257]

**2. Uƙbatu ɗan Abu Mu'aiɗi:**

Shi kuma wannan ɗan gidan Umayyatu ne. Kuma shi ne ya taɓa shaƙe wuyan rigar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a lokacin da yake sallah. Bai sake shi ba har sai da Sayyidi Abubakar *Radhiyallahu Anhu* ya lura da shi ya rugo ya cafke shi ta wajen kafaɗunsa ya tunkuɗe shi yana karanta faɗar Allah Ta'ala: *"Haka kawai za ku kashe mutum don ya ce Allah ne ubangijina! Alhalin kuma ya zo ma ku da hujjoji daga wurin ubangijinku?"*[258]

3. Akwai kuma Asi ɗan Wa'il wanda Allah ya saukar da aya ta 78-80 a cikin Suratu Maryam a kan sha'aninsa. Ya kasance mai yawan izgili da bayyana adawa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Sahabbansa.[259]

4. Akwai Walid ɗan Mughira, baffan Abu Jahali wanda Allah ya yalwata ma sa arziki, ya ba shi wadatar haifuwa. Amma sai ya kasance kuri yake yi ma Allah da waɗannan ni'imomi da ya yi ma sa. Ya taɓa jin karatun Kur'ani daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har ya ratsa jikinsa,

---

[257] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 1794.

[258] Suratu Gafir: 28. *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3678.

[259] Duba: *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 2091 da *Sahih Muslim*, hadisi na 2795.

ya gaya ma mutane cewa, wannan magana ta fi ƙarfin mutum ko aljani, kuma ɗanɗanonta ya fi ƙarfin a misalta. Amma da suka kira shi a gaban kwamitin dattawa sai ya waske; ya ce, ai Kur'ani siddabaru ne kawai mai sa masoya su raba gari su koma gaba. A kan sa ne Allah Ta'ala ya saukar da ayoyin Suratul Muddassir daga ta 11 zuwa ta 30.[260]

5. Akwai kuma Nadhru ɗan Al-Harith daga gidan Abdud-Dar. Mutum ne da ya yi tafiye tafiye a ƙasashen waje ya zo da labarai masu nishaɗantarwa. Kuma da su ne yake ƙoƙarin ɗauke hankalin mutane daga ayoyin Allah da Manzo yake karantawa.[261]

6. Akwai Aswadu ɗan Abdu-Yaguth wanda ya fito daga gidan kawunnen Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* amma yana nufin sa da izgili, yana cewa, "Yau Muhammadu ko an samu wani saƙo daga sama?".[262]

7. Akwai Aswadu ɗan Abdulmuɗɗalib ɗan ƙabilar Banu Asad. Kanen uwarmu Nana Khadija ne a wajen zumunta. Amma Allah bai yi ma sa rabo ba, sai ya yi rajista da wannan ɓatattar ƙungiya ta masu izgili wadda Allah ya saukar da ƙarshen Suratul Muɗaffifun a kan su da kuma aya ta 95 zuwa 96 a cikin Suratu Hijr.[263]

### 3.10 Musulunci ya ci Gaba da Yaɗuwa a Sauran Sassa

Kafin mu koma kan irin azabar da musulmi suka ɗanɗana a hannun mushrikai, za mu yi tsokaci game da yaɗuwar Musulunci a wannan zamani da muke magana a kan sa zuwa sauran sassan yankunan larabawa. Duk da irin muzgunawar da Manzon rahama *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake gamuwa da ita a cikin Makka da cin zarafin da danginsa Kuraishawa suke yi

[260] *As-Sirah An-Nabawiyyah* na Ibn Ishaƙ 1/332-334 da *Al-Mustadrik* na Hakim 2/506 kuma Hakim din ya inganta shi, ya samu amincewar Imam Ad-Dhahabi.
[261] *Nur Al-Yaƙeen,* na Sheikh Muhammad Al-Khudary, shafi na 38.
[262] Duba littafin da muka faɗa a sama, a wurin da ya gabata.
[263] Duba littafin da muka faɗa a sama.

ma sa, gami da kanfe na ɓatunci. Duk waɗannan ba su hana addinin Musulunci ya ci gaba da miƙawa zuwa ƙasashen waje ba. Kai, saboda irin yadda ake maganarsa a garuruwa ne ma wasu masu tsarkin zuciya da neman gaskiya suka yo tattaki zuwa birnin Makka don tantancewa da gane gaskiya, kuma cikin iyawar Allah da suka samu gaskiyar nan take suka karɓe ta. Daga cikin waɗanda Allah ya yi ma wannan baiwa akwai:

**1. Abu Dhar Al-Gifari:**

*Gifara* ƙabila ce da take kan hanyar Makka zuwa Madina, a cikin yankin Yanbu' na yanzu, 'yan kilomitoci kaɗan zuwa Madina. A wajen su ne kuma gunkin Manata yake. A gidajen wannan ƙabilar ne labarin bayyanar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya je ma su, sai Abu Dharr ya aiki ƙanensa Unais don ya nemo ma sa gaskiyar labarin. Da ɗan uwan nasa ya zo sai ya ce ma sa, ni dai na ga wani mutum mai alamun kirki yana kira zuwa ga alheri. Abu Dharr ya ce, bari in je da kaina. Da ya zo Makka bai nemi labari wurin kowa ba sai ya lizimci kawaici kwana da kwanaki yana kiwon hankalin mutane, har Allah cikin ikonsa ya haɗa shi da Sayyidi Ali ɗan Abu Ɗalib *Radhiyallahu Anhu* wanda - a cikin hikima da kauce ma idon maƙiya - ya kai shi wajen Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Ba tare da ɓata lokaci ba Abu Dharr ya musulunta. A nan ne fa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ba shi shawarar ya komawarsa gida salun alun bakinsa ƙanen ƙafarsa. Amma Abu Dhar ya ce, a'a. Shi fa bai ga abin ɓoyo ga addinin gaskiya ba. Ai kuwa shelantawarsa ke da wuya da furta kalimar shahada a farfajiyar Ka'aba sai kafirai suka yi ma sa cah! Suka ce da wa Allah ya haɗa mu ba da kai ba! Suka rinƙa dukan sa har kamar zasu kashe shi. Da ƙyar Abbas - baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* - ya ƙwace shi daga hannunsu yana tsoratar da su daga martanin ƙabilarsa. Duk da haka kuma kashegari Abu Dharr bai bar Makka ba sai da ya sake shelanta imani. Da zai

tafi gida kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya neme shi da ya kira mutanensa - idan ya je - zuwa ga Musulunci.[264]

Da komawar sa gida sai duk 'yan gidansu suka musulunta. Cikin su har da mahaifiyarsa. A rana ɗaya rabin garin suka musulunta bayan da ya tara su ya ba su labarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Sauran rabi kuma suka ce, idan Manzon Allah ya zo zasu yi masa mubaya'a hannu da hannu. Kuma da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi hijira zuwa Madina sai duk suka cika alƙawari; suka same shi a can suka miƙa hannayensu suka yi ma sa caffa.[265]

Wannan tabbataccen labarin da muka kawo yana nuna mana ko wane irin mutum ne shi Abu Dharr. Babu shakka yana cikin irin nau'in mutanen da jita-jita ba ta girgiza su. Haka kuma ba sa shayin bayyana ra'ayinsu ko sama na ruwan kibau ƙasa na aman wuta. Kamar yadda zamu gano kaifin hankalinsa da basirarsa tare da tsarkin zuciyarsa a cikin wannan labari. Abin da ya sanya shi bai yi jayayya ba ko kaɗan da aka karanta ma sa saƙon Musulunci. Haka kuma zamu ga yadda mutanensa suka amince da shi. Dalilin da ya sa suka karɓi Musulunci nan take. Tun kafin bayyanar Musulunci Abu Dhar mutum ne mai taka-tsantsan da kirdadon gaskiya a cikin duk lamurransa.[266]

Da irin waɗannan tsarkakakkun bayin Allah ne Manzon Allah ya fara aza tubalin addini. Akwai wasu ire-irensa waɗanda jita-jitar da ake yaɗawa a kan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ta zamo dalilin shiriyar su.

**2. Amru Ɗan Abasata:**

Wannan shi kuma wani bawan Allah ne da ya kasance yana ƙyamar ayyukan jahiliyya. Don haka da ya ji ana zagin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa ya bar tafarkin da aka sani sai ya niƙo gari ya nufato

264 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3522 da *Sahih Muslim*, hadisi na 2474.
265 *Sahih Muslim*, hadisi na 2473.
266 An bayyana cewa, a kan haka ne aka sa ma sa suna Abu Dhar don takatsantsan da yake yi wajen awon abincin da yake saidawa.

Makka. Ko da ya zo ana tsakiyar lokacin da musulmi suke shan azaba. Da ƙyar da dabara ya samu keɓanta da ma'aiki. Sai ya tambaye shi "Wane ne kai?" Ya ce ma sa "Ni Annabi ne". Ya ce, mene ne Annabi? Ya ce: "Allah ne ya aiko ni". Ya ce: Da me ya aiko ka?". Ya ce: "Ya aiko ni da sada zumunta, da karya gumaka. Kuma ya ce, kada a bauta ma kowa sai shi kaɗai". Amru ya ce: "To yanzu wa ke tare da kai?" Ya ce: "Akwai ɗa, akwai kuma bawa". A nan ne fa Amru ya ba da gaskiya kuma ya ƙulla niyyar zama a wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* duk da halin da ya tarar ake ciki domin ya koyi addini. Amma sai Manzon Allah ya lurar da shi cewa, Makka ba ta zaunuwa a gare ka tare da mu a yanzu. "Ba ka ganin halin da muke ciki da jama'a?" "Kai dai ka tafi kawai garinku. Idan ka ji Allah ya ba ni rinjaye sai ka zo ka same ni". Amru ɗan Abasata sai ya koma garinsu yana bibiyar labarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har sai da ya ji zuwan sa Madina da yadda Allah ya ɗaukaka shi sannan ya zo ya same shi. Da suka haɗa fuska sai ya ce ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* "Ko ka sheda ni?" Manzon Allah ya ce, ƙwarai kuwa. Ai kai ne ka same ni a Makka. Sannan sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya koya ma sa yadda ake sallah da lokutanta kuma ya sanar da shi falalarta.[267]

Amru ɗan Abasata yakan ce ni ne na huɗu a shiga Musulunci. Domin ya fahimci waccan magana ta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* "Akwai ɗa, akwai kuma bawa" a matsayin cewa, mutum biyu kawai ke tare da shi, Manzo shi ne na ukun su. Alhalin kuwa a daidai lokacin da ya musulunta adadin musulmi na da yawa matuƙa amma suna cikin rauni sosai. Don haka daga cikin siyasar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ba ya bayyana adadinsu da sunayensu saboda dalilai na tsaro.[268]

Daga cikin darussan wannan karatu muna iya lura cewa, masu tsarkin zukata waɗanda suka fi kusa da fiɗira irin shi wannan bawan Allah su ne suka fi sauƙin fahimtar gaskiya da kuma karɓar ta. Dubi yadda ya rinƙa kula da bin

267 *Sahih Muslim*, hadisi na 832.
268 *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Kathir 1/443.

labarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har inda ya gano lokacin da ya yi hijira da inda ya tafi sa'annan ya bi shi ya koyi addini. Haka kuma mun ga irin halin matsatsi da musulmi suke ciki a wancan lokaci wanda har ya sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana gudun ajiye baƙi da ke son su zauna wurin sa su koyi Musulunci. Ga kuma yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake kula da fahimtar masu zuwa wurin sa kuma ya sheda su kome daɗewar lokaci. Amsar da Manzon Allah ya ba shi a lokacin da ya tambaye shi "Da me Allah ya aiko ka?" Ita ce: "Ya aiko ni da sada zumunta, da karya gumaka". Don haka addini haƙƙe biyu ne; na Allah da na bayinsa. Duk wanda ya tozarta ɗaya to babu shakka ya samu tawaya a addininsa. Allah muke roƙo ya inganta imaninmu.

**3. Dhimad Al-Azdi:**

Dhimad ɗan ƙasar Yemen ne, daga fitacciyar ƙabilar nan ta Azd-Shanu'a masu dogon tarihi. Mutum ne da Allah ya yi ma sa baiwa ta yin ruƙiyya ga masu fama da kamun iskoka. A lokacin da ya ji wawayen Makka suna taɗin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* suna ce ma sa mahaukaci ya ɗauka maganar arziki ce. Don haka sai ya ɗauki alƙawarin zuwa ya yi ma sa tawada ko Allah zai sa a dace a tunaninsa. Ya kuwa zo wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya gabatar da kansa yana cewa: "Ya Muhammad! Ni mutum ne da nake tawada ga waɗanda aka jarabce su da kamun iskoka. Kuma da yawa waɗanda Allah ya ba su lafiya a sanadiyyata. Ko kana da buƙata?" Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kimtsa domin ya yi ma sa jawabi. Sai ya soma da gabatarwar da yake yi wacce ta ƙunshi godiya da yaba ma Allah a kan cewa, duk wanda Allah ya shiryar shi ne shiryayye, wanda kuma ya ɓatar babu mai juya shi zuwa tafarkin shiriya. Sannan sai Kalmar shahada. Kamar dai yadda muke ji masu huɗuba suna fara huɗubobinsu "*Innal hamda lillah...*". Sannan sai ya ce, *amma ba'ad*..

A nan ne Dhimad ya ce ma sa "Dakata. Maimaita wannan kalamin naka". Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai musanta ma sa ba sai ya

sake maimaitawa. Suka yi haka har sau uku. Dhimad ya ce, to ai ba ka buƙatar ka yi wani jawabi. Wannan ma ya ishe ni. Wallahi ba irin bokayen da ban gani ba da masu siddabaru da mawaƙa. Ban taɓa jin magana mai kama jiki ba irin wannan taka. Kuma na yi amanna kai ba ko ɗaya ba ne a cikinsu. Ba ni hannunka kawai in yi maka caffa a kan shiga Musulunci. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, to zaka karɓa ma mutanenka? Ya ce, eh, har da mutanena.

Akwai wata rana da ayarin mayaƙan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* suka shuɗa ta kan mutanen Dhimad suka yada zango a wajensu. Da aka tashi wucewa sai shugaban ayarin ya ce, akwai wanda ya taɓa kayan waɗannan mutane a cikin ku? Sai wani mutum ɗaya ya ce, eh. Na ɗauki shantalinsu na kama ruwa. Ya ce, to ka mayar ma su da kayansu. Waɗannan mutanen Dhimad ne.[269]

Haka dai zamu ga duk wata furofagandar da Kuraishawa suka yi don su ɓata sunan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ko su dushe haskensa sai ta ƙara ingiza masu hankali zuwa ga bincike da gane gaskiya. Duba kuma irin kyawon halin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yadda wannan ya zo ya ce zai yi ma sa ruƙiyya amma bai nuna fushi ba sam ko damuwa. Ya dai yi niyyar ya yi ma sa bayanin ko shi waye. Amma cikin hikimar Allah shimfiɗar bayaninsa kawai sai ta ishi wannan bawan Allah mai wankakkiyar zuciya. Daga nan kuma masu wa'azi da huɗuba ya kamata su fahimci muhimmancin irin wannan shimfiɗa mai albarka da take buɗe zukata masu tsarki, ta wanke masu ƙazanta da dauɗar son zuciya da saɓon Allah. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai yi nauyin baki ba da wannan bawan Allah ya musulunta sai ya ce ma sa ya isar da saƙon Musulunci zuwa ga jama'arsa, kasancewarsa mutum mai daraja da matsayi wanda in ya faɗa ana saurarawa. Su kuma Sahabbai suna darajanta duk wanda suka san yana da

269 *Sahih Muslim*, hadisi na 868 daga ruwayar ɗan Abbas *Radhiyallahu Anhu.*

matsayi a wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Don haka suka ce a ƙyale mutanen Dhimad, kome nasu kar a taɓa.

## 3.11 Musulmi Sun ci Gaba da Fuskantar wulaƙanci

### 3.11.1 Matakin Azabtawa

Jarrabawa sunnar Allah ce da take tare da ma'abuta gaskiya a duk inda suka kasance. Da ita ne Allah yake rarrabe masu addini da gaskiya daga munafukai masu yin sa kawai don holewa da jin daɗi. Haka kuma babbar makaranta ce da take horar da mazaje a kan haƙuri da jarunta da sadaukarwa. Ga waɗanda suka ɗanɗane ta ba abin da ya kai jarabawa daɗi saboda tsarkake zuciya da kaifafa imani da take yi.

Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sun gamu da jarabawa matuƙa a farkon al'amari. Ka daina zancen masu rauni daga cikin su kamar bayi da marasa galihu da ƙananan yara. Manyansu ma ba a bar su suka sarara ba. Misalinmu na farko a kan mashahurin ɗan kasuwa ne, dattijo, mai abin hannunsa. Amma saboda kusancinsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* mushrikai ba su bar shi ba. Wannan dattijo shi ne babban na hannun daman Manzon Allah; Abubakar Siddiƙu.

A lokacin da adadin musulmi ya kai 38 Sayyidi Abubakar *Radhiyallahu Anhu* ya samu Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana ba da shawarar a fito fili ayi da'awa. Sai ya ce ma sa, "Ya Abubakar! Mu fa har yanzu 'yan kaɗan ne". Amma Abubakar bai gushe ba yana nuna ma sa muhimmancin fitowar har sai da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya amince. Musulmi sun san da wannan shiri da aka yi. Don haka, a ranar da za a zartar da wannan shiri ko wanensu ya koma cikin danginsa ya yi garkuwa da su. A daidai lokacin da masallaci ya cika ginjim da mutane sai kawai aka ga Sayyidi Abubakar ya miƙe tsaye - a lokacin shi kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana zaune. Abubakar ya ce, "Ya ku jama'a! Ku bi Allah, ku bi Manzonsa". Iya abin da ya faɗi kenan. Amma rufe bakinsa ke da wuya sai arna suka yo cah a kan sa. Wasu na dukan sa da takalmi, wasu da duwatsu, wasu kuma da duk abin da suka samu iko, har suka kai shi ƙasa. Utbatu ɗan Rabi'ata ya ɗare a kan cikinsa yana dukan sa da tsinin takalmansa a fuska har

sai da fuskarsa ta caɓe da jini. Dangin Abubakar suka zo suka ɗauke shi a uzurce, ba sa tsammanin yana da sauran numfashi har suka kai shi gidansa. Nan take kuma suka ƙulla mitin a tsakanin su suka yi ijma'i a kan cewa, idan ya cika za su kashe Utbatu duk kuwa abin da hakan zai iya janyowa. Suka fito fili suka shelanta haka a bainar jama'a.

Abu Kuhafata, mahaifin Abubakar ya shiga damuwa matuƙa duk da yake a lokacin bai musulunta ba. Amma yana juyayin abin da ya cim ma ɗansa. Ga kuma fitinar da hakan za ta iya haifarwa a tsakanin Kuraishawa. Can bayan wani lokaci sai aka samu Abubakar ya fara jin sauƙi har yana son ya yi magana. Da ya samu ikon buɗa bakinsa abu na farko da ya ce shi ne, ina Manzon Allah? Ba wanda ya iya ba shi amsa a cikin su. Ummul-Khair; mahaifiyarsa ta nace ma sa sai ya ci abinci. Shi kuma ya yi rantsuwa ba abin da zai shiga bakinsa sai ya ji labarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Da mahaifiyarsa ta nuna ma sa ba ta da masaniya akai sai ya ce ma ta ki je wajen Ummu-Jamil ‘yar Haɗɗabi - ƙanwar Umar - za ta ba ki labari. Ummu-Jamil ba ta yarda ta ce komai game da Manzon Allah ba don ba ta san manufar tambayar ba. Amma sai ta yi dabara. Ta ce, idan kina so mu je in duba ɗanki. Hankalin Ummu-Jamil ya tashi matuƙa ganin irin halin da ta tarar da Abubakar. Ba ta san lokacin da ta rusa kuka ba har da hargowa tana la'antar Utbatu da waɗanda suka goyu bayan sa. Abubakar ya tambaye ta labarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Sai ta ce ma sa, ga ummarka nan tana jin ka. Ya ce, kar ki damu da ita. Gaya mini kawai. Sai ta ce, lafiyarsa ƙalau. "A ina yake?" Ya tambaye ta. Ta ce: a Dar Al-Arƙam. Ya kalli mahaifiyarsa ya ce ma ta wallahi kome ba zan ci ko in sha ba sai na ga Manzon Allah. Nan take suka yi shawarar a saurara har sai dare ya yi, ƙafafu sun ɗauke. Sannan su biyun suka ɗauke shi yana dogara ga kafaɗunsu har suka zo da shi gidan Arƙam wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Manzon Allah kuwa ya nuna alhininsa matuƙa, sannan ya rungume shi, ya sumbace shi. Musulmi suka taso suna ta ba shi haƙuri. Abubakar ya tabbatar ma su da cewa wannan ba komai ba ne a bisa tafarkin Allah. Sannan ya roƙi

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana mai cewa, ga uwata nan ya Manzon Allah. Tana so na matuƙa, kuma tana kyautata min. Kai kuma mutum ne mai albarka. Ka kira ta zuwa ga Musulunci sannan ka yi ma ta addu'a ko Allah zai sa ta rabauta, ta kuɓuta daga wuta. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma ta wa'azi kuma a nan wurin ba ta ɗaga ba sai da ta musulunta.[270]

Ka ji mazaje masu imani, kishin bayyanar da addini, da sadaukarwa a kan sa. Ka ga kuma yadda son Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kama zuciyar wannan mutum har ba ya iya cin abinci ko ya sha ruwa bayan duk wannan azabar da ya sha sai ya ga masoyin nasa, ya samu natsuwa a kan lafiyarsa. Babu shakka musulmi a wancan lokaci mutane ne masu kaifin basira. Kana iya gane haka in ka dubi matakan da Ummu-Jamil ƙanwar Umar ta ɗauka. Ba ta faɗa ma Ummul-Khairi kome ba game da Manzon Allah tun da ba ta san niyyarta ba, amma kuma sai ta yi dabarar zuwa da kanta wajen Abubakar don ta tabbata in shi ne yake son labarin. A nan ma sai da ta yi taka-tsantsan wajen ba da amsar tambayarsa. Kuma a cikin kukan da ta yi da la'antar kafirai akwai jan hankalin Ummul-Khair don ta gane ɓacin tafarkinsu. Haka kuma saurarawar da suka yi har dare ya yi, ƙafafu suka dauke. Dabara ce wacce take da muhimmanci. Domin wurin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake tare da Sahabbansa wani sirri ne da bai dace a daidai wannan lokaci a tona shi ba. Shi kuma Sayyidi Abubakar wannan halin da yake ciki bai hana shi nuna fatarsa na shiriya ga mahaifiyarsa ba. Kuma sai Allah cikin rahamarsa ya sa aka dace.

To, idan irin wannan babban mutum, dattijo, mai yawan alheri, mai kwarjini da karɓuwa ga jama'a an yi ma sa haka. Ya kake zato ga bayin Allah marasa galihu, masu rauni?

---

[270] Duba: *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Kathir 1/439-440 da *Al-Biɗayah Wan-Nihaya,* nasa 3/30 da kuma *Mihnatul Muslimin fi Al-Ahd Al-Makki,* na Dr. Sulaiman as-Suwaikit, shafi na 79.

Abdullahi ɗan Mas'ud *Radhiyallahu Anhu* ya bayyana irin halin da musulmi suka shiga a wancan lokaci. Yana cewa: "Mutane bakwai ne aka fara sanin Musuluncinsu. Su ne: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Abubakar da Ammar da mahaifiyarsa Sumayya. Sai kuma Suhaibu da Bilal ba Miƙdad. Shi dai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, Allah ya ba shi kariya ta hanyar baffansa Abu Ɗalib. Abubakar shi ma da danginsa ne Allah ya yi ma sa shamaki daga gare su. Sauran kuwa sun sha azaba wadda ba ta misaltuwa. Aka rinƙa sanya ma su walkin ƙarfe ana azabta su a rana. Duk cikin su babu wanda ba a ɗimauta hankalinsa aka tilasta shi furta kafirci ba in ban da Bilal.

2. Babu yadda kafirai ba su yi da Bilal ba don ya sauya ra'ayi ya koma kafirci har suka gaji suka miƙa shi ga Shaiɗanun yara suna yawo da shi rango rango a cikin Makka. Shi kuma ba abin da yake fadi sai "Ahad! Ahad!!" Yana nuni zuwa ga imaninsa da tauhidi, kuma yana tabbata ma su ba gudu babu ja da baya.[271]

Allahu Akbar! Bilal bawan Allah. Shi ba wata ƙabila ko wasu dangi ko wani gida da yake kariyar sa. Shi ba ɗan gari ba ne, ba kuma farar fata ne ba. Ba shi da ƙarfi, ba shi da 'yanci. Domin bawa ne wanda aka saya da kuɗi. Amma fa yana da zuciya mai ƙarfi, da imani mai kauri, da sadaukantaka wacce 'ya'ya masu 'yanci suke buƙatar su koya daga wurin sa. Don haka bai fasa yin ɗa'ar da ta dace ga maigidansa Umayyatu ɗan Khalaf ba. Amma maganar aƙida ya riga ya zaɓa ma kansa wacce yake ganin za ta fis she shi. Kuma duk wani mataki da za a ɗauka ba zai hana shi bayyana aƙidarsa ba. Ana cikin haka ne wata rana, Allah - cikin ikonsa - ya biyo da Abubakar *Radhiyallahu Anhu* ta in da Umayyatu yake azabta bawansa Bilal. Da Abubakar ya gane ma idonsa abin da ke faruwa sai ya tsaya ya yi ma Umayyatu wa'azi yana ce ma sa, ka ji tsoron Allah ka fita batun wannan taliki. Umayyatu ya kada baki ya ce, to wane ne ya lalata min shi ba kai ba? Ka saye

[271] *Al-Musnad* na Imam Ahmad, hadisi na 3832. Kuma isnadinsa yana da kyau.

shi kawai in kana so ka ‘yanta shi. Take Sayyidi Abubakar ya karɓi tayinsa; ya sayi Bilal ya 'yanta shi. Daga nan Bilal ya fara shaƙar ƙanshin 'yanci da bautar Allah a cikin sarari ba tare da tsangwama ba. Tun da yake yanzu ya zama da mai 'yanci kamar kowa.

Shi kuma Sayyidi Abubakar ba wannan ne karon farko da yake ‘yanta bayin Allah masu shan wahala a hannun kafirai ba. Domin shi ne ya ‘yanta Amiru ɗan Fuhairata - wanda ya halarci Badar da Uhud kuma ya samu shahada a Ma'una. Haka kuma ya ‘yanta bayi mata da dama. Cikin su har da Ummu Ubais da Zinnirah wadda kafirai suka yi ma ta duka har suka tsiyaye idonta. Kuma suka riƙa yi ma ta gori cewa, don tana zagin Lata da Uzza ne suka makantar da ita. Amma da ta roƙi Allah sai ya warkar da ita, ganinta ya dawo garau. Haka kuma Abubakar *Radhiyallahu Anhu* ya ‘yanta Nahdiyya da 'yarta a lokacin da ya gan su uwargidansu ta aike su niƙan gari tana faɗin wallahi ba zan taɓa ‘yanta ku ba. Bayan da ya yi cinikinsu ya biya sai ya ce ma su ku ajiye ma ta garinta. Sai suka ce, ko dai mu fara kai ma ta niƙan mu dawo? Ya ce, in kuna so ku kai ma ta ba laifi. Akwai kuma wata kuyangar da ya isko Umar ɗan Haɗɗabi na azabtar da ita. Ita ma ya saye ta ya ‘yanta ta.[272]

**3. Iyalan Gidan Yasir:**

Idan ana maganar wahalar da musulmi suka sha a hannun kafirai ba zai yiwu a manta da Yasir da iyalinsa ba. Asalin Yasir ɗan ƙasar Yemen ne. Alherin Allah ya ingizo shi zuwa Makka wajen neman wani ɗan uwansa. Ya zauna a ƙarƙashin Abu Huzaifa ɗan Mughirah Al-Makhzumi wanda ya aurar ma sa kuyangarsa Sumayya suka haifi Ammar. Da Musulunci ya zo su duka ukun suka sa hannu biyu suka karɓe shi. Makhzumawa kuwa suka rinƙa azabta su azaba wadda ba ta misaltuwa. Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da kansa ya gane ma idonsa irin azabar da ake yi ma su. Ya riƙa ba su haƙuri yana cewa, "Ku yi haƙuri iyalan Yasir, babu shakka aljanna ce makomar

[272] *As-Sirah An-Nabawiyyah* na Ibn Hishamu, 1/393.

ku".[273] Ita dai Sumayya Abu Jahali ne ya kashe ta. Shi kuma Yasir kaifin azaba ya gama da shi. Suka bar ɗansu Ammar yana ɗanɗanar zafin azaba a cikin zafin duwatsun Makka har sukan gigita shi ya furta kalmar kafirci bai sani ba don neman su sassafta ma sa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ma su addu'a yana cewa, "Ya Allah ka gafarta ma iyalan Yasir. Kuma ma ai ka riga ka gafarta ma su".[274]

### 3.12 Musulmi Sun Jure Wahala

Waɗanda muka faɗi a baya ba su kaɗai ne suka sha wahala ba. Kusan duk wanda ya shiga Musulunci a wancan lokaci kome matsayinsa sai da ya ɗanɗani wahala kuma ya jure ma ta. Ga wasu ƙarin misalai:

**4. Khabbab Ɗan Al-Arat:**

Khabbab wani maƙeri ne da yake ƙarƙashin wata muguwar mata ana ce da ita Ummu Anmar daga ƙabilar Khuza'ata. Taron dangi suka yi a kan azabta shi har sukan kwantar da shi rairan (bayansa na ƙasa ƙirjinsa da fuskarsa na sama) a kan duwatsu masu zafi. Da wannan matakin ya kasa yi masu amfani sai Ummu Anmar ta ɗauko wani ƙarfe mai zafi a maƙerarsa ta yi masa lalas da shi a ka. A nan ne fa ya je ya kai ƙara wajen ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Babu wani abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* zai iya yi masa a wannan lokaci sai addu'a. Addu'arsa kuwa ba ta faɗuwa a ƙas. Da Allah ya karɓi addu'ar Manzonsa sai wannan mata ta fara ciwon kai. Wasa-wasa ciwon yai ma ta tsanani har ya fara sa ta hauka. Duk maganin da aka ba ta sai ta ji shi kamar garwashi a kanta. Ta rinƙa haushi irin na karnuka har ta fara damun mutane. Sai aka ba ta shawarar ta yi lalas!

Ka ga ikon Allah! Da kanta ta kira Khabbab ta ce ya taimake ta da wannan magani. Khabbab ya ɗauko ƙarfen nan ya hasa wuta ya gasa shi yadda

[273] *Sahih As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibrahim Al-Ali, shafi na 97-98.
[274] *Majma' Az-Zawa'id* na Haithami, (9/293).

ya kamata. Sannan ya ɗauko shi ya rinƙa wasa shi a kanta tana ihu!. Ya kake zaton imanin Khabbab game da Allah da Manzonsa bayan faruwar wannan abin al'ajabi mai nuna cikar ikon Allah? Za ka yarda Khabbab da ire-irensa da suka rungumi Musulunci a irin wannan lokaci munafukai ne? To, wa za su munafurta? Kuma don su cim ma me?

Kafirci bala'i! Faruwar wannan aya bai sa musulmi suka samu sararawa daga ƙunci da azaba ba. Wata rana sai da Khabbab ya je ya samu Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, ya Manzon Allah! Me zai hana ka nema mana taimakon Allah, ka yi mana addu'a? Wannan roƙo na nuna matuƙar damuwa da raki wanda bai dace da matsayin makusantan Annabin Allah ba. Kuma ita sunnar Allah ba ta canjawa. Don haka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɓata rai matuƙa. Yana kishingiɗe a inwar Ka'aba sai ya tashi zaune. Sannan ya ce ma sa: "A can baya, an yi lokacin da ake zuwa da mutum a tona masa ƙabari a kafe shi sa'annan a zo da zarto a tsaga jikinsa daga tsakiyar kansa zuwa ƙarƙashin ƙafafunsa. Wani kuma a yi mashaci da ƙarfe tsakanin tsokarsa da ƙashinsa. Duk wannan bai hana su yin addini ba. Wallahi, Allah zai cika addinin nan nasa har matafiyi ya bar San'a'a ya je Hadramaut bai jin tsoron kowa sai Allah, sai kuma tsoron kura ta kama awakinsa ba dai mutum ba. Amma ku kun cika gaggawa".

Da haka aka kafa addini a kowa ce al'umma. Dole ne a samu masu sadaukar da rayukansu da lafiyarsu da jin daɗinsu don ɗaukaka addini a farkon lamarinsa. Waɗannan kuma Allah da kansa ne yake zaɓar su.

A zamanin khalifancin Umar *Radhiyallahu Anhu* an taɓa tada zancen wahalhalun da aka sha a baya sai Sayyidi Umar ya ce a kira Khabbab. Ya ce ma sa ya cire rigarsa don ya nuna ma mutane bayansa. Sai suka ga abin kuka

musamman bayan da ya rinƙa hikaito masu yadda ake hasa wuta a maƙerarsa, a kwantar da bayansa a kanta har sai ta huce.[275]

**5. Khalid Ɗan Sa'id Ɗan Al-Ass:**

Wani bawan Allah ne saurayi ɗan babban mutum. Mahaifinsa na ɗaya daga cikin masu faɗa a ji a birnin Makka. Lokacin da Allah ya nufe shi da samun shiriya sai ya nuna ma sa a cikin mafarkin yana kan gaɓar wuta. Ga mahaifinsa na ta ƙoƙarin ingiza shi. Shi kuma Muhammadu *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana rirriƙe shi yana hana shi afkawa a ciki. Ko da ya farka a tsorace sai ya ce, wallahi wannan mafarkin gaskiya ne. Nan take ya nufi wajen Sayyidi Abubakar a matsayinsa na aboki kuma makusancin Manzon Allah, ya kwashe labarin mafarkinsa ya faɗa ma sa. Abubakar *Radhiyallahu Anhu* ya ce ma sa, kaiconka! Wallahi Allah na nufin alheri ne a gare ka. Mu je in kai ka wurin Manzon Allah. Da suka je ya saurari Alƙur'ani sai ya musulunta. Amma saboda irin halin da ake ciki sai ya ɓoye Musuluncinsa kamar yadda sauran musulmi a wannan lokaci suke yi. Yau da gobe mahaifin Khalid ya ji ƙamshin wainar da ake toyawa don ya ga ɗabi'unsa sun canja kuma yanzu ba a koyaushe ne ake sanin in da ya tafi ba. Sai ya sa ma sa 'yan leƙen asiri waɗanda suka tabbatar ma sa inda ɗan nasa yake zuwa. Ya kuwa yi ma sa faɗa matuƙa har ya kai ga dukan sa da wata sanda wadda ya kakkarya ta a kan sa. Daga bisani ya ɗaure shi a gida kuma ya hana mutanen gida su yi magana da shi. Khalid yana ta haƙuri yana kai kukansa zuwa ga Allah. Da Sa'id ya kasa shawo kan ɗansa ya bar Musulunci ya koma ga addinin gargajiya sai ya ɗauki wani mataki na gaba. Shi ne matakin hana shi abinci. Sai da ya kwana uku ba tare da an ba shi ko kurɓin ruwa ya sa a bakinsa ba. Sannan mahaifinsa ya ga babu makawa ga barin sa, sai ya sake shi. Daga nan ya ƙara sakin jikinsa a wurin Manzon Allah. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana

[275] Duba: *Ar-Raud Al-Unuf* na Suhaili, 2/98 da *Sahih Al-Bukhari*, 3612 da *Mihnat Al-Muslimeen Fi Al-Ahd Al-Makkee*, na Dr. Sulaiman As-Suwaikit, shafi na 95.

darajanta Khalid a kan haƙurinsa da ƙarfin imaninsa. Daga bisani Khalid na cikin waɗanda aka tura su gudun hijira don kariyar lafiyarsu da imaninsu da kuma samar ma su da isasshiyar horarwa don fuskantar matakin da yake tafe wanda yake buƙatar jan damara a nan gaba.[276]

**6. Mus'abu Ɗan Umair:**

Mus'abu wani yaro ne matashi a garin Makka. Sagartacce ne, ɗan gata. Iyayensa suna ji da shi matuƙa, kuma suna nuna ma sa so na ƙin ƙarawa. Ga su masu arziki da wadata. Ba wani matashi a garin Makka wanda ya kai kyawon tufansa ko ƙanshin turarensa. Kai, ko takalmansa ma abin kallo ne. Ta fuskar abinci shi bai taɓa sanin mai wuta biyu ba. Ana haka sai Allah ya jefa Musulunci a zuciyarsa. Ya kuwa tafi har Dar Al-Arƙam ya musulunta. Musuluncinsa ya kasa ɓoyuwa har iyayensa suka tsare shi a cikin gida suka hana shi zuwa ko ina. Kuma duk da irin son da suke yi ma sa amma a kan Musulunci sun nuna ma sa rashin imani matuƙa. Suka sanya shi a wani hali mai ban tausayi. Bai samu kansa ba sai da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shirya ayarin masu gudun hijira zuwa Habasha sannan Mus'ab ya sulale ya bi su. A kan hanyar su ta zuwa Habasha an ba da labarin yadda ya sha wuya kasancewar babu wani guzuri a tare da shi. Amma kuma 'yan uwansa Sahabbai sun tausaya ma sa, tare da tallafa ma sa da iya dan abin da suke da shi. Bayan da ya dawo daga makarantar Habasha ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya nada shi jakada na farko zuwa birnin Madina in da ya yi amfani da hikima ya nuna ƙwarewa wajen kira zuwa ga Musulunci da kyakkyawan salo wajen isar da saƙonsa. Kafin wani ɗan lokaci masu faɗa a ji a birnin Madina duk sun musulunta.

Mus'ab ya samu shahada a yaƙin Uhud bai san wani jin daɗi na duniya ba tun bayan wanda ya yi bankwana da shi da ya karɓi Musulunci. A lokacin da ya cika bai mallaki ko rigar da za ta wadace shi a matsayin likkafani ba.

[276] Duba *Siyar A'alam An Nubala'* na Dhahabi 1/260 da kuma *Waƙafatun Ma'as-Sirah An-Nabawiyyah*, na Dr. Abdul Aziz Al-Humaidi 1/83.

Bayan da Allah ya yi ma Sahabbai buɗi aka samu wadatar rayuwa da yawa daga cikin su sukan tuna Mus'ab sai su fashe da kuka. Me ya sa? Sukan ce, Mus'ab ya wuce bai ci kome cikin ladar aikinsa ba. Muna tsoron kada ya zamo ladar jihaɗinmu ce muke cinyewa.

Allah sarki! Sahabbai ladarku tana wurin Allah. Mene ne kuka ci a wannan duniya, ku da ba ku san Fanka ba balle Iyakwandishin? Ba ku da ruwan Firijin, ba wutar lantarki. Babu sauran kayan alatu da jin daɗi?! Bayan duk azabar da kuka sha a hannun kafirai kun taimaki Manzo Allah, kun ba da duk abin da kuka mallaka wajen kafa addininsa. Wuta kuma Allah da kansa ya ce kun kubuta daga gare ta:

((وكنتم على شفا حفرة من النار فأنقذكم منها)) سورة آل عمران: ١٠٣

*"Kun kasance a kan gaɓar wuta sai (Allah) ya kuɓutar da ku daga gare ta"*[277]

Ya kamata Mus'abu ya zama abin koyi ga duk wani saurayi da yake cikin lokacinsa. Samun yardar Allah ya fi samun abin duniya. In da uwayensa sun san irin ɗaukakar duniya da ta lahira da ya samu a kan haƙurinsa da ba su takura ma sa yadda suka yi ba. Amma shiriya haske ne da Allah yake jefa shi a cikin zukatan waɗanda ya zaɓa daga cikin bayinsa. Ya Allah! Ka yi muna rabo da arzikin samun shiriya da tabbatuwa a kan ta har mai ƙarar da jin daɗi - kuma mai sadar da mummunai zuwa ga jin daɗi - ta cim mana, ta sadar da mu zuwa aljanna gidan ni'ima. Allahumma amin.

## 3.13 Tura ta Kai Bango

Wani abin ban sha'awa ga waɗannan bayin Allah shi ne, dukkaninsu suna jin zafin abin da ke faruwa ga 'yan uwansu ko da kuwa kome bai same su ba. Abin da zai nuna maka wannan shi ne, labarin Usmanu ɗan Maz'un

[277] Suratu Ali Imran: 103.

*Radhiyallahu Anhu* wanda aka hana shi shiga Makka sai da izini da garkuwar Walidu ɗan Mughirah. Bayan haka ya wayi gari yana shiga duk inda ya ga dama a cikin Makka babu wanda yake ce ma sa uffan albarkacin wannan garkuwa da Walid ya ba shi. Amma kuma zuciyarsa na ƙonuwa a kan abin da 'yan uwansa suke sha na wahala da azaba. Har sai ya fara tuhumar imaninsa. "Ta ya ya musulmi duk suke shan wahala, ni kaɗai ina sakewa? Kuma wai a kan garkuwar wani kafiri maƙiyin Allah da Manzo?" Haka zuciyarsa ta rinƙa cewa. Daga nan ya ɗauki alwashin rayuwa ba za ta ci gaba a haka ba. Ganin ba zai iya dakatar da azabar da ake yi ma musulmi ba sai kawai ya je wajen Walidu ɗan Mughirah ya ce ma sa, ya baban Abdu Shams! Duk yadda ake taimako ka yi, kuma na gode. Amma garkuwarka ka janye kawai ba ni buƙata. Walid ya ce, me ya faru? Ko wani ne ya tunzura ka, ko ya taɓa mutuncinka? Usmanu ya ce, sam. Kawai dai haka nake so, domin garkuwar Allah ta ishe ni. Abin ka da maƙetaci, sai Walid ya ce ma sa to, mu je can mahaɗar jama'a mana a daidai ɗakin Ka'aba sai ka shelanta ma mutane ka wadatu daga garkuwata. Usmanu ya shiga gaba Walid yana bin sa. Da suka je kuwa ba wani haufi Usmanu ya gaya ma jama'a cewa shi ya nemi Walid ya janye ma sa garkuwarsa.

Ba a ɗauki wani dogon lokaci ba sai 'yar gardama ta shiga tsakanin sa da Labidu ɗan Rabi'ata, wani fitaccen mawaƙi kuma baƙo a garin makka. Labid ya nemi agaji ga mutane. Wani ya ce ma sa ka yi haƙuri. Wannan na cikin wawayen gari waɗanda suka yi tawaye ma addinin iyaye. Usmanu ya ce da wa Allah ya haɗa nib a da kai ba! A nan ne fa rigima ta kaure. A cikin haka wani ya ɗauke Usmanu da mari sai da fuskarsa ta yi ja wur. Walid ya ce ma sa ka ga irin abin da nake gaya ma ka!. Ka halaka idonka a banza!!. Ka dawo kawai in sake yi maka garkuwa. A cikin fushi Usmanu ya ce ma sa, wallahi ba ni buƙata. Kuma ɗaya idona ma na da buƙatar abin da ya sami ‘yar uwarta saboda Allah.

Wannan yana nuna ƙarfin imaninsa da kwaɗayinsa ga lada. Babu shakka kuwa ya same ta. Domin ko bayan mutuwar sa Ummul Ala'i ta yi

mafarkin ta gan shi da wata ƙorama ta ruwa mai gudana. Sai ta faɗa ma ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Ya ce "wannan kyakkyawan aikinsa ne".[278]

Yanzu kam misali ɗaya ya rage mu kawo - domin mu yi wutiri - sai mu cira zuwa wani fasali. Mun tsawaita wannan bayani ne don masu hankali su san girman waɗannan mutane da Allah ya zaɓa ma Manzonsa. Mai tunanin cewa, wani abin duniya na karkata zukatan waɗannan bayin Allah daga bin Allah da Manzo lalle bai yi nazarin tarihinsu ba, ko kuma son zuciya da ƙin gaskiya sun ɗimauta shi.

## 7. Abdullahi Ɗan Mas'ud

A can baya mun ga yadda wannan Sahabi ya bayyana irin halin da ake ciki a garin Makka, in da ya ce babu wanda ya kuɓuta daga cikin musulmi daga shan azaba a hannun mushrikai. Da muka bincika sai muka ga shi ma ɗin kansa bai kubuta daga shan azabar ba.

Sanadiyyar musuluntar Abdullahi ɗan Mas'ud tana komawa ne ga tsarkin zuciyarsa da kyawon halinsa. A lokacin da yake yaro ƙarami Uƙbatu ɗan Abu Mu'ait ya yi jinga da shi akan kiwon tumaki. Wata rana yana kiwon sa sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* tare da rakkiyar Abubakar suka bi ta wurin sa. Manzon Allah ya ce ma sa, yaro ko ana samun madara a wurin ka? Sai ya ce, eh. Akwai madara bawan Allah. Amma fa ni ba kayana ne ba, kiwo aka ba ni. Sai Manzon Allah ya ce ma sa to, nuna ma ni tunkiyar da ba a fara barbararta ba. Ma'ana wacce ba ta ma san zancen ɗaukar ciki ba balle ayi maganar haifuwa da shayarwa. Sai ɗan Mas'ud ya je ya kamo ma sa wata 'yar budurwar tunkiya. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shafi hantsarta, nan take ta dararo da madara, suka ɗiba a wata ƙwarya suka

[278] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 7004. Duba kuma *Al-Asas Fis Sunnah* na Sa'id Hawa 4/2010-2012 da *Tarikh Al-Islam* na Dhahabi 1/112 da *Mausu'at As-Siyar* na Sallabi, shafi na 160-161.

sha suka koshi. Sai ya ce da hantsarta, ki dakata. Nan take sai madarar ta ɗauke. Ganin wannan abin al'ajabi ya sa ɗan Mas'ud ya biyo Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce ma sa koya min irin wannan karatun naka. Sai Manzon Allah ya yi murmushi, ya shafi kansa, ya ce, "Allah ya jiƙan ka. Ai kuwa kai yaro ne sa'ar ɗaukar karatu".[279] To, ka ji farkon haɗuwar sa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam.*

Abdullahi ɗan Mas'ud ya kasance mutum mai 'yan ruwa. Ma'ana yana da ɗan ƙaramin jiki sosai da kuma 'yan ƙananan ƙafafu. Amma wannan ƙanƙanin jikin nasa a cike yake da imani maƙil. Don kuwa shi ne mutum na farko da ya bayyana karatun Alƙur'ani a garin Makka bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Haka kawai kuwa a cikin taɗi wasu Sahabbai suka ce, jama'a fa Kuraishawa ba su taɓa jin an karanta ma su littafin Allah mai albarka a fili ba. Ko a cikin mu akwai wanda zai iya fitowa ya karanta ma su? Ɗan Mas'ud ya ce, ni zan yi. Suka ce ma sa, haba! Wane kai. Muna son wanda idan an taɓa shi a gidansu za a tada jijiya. Ya ce, ku dai bari ku gani. Sai kuwa ya je daidai Ka'aba in da kowa da kowa ke haɗuwa. 'Yan kulob suna ta ma-sha-a da shan giya. Sai ya fara tilawar *Suratur Rahman*. Da farko hankalinsu bai gaskata cewa Kur'ani ne yake karantawa ba saboda ba su tsammanin haka. Amma da suka ahamo sai suka bi shi da duka har suka yamutsa fuskarsa. Sahabbai suka ce, ka ga abin da muka ji ma ka tsoro kenan. Abdullahi ya ce, wallahi ban taɓa jin an cire min tsoron su ba kamar yanzu. Kuma ko gobe ma zan iya ƙara wa. Suka ce, a'a. Don Allah ka bari. Haka ma ya isa. Ai ko yanzu sun ji abin da ba sa so kuma suke fargaba.[280]

Daga nan mai karatu zai fahimci irin nau'in mutanen da suka amshi kiran Musulunci tun da farko. Zaɓaɓɓu ne, masu hankali, amintattu, waɗanda Allah ya gwada ma su karamomin habibinsa shugaban talikai *Sallallahu Alaihi*

---

[279] *Al-Bidaya Wan-Nihaya* na Ibn Kathir 3/32 da *Siyar A'alam An-Nubala'* na Dhahabi 1/465.

[280] *Usd Al-Gaba* na Ibn Al-Athir 3/385-386. Duba kuma *Mihnat Al-Muslimeen Fi Al-Ahd Al-Makkee,* na Suwaikit, shafi na 88.

*wa Sallam*. Suka kuwa bi shi bil haƙƙi suna masu neman yardar Allah. To, ya za a yi bayan sun share shekaru 23 suna ɗibar karatu da horo a kan imani ta hannunsa, sun sha wuya a kan addinin Allah, sa'annan sun yi jihadi tare da shi wajen tsayar da addinin, sun kashe iyayensu da danginsu akan haka, sai kwatsam su juya yi ridda! Wai don kawai suna ƙyamar wanda Manzon Allah ya naɗa ma su a matsayin magajinsa! Kuma ɗan uwansa na jini, sannan surukinsa? In ban da a ƙwaƙwalwa da tunanin 'yan Shi'a don Allah a wane hankali wannan tatsuniya za ta samu gurbin zama?!

### 3.14 Mushrikai Sun Ɓullo da Sabon Salo

### 6. Matakin Sulhu

Ganin duk irin matakan da suka ɗauka na ƙuntatarwa, takurarwa da azabtarwa ba su hana musulmi riko ƙan-ƙam ga addininsu ba, sai mushrikai suka sake dabara. A yanzu sun yarda su hau teburin sulhu da Manzon Allah kuma suna ganin da haka zasu yi galaba a kan sa. Kwamitin dattawa ya shawarta wanda ya kamata a tura ma sa, sai aka yi matsaya a kan Utbatu ɗan Rabi'ata ganin irin zalaƙar baki da yake da ita. Ga kuma kwarjini da cika fuska. Da Utbatu ya zo wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai ya fara da tambayar sa, shin Muhammadu kai da uwayenka wane ne ya fi? Domin mun san waɗannan ababen bautar namu su ma su suke bauta ma. Ka faɗa mana kai ka fi uwaye da kakanninka ne? Tsakanin kai da Abdullahi wa ya fi wani? Ka fi Abdulmuɗɗalib ko ka fi Hashim? Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ja bakinsa ya yi shiru bai ce ma sa kome ba. Sai ya ci gaba: "Muhammadu, wallahi a tarihin ƙasar nan ba mu taɓa ganin mutum shu'umi irin ka ba. Ka tarwatsa haɗuwarmu, ka zagi addininmu, ka tozarta mu a idon duniya. A yau ko ina maganar ka ake yi; ana faɗin wani boka ya bayyana cikin Kuraish, wani ɗan dabo ya ɓullo a garin Makka. A yanzu abu kaɗan ya rage ka sa mu ɗauki takubba mu karkashe kawunanmu". Duk abin nan da yake faɗi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana shiru yana sauraren sa. Sannan sai ya ci gaba: "Ya Muhammad! Ka faɗa mana idan kana da buƙatar kuɗi mu tara maka abin da kowa bai da irin sa. Ko kana sha'awar mata ne? Za mu sa 'yan matan gari su yi fareti ka zaɓi goma da kake so mu aura maka su a huta. Idan kuma ka san cewa, aljannu ne suke damun ka sai ka faɗi don mu tashi tsaye wajen nema maka magani".

Sai da Utbatu ya dasa aya ya nunfasa sannan sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce ma sa, Baban Walidu ka ƙare? Ya ce ma sa eh, bismillah, in ji daga gare ka. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi isti'aza ya fara karanta ma sa Alƙur'ani. Sai da ya karanta ma sa ayoyi 13 na

farkon Suratu Fussilat har ya kawo in da Allah yake cewa: *"Idan sun kau da kai to, ka ce na gargade ku a kan wata babbar tsawa irin wadda ta ci Adawa da Samudawa".*[281] Sai Utbatu ya zabura ya rufe bakin Manzon Allah, ya ce, tsaya! Don Allah haka ya isa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, to ka je ka yi nazarin abin da ka ji.

Ai kuwa fitar sa ke da wuya ya nufaci Kuraishawa sai suka rantse da Allah cewa Utbatu ya canja, bai dawo da irin fuskar da ya tafi ba. "Me ake ciki?" Suka tambaye shi. Ya ce, ba komai. Na je na same shi. "To, ya kuka yi?". Ya ce, wallahi na ji maganar da ban taɓa jin irin ta ba. Ba waƙa ba ce, ba sihiri ba, ba kuma bokanci ba. Wallahi kul-ba-daɗe wannan maganar tasa sai ta samu karɓuwa. Idan kuna bin shawarata ku fita batun sa ga abin da ya sa gaba. Idan duniya ta karɓi saƙonsa har ya ɗaukaka, ɗaukakar taku ce. In kuma wani abu ya faru da shi shikenan, Allah ya raka taki gona! Suka ce, haba! Wallahi tun daga nesa mun san ya sihirce ka. Utbatu ya ce ba ruwana. Ku je ku yi yadda kuka ga dama.[282]

Allah sarkin sarauta. Da Allah ya nufi wannan taliki da shiriya wannan ita ce babbar damarsa. Amma ita shiriya rabo ce min-indillahi. A cikin wannan labarin za mu ga irin haƙuri da juriyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Domin duk abin da Utbah ya faɗi na cin zarafi da zargi, har da tuhumar sa da ciwon aljanu bai fusata shi ba. A cikin mutuntawa ya ce ma sa, "Baban Walidu ka ƙare?" Game da tambayar da ya yi a kan iyayensa kuma sai Manzonmu ya lizimci kawaici bai ce ma sa kome ba. To, wane ne kuwa zai buɗa baki ya ce ya fi iyayensa?! A maimakon haka sai ya mayar da hankali ga isar da saƙonsa, in ya so shi ya yanke hukunci da kansa idan wannan saƙo ya ci ƙarfin addinin iyaye ko ba haka ba. Game da ababen kwaɗaitarwa da ya gitta ma Manzon Allah kuwa, ba fa da wasa yake yi ba. Iyakar gaskiyarsa shi da sauran masu faɗa a ji a garin Makka kenan. Da buƙatarsa ta duniya ce, zasu

[281] Suratu Fussilat, aya ta 13.

[282] *As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Ibn Hishamu 1/294 da *Al-Biɗayah Wan-Nihaya* na Ibn Kathir 3/68-69.

taru su biya ma sa ita. Amma ina ɗan aiken Allah ina waiwayar dauɗar duniya! Sau da yawa magadan Annabawa - tun da su ba ma'asumai ne ba - sukan faɗa a irin wannan tarko na su Utbah. Da zaran aka bai wa malami muƙami, ko aka buɗe ma sa hanyar samun kuɗi, sai ya shiga sharholiyar jin daɗi da aure-aure da hawan manyan ababen hawa da gina gidaje. Ta cikin wannan kuma sai ya manta da faɗin gaskiya, da yaƙar zalunci, da isar da saƙon Allah. Idan aka yi ɓarna sai ka gan shi yana kame-kame da kanikanci don ya gyara duniyar maɓarnata. Idan kuwa aka ce ma sa faɗi gaskiya, da ka kalli idonsa zaka ce, in baki ya ci dole ne ido su ji kunya. A wasu ƙasashen ma akan yi amfani da wasu ayyuka na Musulunci a zahiri a shigar da malami a cikin su don ɗauke hankalinsa daga tafarkin da ya ɗauko na isar da saƙon gaskiya.

Dole ne malamai magadan Annabawa su ci gaba da ɗaukar izna a cikin tarihin fiyayyen halitta. Ba kawai karantawa da fatar baki ba, a'a. Dole ne su sanya shi a gaba a matsayin abin koyi. Su kuma tuna zancen Annabi Yusuf *Alaihis Salam* da ya ce: *"Ya ubangijina! Haƙiƙa, zama gidan kurkuku ya fi soyuwa a gare ni a kan abin da suke kira na zuwa gare shi (na alfasha)"*. Allah muke roƙo ya datar da mu.[283]

Har wayau a cikin tarihin da muka gabatar mun ga tasirin Alƙur'ani ga zukata, da irin yadda gaskiya idan aka shimfiɗa ta take rufe karya. Irin su Utbah su ne suka ga gaskiya amma suka fandare ga barin ta. Kuma suka yi tsayin daka ba za a isar da ita a fili zuwa ga jama'a ba. Shi ya sa a ranar Badar Maɗaukakin Sarki duk ya share su, masu rabon shiriya kuma sai ya bari suka ji saƙon kuma suka karɓe shi. Ya Allah! Ka kare mu daga girman kai, ka yi ma na gamon katar da bin godaben shiriya miƙaƙƙe.

[283] *Fiƙh As-Sirah An-Nabawiyyah*, na Munir Gadhban, shafi na 169.

### 4.15 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi Baran-baran da Mushrikai

A karo na biyu, sai mushrikai suka sake naɗa kwamiti wanda ya ƙunshi mutane huɗu; Al-Aswad ɗan Abdilmuttalib da Walid ɗan Al-Mughirah da Umayyatu ɗan Khalaf da kuma Asi ɗan Wa'il. Sai aka ce su je su sasanta da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a kan su haɗu a bauta ma Allah tare da shi, shi kuma ya zo su bauta ma gumaka tare. A nan ne Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da *Kul ya ayyuhal kafirun..* Surar da ta raba ragi kwata-kwata tsakanin musulmi da mushrikai wajen sha'anin ibada.[284]

Da wannan ba ta samu ba sai suka ce, to, mu roƙi Muhammad ya ɗan sassafta ya rage wasu kalaman da yake yi, ko ya canja wasu ayoyi da ba su wofintar da iyayengijinmu. Suka aiki mutane biyar don su isar ma sa da wannan saƙo, cikin su har da Mikrazu ɗan Hafsu. Sai Allah ya sauko da aya ta 15 a *Suratu Yunus* in da ya yi watsi da wannan buƙata ta su.

Duk da haka mushrikai ba su haƙura da ƙoƙarinsu na ganin sun shawo kan musulmi su daina bin kiran Musulunci ba. Sai suka tashi wasu mutane guda biyu; Nadhru ɗan Al-Harith da Uƙbatu ɗan Abu Mu'ait suka je Madina don su gana da yahudawa ya'alla ko a samo bakin zaren yadda za a warware kiran Musulunci. Su kuma daman yahudawa ba wai gaskiyar ce suka jahilta

284 Wataƙila wannan zai tuna ma mai karatu ƙawancen 'yan Shi'ar Najeriya da kiristoci in da su - kiristocin - suka fara halartar bikin maulidi a tare da su a birnin Zariya tun shekarar 2012. Daga bisani a wannan shekara ta 2014 sai ko wane ɓangare ya shirya maulidi irin na ɗan uwansa. 'Yan Shi'a suka yi maulidin annabi Isah *Alaihis Salam* a yayin da su kuma kiristoci suka yi maulidin annabi Muhammad *Sallallahu Alaihi Wasallam,* duk da sunan haɗin kai da zaman lafiya. Wannan kwaɗon (ko kuma rummace) shi ne Allah ya hana Manzonsa ya amince da shi tsakanin sa da mushrikai. Addinin Allah hanya ɗaya ce rak. Ko a karɓe ta ko a bi layin jahannama. A kan wannan batu ne kuma Allah ya saukar da aya ta 41 a *Suratu Yunus* da kuma *Suratul An'am* (aya ta 56-57). Duba tafsirin Sayyid Kutb, *Fi Dhilal Al-Kur'an* 6/3991.

ba, sai dai taurin kai ne yake tattare da su. Daman sun baro ƙasa mai albarka ne; "Sham" suka tare a Madina bisa ga sifar garin da suka gani a cikin At-Taura cewa, Manzon Allah na ƙarshe zai kafa gwamnatinsa a cikin ta. Don haka, idan husuma ta shiga tsakanin su da larabawa sukan ce, Annabi ya kusa bayyana wanda zamu taimake shi mu yaƙe ku. Duk a tsammaninsu za a sake aiko Annabin ne daga cikin 'yan gidansu "Bani Isra'ila" kamar yadda aka saba. To, da Allah ya tashi aiko Annabinsa na ƙarshe sai ya kauce ma gidan nasu ya ɗauko Annabi Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam* daga gidan baffansu; jikan Isma'ila ba na Ishaƙa ba (dukkan su 'ya'yan Annabi Ibrahim ne *Alaihimus Salam*). Su kuma sai suka ce ba za su bi shi ba, domin da aka yi haka an raina gidansu. Mushrikai sun je neman fatawa a Madina gurin Yahud, kasancewar su masu ilmin littafin da Allah ya saukar. Suka ce, ku faɗa mana don Allah wai tsakanin mu da Muhammad wa yake bisa gaskiya? Kuma idan mu ne a kan gaskiya ku ba mu makarinsa. Ku faɗa mana tambayoyin da zamu yi ma sa na addini mu ƙure shi! Sai Yahudu suka ce da su, ai addininku ko alama ba a haɗa shi da nasa. Kun fi shi kusa da gaskiya. Sannan sai suka ba su tambayoyin ƙurewa da suka nema. Nadhru da Uƙbatu sun dawo da tambayoyinsu guda uku suna murna suka naɗa wani sabon kwamiti aka je aka tambayi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* a kan su. Sai ya ce da su ku bari sai gobe zan ba ku amsa. Gobe ta wuce, jibi ma haka. Har aka kwana goma sha biyar Jibrilu *Alaihis Salam* bai zo ba bale ya faɗa ma sa amsa. Da aka kai haka sai suka fara yi ma sa izgili suna cewa, daman mun san kai ba Annabin gaskiya ba ne. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya shiga damuwa matuƙa a kan haka. Daga bisani Allah ya saukar da Suratul Kahf wadda ta amsa dukan tambayoyinsu ɗaya bayan ɗaya, kuma Allah ya caji Manzonsa da cewar day a yi zai ba da amsa gobe ba tare da ya ce "in Allah ya so" ba, dalilin da ya janyo aka yi ma sa wannan jinkiri wajen ba shi amsa.[285]

Babban darasi a nan, su manyan bayin Allah ba ayi ma su sassafci a kan ƙananan abubuwan da suke karantar da mutane. A cikin karantarwar

[285] *Mausu'at As-Siyar* na Sallabi, shafi na 178-180.

Annabawa dole ne kowa ya sallama wa Allah; ya yarda shi bawa ne. Kuma ba abin da ya isa ya yi a cikin mulkin ubangiji sai bayan amincewar sa. Don haka kome musulmi yake son yi dole ne ya haɗa da cewa, in Allah ya so. Duk da gamsassun amsoshin da Allah da kansa ya ba mushrikai a cikin wannan sura har yanzu ba su amince ba. Suna nan a kan bakarsu; sai sun ga bayan addinin Musulunci.

### 3.16 Musulmi Sun Kaura Zuwa Habasha

Kamar yadda muka gani a baya, tura ta kai bango; haƙurin musulmi ya kusa ƙarewa, kuma babu wata alama da ke nuna mushrikai za su karkato su bari ayi addini ba tare da takura ba. Don haka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* sai ya fara tunanin mafita ita ce, musulmi su nemi wani waje da za su sarara; su yi bautar Allah a cikin natsuwa. A cikin watan Rajab na shekara ta biyar ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya umurci wasu kaɗan daga cikin Sahabbansa da su yi ƙaura zuwa ƙasar Habasha, ƙasar da teku ya raba ta da tsibirin larabawa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce da su, ku je can ku bauta ma Allah, domin sarkinsu adili ne; wanda bai bari a ci zalun kowa a ƙasarsa. Sun fita su goma mazaje. Huɗu daga cikin su suna tare da matansu, a ƙarƙashin jagorancin Usmanu ɗan Affan wanda shi ma yana tare da matarsa; Ruƙayya 'yar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*.

Da jin labarin fitar su sai mushrikai suka yi sauri suka tura runduna ta musamman don a dawo da su. Amma ina! Allah ya taimake su. Domin kuwa isar su ke da wuya sai suka tarar wani jirgi ya iso gaɓar teku yana jiran fasinja. Sai suka ɗauki hayar sa gaba ɗaya a kan rabin dinari, suka biya. Nan take aka sukwanya da su kafin isowar rundunar Kuraishawa aka tsallakar da su.[286]

[286] *Fath Al-Bari* 7/187-188.

Abin mamaki shi ne wannan ayari na farko da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tura su gudun hijira a Habasha, da ma babban ayari da zamu gani a nan gaba ba mutane ne masu rauni waɗanda ke shan wahalar ta sosai ba. Misali babu bawa ko ƙaramin yaro ko sauran waɗanda muka faɗi an azabta su a can baya cikin wannan ayari, sai fa ɗan Mas'ud. Amma a cikin su babu irin su Bilal da Suhaib da Khabbab da Ammar da makamantan su. Waɗanda ke cikin ayarin galibi manyan mutane ne masu dangi kamar Usmanu ɗan Maz'un da Zubair ɗan Awwam da Abdurrahman ɗan Auf da Abu Salamata da sauran su. Haka ma shi kansa jagoran tafiyar; Usmanu ɗan Affan. Daga bisani Abubakar Siddiƙ shi ma ya yi azamar zai cim ma su har sai da ya kai *Bark Al-Gimad* wani babban mutum ana ce da shi Ibn Ad-Dighinnah ya haƙurtar da shi, ya dawo da shi Makka da sharaɗin zai ba shi kariya. Dalilin da ya sa kenan wasu manazarta ke ganin ba an tura su ne kawai gudun hijira don su tsira da addininsu ba. A'a, akwai wannan dalili. Amma akwai kuma wasu manufofi na siyasa da na da'awa. Ma'ana dai ana son a isar da saƙon Musulunci zuwa ƙasar waje. Sannan kuma a samo bayanai da zasu taimaka wajen gano in da za a kafa daular Musulunci ta farko.[287]

Babu wani abin mamaki a cikin wannan idan muka yi la'akari da cewa, Habasha na cikin wuraren kasuwancin Kuraishawa, kuma a dalilin wannan hijirar ne sarkin ƙasar tare da wasu mutane da dama suka musulunta. Kuma ko bayan da aka samu aminci ta hanyar kafa birnin Musulunci a Madina Manzon Allah ya bar waɗannan mutane a can Habasha suna yaɗa addini har sai da aka zo yaƙin Khaibar a shekara ta shida bayan hijira. Abin da ya sanya da yawan waɗanda suka yi hijira ta biyu ba su halarci manyan yaƙoƙa irin su Badar da Uhud da Khandaƙ da Hudaibiyya ba saboda suna can a fagen yaɗa da'awa a waccan ƙasa.[288]

Bugu da ƙari kuma, Habasha ita ce ƙasa tilo wadda Annabi *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake so Allah ya ba shi damar yin ƙaura zuwa gare ta. Ko

[287] *Fi Dhilal Al-Kur'an* na Sayyid Kutb 1/29.
[288] *Al-Manhaj Al-Haraki Lis-Sirah* na Munir Al-Ghadban 1/67-68.

don yana da daɗaɗɗiyar masaniya ne a kan ƙasar? Ummu Aiman - wacce ta yi renon sa - 'yar ƙasar Habasha ce. Ko kuma don labarin sarki adili da ke mulkin can a wancan lokaci? Ko kuma don ƙasar tana kan addinin kirista ne? Duka waɗannan dalilai suna iya kasancewa. Domin Allah ya faɗa mana cewa, kiristoci sun fi kowa sauƙin jawuwa zuwa ga gaskiya idan suka ji ta kuma suka fahimce ta.[289] To, ko da yake can ɗin ne Annabi yake so, amma kuma Maɗaukakin Sarki ba haka ya tsara ba. Hijirar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da kafa gwamnatinsa ta farko gwanin sarki Allah ya tsara su ne a Madina, kuma har ya wasafta wannan birnin a cikin At-Taura, Yahudu suka tare can suna dakon zuwan sa. A can ne Allah ya kai Manzonsa, Yahudu suka yi iya jayayyar da suke iyawa da ƙulle-ƙullen makircinsu, amma Allah ya rinjayar da Manzonsa a kan su. Daga ƙarshe aka kore su ga baki ɗaya daga cikin ta da ma kewayenta.

### 3.17 Yanayi ya Canja a Makka,'Yan Gudun Hijira Sun Dawo

Bayan tafiyar wannan ayari na farko da muke magana a kan sa, kwatsam sai aka samu sassafcin yanayi a birnin Makka. Domin kuwa jarumawa biyu daga cikin waɗanda ake tsoro Allah ya karkato da zukatansu sun karɓi Musulunci. Su ne; Sayyidi Hamza - baffan Manzon Allah - da Sayyidi Umar ɗan Haɗɗabi. Don haka ala-tilas aka fara sakar ma musulmi mara, har ma ya kasance a yanzu suna sallah a fili a cikin masallaci. Jin wannan sauyi da aka samu sai ayarin Usmanu ɗan Affana - bayan watanni uku da suka share a can - suka juyo suka dawo gida. Amma kuma tsugunnen dai ba ta ƙare ba. Zamu yi magana a kan musuluntar waɗannan jarumawa da muka faɗa, sannan mu koma kan abin da ya sake tilasta yin hijira ta biyu zuwa Habasha.

[289] Suratul Ma'ida: 82.

### 3.18 Musulunci ya Samu Garkuwa

Bayan tafiyar Muhajirai na farko su goma sha huɗu babu abin da mushrikai suka ƙara a kan musulmi sai ta'addanci da ƙetare iyaka. A cikin haka ne Wata rana Abu Jahali ya tafka irin ta'asar tasa; ya kalli ƙwayar idon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zage shi, kuma ya yi ma sa izgili, ya yi ƙoƙarin muzanta shi. Fiyayyen halitta wanda ya fi kowa haƙuri ya shuɗe abin sa bai ce ma sa uffan ba. Ashe duk abin nan da ke faruwa a bisa kunnen wata kuyanga 'yar gidan Abdullahi ɗan Jud'an.[290] Sai wannan kuyanga ta kwashe labarin duk abin da ya faru ta faɗa ma Hamza, wanda yake baffan Manzon Allah ne kuma abokin renon sa, tun da yake nonon da Hamza ya saki shi Manzon Allah ya kama. Hamza ya ce ma ta, tsakaninki da Allah a gabanki aka yi haka? Ta ce, ƙwarai kuwa. Nan take jinin Hashimawa ya motsa a cikin jikinsa, ƙasa ta kasa ɗaukar ƙafafunsa. Bai zarce ko ina ba sai majalisin kafirai in da Abu Jahali yake baje kolinsa. Da isar Hamza, ga shi saurayi mai ƙarfi, kuma mafi kwarjinin samarin Makka. Bai tsaya wani dogon bahasi ba sai ya cira bakarsa ya watsa ta a kan Abu Jahali sai da ya yi ma sa mummunan rauni. Sannan ya ce, ya za ka zage Muhammadu ina a kan addininsa?!

Allahu Akbar. A lokacin da Hamza ya furta wannan kalami bai ƙudure a zuci abin da ya faɗi da baki ba. Amma kuma ko da ya dawo hayyacinsa bayan fushi ya sake shi, sai ya sake nazarin abin da ya faɗa. To, mene ne illa idan na bi addinin Muhammadu amintacce wanda na tabbata Allah ya aiko shi, ba ƙarya yake yi ba? Wannan duka mai zafi da Abu Jahali ya sha watakila shi ne karo na farko da ya fara samun irin sa. Abin da ya sa da rikici ya ɓarke a tsakanin danginsu biyu, ya ce ku dakata. Wallahi ni ne na jawo jidali, don na ci mutuncin ɗan yayansa.[291]

[290] Shi ne wanda Manzon Allah ya taɓa sa hannu ga wata yarjejeniya a kan 'yancin masu rauni a gidansa.

[291] *Mukhtasar Siratin Nabiy*, na Sheikh Muhammad ɗan Abdulwahhab, shafi na 90.

Labarin dukan da Abu Jahali ya sha a hannun Hamza ya rinƙa yaɗuwa a cikin jama'a, yana tafiya kafaɗa da kafaɗa da labarin musuluntar sa. Wannan ya kashe jikin Kuraishawa matuƙa. Kwana uku bayan haka, sai kuma suka ji Umar ɗan Haɗɗabi shi ma ya musulunta.

Game da musuluntar Umar, wani al'amari ne na Allah da ya zo a matsayin ijaba ga du'ain Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Domin kuwa Khabbab ɗan Al-Arat ya ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana addu'a yana cewa, "Ya Allah! Ka ƙarfafi addininka da wanda ka fi so a cikin biyu; Umar ɗan Haɗɗabi ko Abu Jahali ɗan Hishamu". Umar saboda ƙarfin jiki da jaruntarsa, Abu Jahali kuma saboda ƙarfin iko da sarautarsa. Har zuwa ranar da ya musulunta, Umar bai da wani sassafci ko ɗan kaɗan ga musulmi. Amma albarkacin wannan addu'a take Allah ya sanyaya zuciyarsa bayan da ya tarar da ƙanwarsa tare da mijinta suna karatun Alƙur’ani a ƙarƙashin kulawar malamin da aka haɗa su da shi; Khabbab ɗan Al-Arat. Da musuluntar sa, abu na farko da Umar ya yi shi ne, ya je wurin kawun nasa "Abu Jahali" ya ƙwanƙwasa kofarsa. A cikin lalama da fara'a ya ce ma sa "Maraba lale. Ɗana, yau me ya kawo ka wurina a wannan lokaci"? Umar ya ce, na zo ne in sanar da kai na bi Allah, na bi Muhammad Manzon Allah! Da jin haka, a fusace, Abu Jahali ya tura ma sa ƙofa ya haɗa ma sa da zagi mummuna.

Bayan haka kuma sai Umar ya tambaya, wane ne baki abin magana wanda ya fi kowa yaɗa labari a garin Makka? Aka ce ma sa wannan ai sai Jamil Al-Jumahi. Abdullahi ɗan Umar ya ce, sai na bi shi don na ga abin da zai faru. Wallahi bai gama faɗa ma Jamil saƙon ba sai da ya zabura ya ruga zuwa ƙofar masallaci. Ya kuwa ƙwala ihu yana cewa, jama'a ku saurara! Umar fa ya karkace!! Shi kuma Umar yana bin sa yana cewa, ƙarya yake yi. Na dai bi hanyar gaskiya. Ba da jimawa ba kuwa aka yi ma Umar taron dangi, suna duka yana dukan su. Amma da yake sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi sai da suka kai shi kwance. A nan ne ya ce, wallahi da mun kai mutane 300 a Musulunci,

da Makka ta yi ma ku ƙamshin ɗan goma don da mun fitar da ku daga cikin ta ko kuma ku ku fitar da mu.

Daga wannan lamari ne musulmi suka fara samun kan su, aka daina muzguna ma su. Domin kowa yana tsoron haɗuwar sa da waɗannan jarumawa guda biyu idan yana shi kaɗai. A hankali ma sai suka fara fitowa masallaci suna yin sallar su ba tare da fargaba ba. Wannan shi ne labarin da 'yan gudun hijira na farko suka ji suka ɗauka gari ya yi sanyi suka dawo.

To, ya aka yi musulmi suka sake yin hijira a karo na biyu?

## 3.19 Makirci na Karshe: Manzon Allah da Danginsa

## Sun fuskanci Ɗaurin Ta-la-la

Bayan da duk ƙoƙarin Kuraishawa na daƙile addinin Allah ya ci tura Musulunci sai ci gaba da yaɗuwa yake yi a birni da ƙauye. Ga kuma musulmi sun haƙurce duk irin wahalhalun da ake ba su. Sannan kuma ta fuskar hujja an kasa i ma su, an kuma kasa sa su sassafta. Kawai sai suka sake hawa kan teburin shawara suka yi matsaya a kan cewa, babu wata mafita sai dai a kashe Manzon Allah! Da labari ya kai ga Abu Ɗalib sai ya tara duk zuriyyar Abdulmuɗɗalib ya sanar da su abin da ake ciki, kuma ya nemi su ɗaura ɗamarar kariyar sa har in da ƙarfinsu ya ƙare. Musulmi da wanda ba musulmi ba daga cikin danginsa suka ɗauri aniyar yin haka. Musulmi sun yi saboda Allah, kafirai kuma saboda kishin dangantakarsu. Wannan sai ya haifar da yankewar alaƙa tsakanin su da sauran mutanen Makka. Kuraishawa suka rubuta taba'a suka liƙa ta a jikin Ka'aba cewa, daga yau ba aure da auratarwa, ba saye da sayarwa, babu rahama babu tausayi tsakanin su da ‘yan Abdilmuttalib har sai sun miƙa Muhammad an yanke ma sa hukuncin kisa! Tsarki ya tabbatar ma Allah!

Wasa-wasa fitina ta fankama. Dangin Annabi da Sahabbansa suka shiga wani mawuyacin hali. Ba a magana da su, ba a ciniki ko auratayya da su, ba a bari wani tallafi ko taimako ya je hannunsu. Idan aka kawo haja daga ƙasashen waje kuma ba a bari su shiga kasuwarta ballantana a sai da ma su. Duk a cikin

haka kuma kullum dare sai an sauya ma Manzon Allah wurin kwanciya fiye da sau ɗaya don jin tsoron a kawo ma sa farmaki. Shekara uku cif wannan zalunci yana gudana a kan su. Abincin da za su ci ma sai da ya gagare su. Ana haka, sai Allah cikin ikonsa ya zo da mafita. Wani bawan Allah ana ce da shi Hishamu ɗan Amr daga gidan Banu Hashim ya shirya juyin mulki kan wannan zalunci. Nan take ya nemi mutane masu hankali irin sa daga ƙabilu daban daban. Ya gana da su a asirce kuma ya samu mutane huɗu da suka amince a kan cewa za su yi tawaye tare da shi a kan wannan zalama. Suka jagorantar da Zuhairu ɗan Abu Umayyata daga "Banu Makhzum" gidan su Abu Jahali wanda kuma yake ɗan gwaggon Manzon Allah ne "Atika". Sai da Zuhairu ya dubi lokacin haɗuwar su gaba ɗaya, sai ya zo ya yi ɗawafi sannan ya yi shela: "Ya ku jama'a! Wane irin zalunci ne wannan? Muna ci, muna sha, muna sa suturar da muke so amma 'yan uwanmu 'yan gidan Hashim suna halaka, yunwa tana son ta ga baya gare su?!" Hankula kuwa gaba ɗaya sai suka karkata gare shi. Sai ya ci gaba: "Wallahi ba zan zauna a wurin nan ba sai an yaga wannan takarda ta zalunci da keta alfarmar zumunta". Sai Abu Jahali ya yi fararat ya ce, "ƙarya kake yi wallahi. Ba a yaga ta". Zam'atu ɗan Al-Aswad ya miƙe daga can wani ɓangaren masallaci - daman haka aka shirya - ya ce ma Abu Jahali, ai kai ne maƙaryaci wallahi. Ko can farko da aka rubuta ta ba mu amince ba. Yana gama faɗin haka sai Abul Bukhturi ya tashi - shi ma yana cikin kwamitin - ya ce, wallahi Zam'atu ka yi gaskiya. Ba da ra'ayinmu aka rubuta ta ba. Shi ma Mut’imu ɗan adiy ya tashi tsaye, sai Hishamu shi ne ya zo na ƙarshe. Duk suka muzanta Abu Jahali, suka ƙarfafa a yaga wannan muguwar takarda. Shi kuma Abu Jahali bai samu ko mutum ɗaya da ya goyu bayan sa ba. Sai kawai cewa ya yi: "Wannan da gani ka san abu ne da aka shirya. To, ba za mu yarda ba". Mut’imu ya nufaci Ka'aba kawai ya ɓallo wannan azzalumar takarda. Ko da aka ɗauko ta duk gara ta cinye kalaman zalunci da yanke zumunta da ke cikin ta, amma ta bar wuraren da sunan Allah ya ke. Allahu Akbar! Ko wannan kaɗai ya ishe su wa'azi in da akwai rabo. Amma ina! Mai rabon shan duka...

A cikin wannan darasi akwai ababen lura da dama. Sau da yawa Allah yakan taimaki Musulunci ta hannun wanda ba musulmi ba idan ya ga dama kamar yadda waɗannan mushrikai su biyar suka shirya wannan tawaye har musulmi suka samu sa'ida. Musulmi kuma suna iya cin gajiyar aikin alheri ko ya fito daga wurin kafiri. Shi kuma zalunci duk lafiyayyen hankali yana ƙyamar sa. Abin da duk ya fi wannan ban sha'awa shi ne irin tarbiyyar Sahabban Annabi da bin umurni da suke yi da tsayawa kan doka. Kana tsammanin a cikin su ba wanda zai iya bin dare ya kashe shugaban wawayen nan "Abu Jahali" duk a huta? Ko ɗan Karamin matashin cikin su "Ali ɗan Abu Ɗalib" da bai wuce shekaru 15 ba a wancan lokaci yana iya wannan. Ballantana akwai jarumawa manya irin su Hamza da Umar da sauran su. Me ya hana su yi haka? Saboda ba a ba su umurni ba. Irin wannan shawara da wani daga cikin su ya yi gabansa ya yanke ta zai yiwu ya samu nasarar gamawa - cikin dare - da Abu Jahali ko ma duk wani arne irin sa. To, amma kuma me zai biyo bayan haka? Shi ya fa daman mai haƙo ba ya ta da hannu. Don haka, haƙurin shi kaɗai ne mafita. Kuma albarkacinsa duniya ta tausaya ma su, ta tsani shugabannin Makka saboda nuna halin rashin imani da suka yi. Mutane da dama da suke zuwa aikin Hajji suna yaɗa labarin a sauran garuruwa sai ana cewa, lallai wannan addinin gaskiya ne. In ba haka ba wa zai ɗauki wahala kan sa har ya shiga wannan hali! A daidai wannan lokacin ne ƙabilun Gifara da Dausu da Azd-Shanu'a - ta Yemen - da mutanen Najran da Habasha suka yi ta shiga Musulunci. To, ina amfanin a ta da fitina a wannan lokaci tun da babu cikakken shirin tunkarar ta! Wanda Allah ke wa faɗa ba ya faɗa.

Da yawan zaluncin da ake yi mutane ba su amince da shi ba a cikin zukatansu. Idan aka samu dalili sai su yi fito-na-fito da shi. Don haka ba a yanke hukunci a kan mutane ga abin da ba su suka yi shi ba. Ai ka ga duk a cikin talakawa – kai har da manyan gari – babu wanda ya fito fili ya goyu bayan Abu Jahali. Su kuma Banu Hashim da Banul Muttalib albarkacin wannan haƙuri nasu Allah ya ba su kaso daga cikin humusin ganimar yaƙi.

Saɓanin Banu Abdishams da Banu Naufal. Duk dangi ɗaya ne amma ba su taimaki Annabi ba. Haɗewa suka yi da kafirai. Sai aka fitar da su daga cikin wannan rabo.[292] A ranar Khaibar waɗannan gidajen biyu kaɗai Annabi ya raba ma wannan kaso na ganima. Da aka tambaye shi sai ya ce: "ba su taɓa rabuwa da mu ba a zamanin Jahiliyya ko na Musulunci".[293]

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kasance yana tuna "Muhassab" wurin da mushrikai suka haɗu don cim ma wannan muguwar matsaya. Kamar yadda ya ce a ranar da zai isa aikin Hajji, aka tambaye shi, a wane gida za mu sauka gobe? Sai ya ce, Aƙilu ya bar mana sauran gidaje ne a Makka? Za mu dai sauka a Muhassab, can in da Kuraishawa suka haɗu a kan kafirci su da Banu Kinanata.[294]

### 3.20 Musulmi Sun Sake Komawa Habasha

A can baya mun ga yadda musulmi suka dawo daga ƙasar Habasha suna cike da fatar samun sassafci bayan da suka ji labarin cewa, manyan jarumawa guda biyu sun shiga Musulunci. To, amma ashe abin ba haka yake ba. Domin kuwa Kuraishawa sun sake jan ɗamara domin yaƙi da musulmi, kuma sun fito da wasu sababbin hanyoyi na azabta su. Bayan dawowar su ne kuma aka ɓullo da matakin da muka gama faɗi na ɗaurin ta-la-la. Abin da ya sa dole aka sake umurnin su su koma Habasha. A wannan karon ma sai adadinsu ya karu daga 14 zuwa sama da 100. (Mazaje 82 da mataye 18, tare kuma da wasu ƙananan yara daga cikin 'ya'yansu). Kamar wancan karon dai ayarin musulmi a cike yake da makusantan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* waɗanda suka haɗa da: ɗan baffansa Ja'afar Abu Ɗalib, da Usmanu

[292] Duba *Tafsir Al-Kur'an Al-Azim*, na Ibn Kathir a wurin ayar ganima ta Suratul Anfal: 41 2/312.
[293] *Sunan Abi Dawud*, hadisi na 2980.
[294] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3058.

ɗan Affan jikan Baidha'u gwaggon Manzon Allah tare da matarsa Ruƙayyatu 'yar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*.

Kuraishawa sun damu matuƙa da sake yin hijira. Kamar dai suna ganin dole ne musulmi su zauna su yi ta jurewa duk wahala da azabar da suke ba su, amma ba su da haƙƙen su yawata a cikin ƙasar Allah mai faɗi in da za su samu 'yancin kansu. Nan take suka shirya tafiyar wakilai guda biyu don su gana da sarkin Habasha wanda zai ba su damar ingizo ƙeyar musulmi su dawo da su gida a tunaninsu. Wakilan da aka tura su ne: Amru ɗan Al-Ass da Abdullahi ɗan abi Rabi'ata waɗanda ake ganin sun ƙware wajen iya hulɗar jakadanci kuma sun iya bakinsu wajen isar da saƙo. Sannan aka shirya kyaututtuka na musamman zuwa ga sarki da duk fadawa da 'yan majalisarsa a matsayin cin hanci don a samu haɗin kansu. Sun bayar da kyautar fatu waɗanda aka yi jimar su ga ko wane ɗaya daga cikin 'yan majalisa da fadawa kafin su kai ma sarki nasa. Da suka samu ganawa da sarki suka gabatar masa da tasa kyauta sai suka faɗa masa cewa, sun zo ne suna wakiltar al'ummar ƙasarsu kuma sun kawo ƙarar 'ya'yansu da suka fanɗare ma su, suka fice daga addininsu kuma ba su shiga addinin sarki ba. "Bayan haka, sun raba kanmu, sun zagi ababen bautarmu, sun wautar da iyayenmu. Don haka, buƙatarmu ita ce, sarki ya ba mu izini mu ingiza ƙeyarsu mu koma da su gida mu ɗauki matakin da ya dace a kan su tun ba su ɓata ma sarki ƙasarsa ba". In ji wakilan.[295]

Da yake daman an shirya da sauran 'yan majalisa sai duk suka goyu bayan su, suka nemi sarki ya yi abin da suke so ba tare da ya saurari waɗannan mutane ba. Amma Najashi mutum ne mai hankali, kuma adili. Sai ya ce, wallahi ba za a taba yin haka ba. Mutane su baro ƙasarsu ta gado, su ƙaurace ma iyayensu, su zaɓi ƙasata da zama cikin jama'ata sannan in kore su ba tare da ko wane irin yankan hujja ba! Sannan ya yi umurni aka kira su don ya ji ta bakinsu.

[295] Kafiri a kullum cikin wauta yake. Sun manta cewa, sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi!.

Cikin wakilan Kuraishawa ya ɗauki ruwa sosai da wannan mataki da sarki ya ɗauka. Domin sun san cewa, idan ya saurare su ya ji irin halin da aka sa su babu gaira babu dalili lalle ne zai tausaya ma su.

Kafin su zo wurin sarki, Sahabbai sun yi matsaya a kan shugabantar da Ja'afar ɗan Abu Ɗalib don ya zama mai magana da yawunsu. Kuma sun yi alƙawarin ba za su faɗa ma sarki ƙarya ba a cikin duk abin da ya tambaye su. Da zuwan su sarki ya tambaye su, wane irin addini ne kuke yi wanda ba shi ake yi a ƙasarku ba, ba kuma shi muke yi a nan ba, sannan kuma kowa bai san shi ba? Ja'afar ya kada baki ya ce, Allah ya daɗe ran sarki. Mu dai a can da a ƙasarmu cikin duhu muke. Muna bautar gumakan da muka sassaƙa da hannayenmu, muna cin mushe, muna aikata alfasha, muna yanke zumunta, muna cutata ma maƙwauta, kuma duk wanda yake da ƙarfi sai ya ci zalun wanda bai kai shi ba. Muna haka, sai Allah ya aiko mana Manzo a cikinmu. Duk mun san shi, mun san matsayinsa da asulinsa. Mun kuma tabbatar da gaskiyarsa, nagartarsa, amanarsa da kamun kansa. Wannan Manzo sai ya kira mu zuwa ga kaɗaita Allah da bauta, ya ce mu daina bin gumakan da iyayenmu suka kasance suna bauta. Ya ce kuma mu riƙe gaskiya da amana, mu sada zumunta, mu kyautata ma maƙwauta, mu daina cin ƙazanta kamar jini da mushe, mu daina ayyukan alfasha da shedar zur da cin haƙƙin maraya da yin kazafi ga mutanen kirki. Sannan ya umurce mu mu bauta ma Allah shi kaɗai ba tare da mun sanya ma sa abokin tarayya ba. Ya umurce mu mu yi sallah, mu ba da zakka, mu yi azumi. Allah ya taimaki sarki, a kan haka ne muka bi shi, muka halalta abin da Allah ya halalta, muka haramta abin da ya haramta. Kawai sai sarakunan garinmu suka tsane mu, suka kafa mana ƙahon zuƙa. Ba kuma irin fitina da azabar da ba su yi mana ba a kan wai sai mun koma cikin duhu bayan Allah ya yi walƙiya mun gane hanyar gaskiya. Ganin haka ya sa muka kamo hanya zuwa garinka muna neman mafaka don mun ji labarin kana adalci, ba ka cuta.

Sarki ya kaɗa kai sannan ya ce, to, kun zo da wani abu cikin abin da yake karanta ma ku? Ja'afar ya ce, ƙwarai kuwa. Sannan sai ya karanta ma sa

farkon Suratu Maryam, in da Allah ya yi bayanin mahaifiyar Annabi Isah *Alaihis Salam* da nagartar iyayenta da tarihin haifuwarta da ibadarta, har zuwa haifuwar Annabi Isah *Alaihis Salam* da yadda ya fitar da ita kunya bayan Yahudawa sun zarge ta. Ko da Ja'afar ya gama karatu sarki da malamansa duk sun jiƙe gemmansu da hawaye saboda daɗin karatu da tasirinsa. Kai har littattafansu duk sun jiƙe sharkaf da hawayensu. Sarki ya ce, wallahi wannan littafi naku mafitarsa ɗaya ce da wanda Annabi Musa *Alaihis Salam* ya zo da shi. Kuma ba zan taɓa bari a cutata maku ba. Ku je duk in da kuke so ku zauna a cikin ƙasata na yi maku izini. Ku kuma ku tafi da kyautarku, ba na buƙata, domin ni ban bai wa Allah cin hanci sa'adda ya ba ni mulkin nan ba.[296]

Karya fure take yi, ba ta 'ya'ya. Wani hani kuma ga Allah baiwa ne. Sara da sassaƙa ba sa hana Gamji tofo. Jekadun Kuraishi a nan sun yi ma addinin Musulunci hidima ba su sani ba. Wa zai buɗe ma musulmi fadar sarki Najashi a wancan lokaci har su isar ma sa da saƙo in ba don wannan dalili ba? Daga wannan zaman ne Najashi ya ƙulla alaƙa da musulmi kuma ya rinƙa sauraron karatun Alƙur'ani, har ma ya samu alaƙa ta kai tsaye da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*; yana aike ma sa da saƙonni, shi ma kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yana yi ma sa aike. A dalilin wannan alaƙar tasu ne ma ya sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya umurce shi ya ɗaura ma sa aure da Ramlatu matar da Ubaidullahi ɗan Jahsh ya bari bayan cikawarsa a can. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tausaya ma iyalin wannan bawan Allah kasancewar sa mutumin kirki, ita kuma 'yar babban gida ce a garin Makka, domin diyar Abu Sufyana ce, amma ta bar jin daɗin duniya ta bi mijinta zuwa Habasha don su tsira da addininsu. A cikin auren ta kuma har wayau akwai wata manufa ta siyasa. Muna gane wannan in muka san cewa, Abu Sufyana, wanda tuni ya ɗaura ɗamarar yaƙi da addinin Musulunci jikinsa ya yi sanyi matuƙa da jin cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɗaura aure da ɗiyarsa. Najashi ya yi ma ta

[296] *Musnad Ahmad*, hadisi na 1740.

sadaki a madadin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* irin sadakin 'yan alfarma; dirhami 4000.

Duk da yake yanayin jama'arsa bai ba shi damar bayyana Musuluncinsa kowa ya sani ba, amma Najashi ya musuluntar da iyalansa da amintattunsa, kuma ya bai wa musulmi dama sun yaɗa addini a cikin ƙasarsa. Muhimmin darasi a cikin wannan shi ne cewa, da yawa Allah yakan yi amfani da rundunar ƙarya don ya taimaki gaskiya. Dubi yadda Allah ya juyar da makircin Kuraishawa don bice hasken addini ya koma babban makami na taimakonsa da bunƙasa shi. Sun yi amfani da duk hanyoyin da suke iyawa har da ba da cin hanci. Amma kuma sai Allah ya taimaki gaskiya ta hanyar wannan yunƙurin nasu. Ta ɓangaren musulmi kuma muna iya lura da zaɓen Ja'afar da aka yi a matsayin wakilin musulmi da irin hikimar da ke tattare da jawabinsa da ma surar da ya zaɓa don karanta ma Najashi. Aikin da ake son ya yi kyau kuwa sai an zaɓa ma sa gwanayensa.

A lokacin da ajali ya cim ma Najashi, Sayyidi Jibrilu *Alaihis Salam* ya sanar da Manzon Allah, shi kuma ya sanar da musulmi a Madina, sannan Manzon Allah ya shiga gaba, suka yi sahu-sahu suka yi ma sa sallar jana'iza ta wanda ba ya kusa "Salatul Ga'ib".[297]

Wani darasi da bai kamata mu shuɗe a kan sa ba a daidai wannan gaɓar shi ne, fatawar da shehin Musulunci ɗan Taimiyya *Rahimahullahu* ya gina a kan wannan ƙissa. Fatawar ta duba cewa, su waɗannan da suka yi hijira zuwa Habasha suna can ne aka ƙara yawan raka'oin sallar azahar da la'asar da Isha'i suka koma huɗu-huɗu, a yayin da ita kuma sallar magriba aka ƙara ta ta koma raka'a uku bayan a da dukkansu raka'oi bi-biyu ne. Ya ce, kuma ba mu ga in da aka samu cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya umurce su da su rama sallolin da suka yi kafin su san da wannan ƙari ba. Ya ce, daga nan

[297] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 1333 da 3877. Duba kuma: *Usd Al-Gaba* 1/99 da *Al-Isaba* 1/109.

muke fahimtar cewa, jahiltar wasu lamurran addini idan ba da gangan ba ne, ba ta wajabta uƙuba ga mutum ko ɓacin ibadarsa.[298]

**3.21 Jarrabawa ta Kai Maƙura**

A daidai lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* da Sahabbai suka fita daga waccan jarabawa ta ɗaurin ta-la-la da muka faɗa sai kuma wata sabuwar jarabawa ta sabka a gare su. Wannan jarabawa ita ce rasuwar manya-manyan mutane biyu da suka zamo jigogi ga addinin Musulunci; Abu Ɗalib da Nana Khadijah. Sun rasu a cikin mako ɗaya, a ƙarshen shekara ta 10 daga farkon Annabta.[299] Shi dai Abu Ɗalib kamar yadda aka sani ya kasance mai cikakken goyon baya da ba da gudunmawa da kariya ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Kuma duk wata barazana da take fuskanto Manzon Allah to, yakan tare ta ne bil-haƙƙi har sai in da ƙarfinsa ya ƙare. Ita kuma Nana Khadija ita ce uwargida mai kwantar da hankali da samar da natsuwa gare shi ta hanyar so da ƙauna da take yi masa da kyawawan shawarwari managarta da take ba shi, ga kuma amfani da kuɗinta wajen ci gaban addini. Babu shakka mutuwarsu ta samar da wani giɓi mai girma a cikin zuciyar ma'aiki. In da ma ace dukan su sun cika a kan imani, to da lamarin mai sauƙi ne. Domin makomarsu abin farin ciki ce. Ita dai Khadija daman tun da farko ta musulunta, kuma ta ci gaba da yin sallah da sauran al'amurran neman kusanci da Allah har ma Allah ya aiko Jibrilu *Alaihis Salam* da saƙo zuwa gare ta ta hannun mijinta cewa, an yi ma ta tanadin gida a mafi ƙololuwar aljanna. Amma shi Abu Ɗalib har zuwa lokacin mutuwarsa ya kasance mai imani da gaskiyar Manzon Allah a zuciyarsa, kuma yana furta haka sau da yawa a gaban jama'a. Amma kuma bai cika sauran sharaɗin musulunta ba, shi ne; miƙa wuya ga Manzon Allah da janyuwa zuwa ga

---

298 *Majmu'u Fatawa Ibn Taimiyyah*, 22/43.

299 Duba *Fathul Bari* na Ibn Hajar, (7/194).

umurninsa. A lokacin da ya zo cikawa sai mafi kusancin mutane daga cikin kafiran abokansa suka zo duba shi a daidai lokacin da Manzon Allah yake rungume da shi yana rarrashinsa ya shiga Musulunci. Su kuma sai suka rinƙa nuna masa cewa, idan ya yi haka zai yi abin kunya ne, don kuwa da tsufansa don ya ga mutuwa ya saki addinin mahaifinsa Abdulmuɗɗalib. Daga ƙarshe ya yi wata waƙa mai ban tausayi wadda a cikin ta yake nuna cewa, kawai abin da zai hana shi ya faranta ran Manzon Allah ta hanyar furta kalmar shahada shi ne gudun a ɗauka cewa, ya yi raki ne. Allahu akbar! Babu shakka Musulunci rabo ne. Miyagun abokai kuma hatsari ne. Sannan Allah ba ya son Musuluncin da za a yi shi don daɗaɗa ran waninsa, ko da kuwa wanin nan fiyayyen halitta ne *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* yana cewa:

((وما أمروا إلا ليعبدوا الله مخلصين له الدين حنفاء..)) سورة البينة: ٥

> *"Ba wani abu ne aka umurce su da yi ba sai kawai su bauta ma Allah suna masu tsarkake ma sa addini, masu kauce ma Shirka..".*[300]

Don haka, duk wanda zai yi addini ba don Allah ba ya yi a banza, kuma Allah ba zai karɓa ma sa ba. Karin darasi a nan, idan kana son rahamar Allah to, ka miƙa wuyanka ga reshi. Idan fiyayyen halitta bai iya shigar da baffansa Abu Ɗalib a cikin aljanna ba, ba wanda zai iya shigar da kai ita duk yadda kake son sa. Aljanna kayan Allah ce, kuma ya sa ma ta sharaɗi; babu mai shigar ta sai mai imani. Kamar yadda bakin da bay a ƙarya ya faɗa.[301]

Wani abin lura a nan shi ne yadda Allah yake jujjuya musulmi daga wata musiba zuwa wata. Kada ka yi tsammanin wai, masoyan Allah ba su gamuwa da jarrabawa. Bil-hasili ma ita jarabawa ta fi sauka a kan masoyan

[300] Suratul Bayyina: 5
[301] *Al-Hijrah Wa Muƙaddimatuha,* na Dr. Yahya Al-Yahya, shafi na 6.

Allah don abin da Allah ya sanya a cikin ta na ƙarin girma da ɗaukakar matsayi da yawan lada bayan shuɗewar ta.

### 3.22 Musulunci ya Tsallaka Zuwa Ƙasashen Waje

Ganin halin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* yake ciki bayan wafatin waɗannan jigogin tafiyarsa guda biyu, sai Allah ya jefo ma sa tunanin fita daga garin Makka don ya nemi magoya baya wataƙila ko Allah zai kawo ma sa mafita a wani waje tun da su kam sun ƙi karɓar falalar Allah da ya aiko ma su. A cikin watan Shawwal na shekara ta goma da muke magana a kan ta, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* tare da rakiyar ɗan gidansa Zaidu ɗan Haritha ya tasar ma gidajen ƙabilar Thaƙif da ke garin Ɗa'if mai nisan kilomita 90 daga birnin Makka. Kasancewar Ɗa'if wani gari ne da yake kan tudu, wuri ne mai sanyi da ni'imar yanayi saɓanin Makka. Kuraishawa da yawa sun mallaki kadarori da gidaje a can, kuma akwai ƙawance mai ƙarfi da auratayya a tsakanin su da 'yan ƙabilar Thaƙif mazaunan Ɗa'if. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi fatar samun matsugunni a wannan gari da kuma goyon baya, ba don kome ba sai don zai zama yankan baya ga mushrikan Makka waɗanda suka takura ma sa a garinsu. To, sai dai a nan ma 'yar gidan jiya ce, domin shugabannin Ɗa'if ba su ba shi haɗin kai ba. Bayan sun yi ma sa maganganu na izgili da cin fuska kuma sai suka tura ma sa yara ɓata-gari suka yi ma sa rakiya da duwatsu; suka rinƙa jifar sa har in da ya ɓace ma su, suka daina ganin sa. Rigarsa ta jiƙa sharkaf da jinin jikinsa da na kansa saboda jifa. Haka shi ma Zaidu, a wajen kariyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya gamu da irin abin da ya gamu da shi.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ɗauki matakan tsaro da suka dace sosai wajen wannan tafiya. Da farko dai bai tafi a kan abin hawa ba, sai ya tafi a kasa domin ya ɓatar da tunanin jama'a kan cewa barin garin zai yi. Idan kuwa har suka fahimci haka babu shakka zasu kawo ma sa tarnaƙi a cikin lamarin tafiyar. Na biyu kuma ya tafi ne tare da Zaidu wanda aka san shi a

matsayin ɗansa, ta yadda babu wani shakku a ganin su tare. Sannan ya roƙi shugabannin Ɗa'if bayan da suka ƙi karɓar baƙuncinsa da su rufa ma sa asiri kada su bayyana maganar zuwan sa a can, duba da irin tsarguwa da za ta same shi idan labarin zuwan sa ya je ma mutanen Makka tare da cewa bai samu karɓuwa ba. Amma duk da haka ba su yi ma sa halin girma ba, sai da suka bayyana al'amarinsa har suka sa aka jefe su zuwa bayan gari, shi da ɗan rakiyarsa.[302]

Manzon Allah ya fito bayan garin Ɗa'if jini yana zuba daga kansa har ga takalminsa, yana neman wurin da zai zauna ya huta. Ya shiga lambun wasu miyagun mushrikan Makka su ne Utbatu da Shaibatu 'ya'yan Rabi'ata suna kallon sa har ya samu wata babbar inwa ya zauna yana addu'a:

> *"Ya ubangijina! Zuwa gare ka kai kaɗai nake kai ƙarar halin da nake ciki. Ya Allah! Karfina ya tafi, dabarata ta ƙare, mutane sun raina ni. Ya mafi jinƙan masu jinƙayi! Kai ne ubangijin masu rauni kuma kai ne ubangijina. Ina ne zaka jingina lamarina? A wurin na nesa da zai musguna min? Ko wurin maƙiyin da ka riga ka damƙa ma sa al'amarina? Idan ba ka cikin fushi da ni, ya Allah, babu damuwa. Amma kuma na fi son kwanciyar hankali. Ina mai neman tsari da hasken fuskarka wanda ke kawar da ko wane irin duhu, kuma yake gyara al'amarin yau da gobe, kada fushinka ya sauka a kaina, ko ƙyamarka ta far ma ni. Ina mai ba ka haƙuri - ya Allah - har sai ka amince. Kuma ba ni da wani ƙarfi ko dabara sai ta wajen ka".*[303]

Domin cikon jarrabawar ubangiji sai Allah ya aiko ma sa Mala'ika Jibrilu yana a kan hanyar sa ta komawa Makka a tare da rakiyar Mala'ikan

[302] *Mausu'at As-Siyar*, na Sallabi 1/213.
[303] *Sahih As-Sirah An-Nabawiyyah* na Ibrahim Al-Ali, shafi na 136 da kuma *Al-Hijrah An-Nabawiyyah Al-Mubarakah*, na Dr. Abdurrahman Al-Bir, shafi na 38.

duwatsu, suna neman izininsa a kan halaka mutanen Ɗa'if saboda abin da suka yi ma sa. Sai ya ba su haƙuri ya ce, ina fatar su shiriya. Ko kuma idan hakan ba ta samu ba a gaba zuriyyarsu ta ba da gaskiya.[304] Ka ji halin girma daga fiyayyen halitta mafi tausayi da rahama ga talikai.

Duk da irin jarabawoyin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya haɗu da su a cikin wannan tafiya, amma ya samu manyan nasarori guda biyu:

Nasara ta farko: Musuluntar Addas; wani matashi kirista dan ƙasar waje wanda yake aiki a gonar su Utbatu inda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yada zango yana hutawa. A lokacin da waɗannan mushrikai suka ga halin da yake ciki sun tausaya ma sa, sai suka aiki wannan yaron don ya kai ma sa kyautar dabino. Da zai ci ya yi bismillah, sai Addas ya tambaye shi cikin mamaki, a kan wannan kalma. Daga nan ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya samu mashiga ta kiran sa zuwa ga Musulunci kuma nan take ya karɓa.

Nasara ta biyu: Musuluntar ayarin aljanu su bakwai waɗanda suka saurari karatunsa a cikin ƙiyamullaili a kan hanyarsa ta komawa Makka. Sun musulunta nan take kuma suka ɗauki saƙonsa zuwa ga 'yan uwansu aljannu suna yi mu su wa'azi da abin da suka ji. Allah *Tabaraka Wa Ta'ala* ya ba Manzonsa labarinsu a cikin Suratul Jinn da kuma Suratul Ahƙaf. Daga bisani bayan aljannu da yawa sun musulunta ta hanyar waɗannan masu wa'azi sai suka aiko ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya je ya karantar da su, kuma ya ba su guzurin abinci daga sauran abin da al'ummar muminai suka ci.[305]

Hikimomin Allah da yawa suke! Wannan alheri da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya kawo ma mutanen Ɗa'if ba su karɓe shi ba, kirista ɗan ƙasar waje ya karɓa. Kuma duniyar aljannu ita ma ta karɓa. Idan

---
304 *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3231.
305 *Sahih Muslim*, hadisi na 150.

Kuraishawa sun azabta Sahabbansa daga cikin mutane, to ya zasu yi da Sahabbai aljannu?!

### 3.23 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Dawo Gida

Da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya zo shiga Makka sai ya yi wata siyasa wacce take cike da hikima bisa ga halin da ya bari da wanda ya tabbatar zai samu a garin. Sai da ya yi nazari mai zurfi sai ya zaɓi Mut'imu ɗan Adiyyu, ɗaya daga cikin waɗanda suka kafa wancan kwamiti na yaga takardar zalunci da aka liƙa ga Ka'aba wadda ta wajabta masu ɗaurin ta-la-la na tsawon shekaru. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya aika ma sa cewa, yana roƙon shiga Makka a ƙarƙashin kariyarsa. Mut'imu bai yi wata-wata ba ya ba da shela a cikin garin Makka cewa ya amintar da Muhammad *Sallallahu Alaihi wa Sallam*, kuma yana ƙalubalantar duk wanda yake tunanin taɓa shi ko ya yi ma sa wulaƙanci. Sannan ya gayyato 'ya'yansa suka fito da takubba suka shigar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har cikin masallaci ya yi ɗawafi ya yi sallah, sannan suka raka shi gidansa ba wani wulaƙanci da ya same shi.

Mut'imu dai shugaban gidan Naufal ɗan Abdu Manafi ne, kuma ya mutu a kan kafirci. Amma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* bai manta ma sa wannan alheri da taimako da ya yi ma sa ba. Har a lokacin da ake taƙaddama a kan fursunonin mushrikai da aka kama a Badar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* cewa ya yi, da ace Mut'imu yana duniya, idan ya neme su zan sakar ma sa su kyauta.[306]

[306] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 4024.

### 3.24 Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya Samu Lambar Yabo

A can baya mun ga irin wahalhalun da Manzonmu ya sha wajen wannan kira da yake yi, shi da magoya bayan sa. Har a cikin addu'arsa mun ji yana cewa, *"Ya Allah! A ina ne zaka jingina lamarina? A wurin na nesa da zai muzguna min? Ko wurin maƙiyin da ka riga ka damƙa ma sa al'amarina? Idan ba ka cikin fushi da ni, ya Allah, babu damuwa. Amma kuma na fi son kwanciyar hankali".*

Ijaba a kan wannan addu'a tasa sai Allah ya so ya nuna ma sa irin matsayin da yake da shi a wurin Allah da wurin masoyan Allah. Haka kuma aka so ya ga girman duniya da faɗin sarari na halittun Allah ta yadda zai kalli Makka a matsayin wani ɗan ƙaramin ƙauye da bai kamata a ta da hankali ba don mazaunanta sun yi ma gaskiya tawaye. A nan ne ya samu goron gayyata daga fadar Maɗaukakin Sarki, a cikin rakiyar babban amininsa daga cikin Mala'iku; Jibril *Alaihis Salam* suka tashi a kan wani abin hawa mai tafiyar walƙiya, shi ba jaki ba ne kuma ba doki ba. Suka yi tafiya a talatainin dare, suka je ƙasa mai albarka ta Falasɗinu. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi sallah a masallaci mai alfarma na Baitul Maƙdis - masallacin Annabawa - yana mai jagorantar su, sannan ya taka zuwa sammai guda bakwai - tare da Jibril - in da ya haɗu da wasu manyan Annabawa a kan hanyarsa ta zuwa fadar buwayayyen sarki.

A cikin wannan tafiya Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya gana da mahaliccinsa in da ya yi magana da shi ba shamaki. Kuma aka karrama shi da salloli guda biyar waɗanda ladarsu ta salloli hamsin ce.[307]

[307] *Sahih Al-Bukhari*, hadisi na 3887. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya samu karramawa ta musamman wadda ta sa aka kira shi don ganawa da maɗaukakin sarki a fadarsa, ya je da gangar jikinsa, mu kuma ya zo mana da tsarabar da za mu rinƙa ganawa da maɗaukakin sarki a fadarsa sau biyar a ko wace rana muna nan a ƙasa ba mu je ko ina ba. Allah muna godiya gare ka da zama cikin al'ummar wannan fiyayyen Manzo. *Al-Hijratu Wa Muƙaddimatuha,* na Dr. Yahya Al-Yahya, shafi na 14.

Haka kuma an nuna ma sa nau'oin mutane da suke shan azaba don ya tsoratar da al'ummarsa, waɗanda suka haɗa da: mazinata da masu hana zakka da masu cin naman mutane da masu dafe haƙƙen marayu da sauran su.[308] Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya dawo gida daga wannan muhimmiyar tafiya kafin wayuwar gari.

Wannan tafiyar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi ita ake ce ma "Isra'i da Mi'iraji". Kuma Maɗaukakin Sarki ya faɗe ta a surori biyu na Alƙur'ani su ne, "Suratul Isra'i" da "Suratun Najm". Tare da ɗinbin falala da girmamawa da take da ita a gare shi, ta zama wata babbar jarrabawa ga mutanen Makka; musulmi da kafirai. Su dai musulmi sun ci wannan jarrabawa tsaf, tun da daman can sun gaskata shi a manzancinsa. Don haka ba a samu musulmi ɗaya da ya nuna shakku a kan faruwar hakan ba. Amma kafirai sai suka mayar da wannan magana abin izgili da dariya. Suka kuma ƙalubalance shi da wasu tambayoyi waɗanda Allah ya ba shi ikon amsa su. Amma saboda rashin rabo sai suka ce yanzu ne ma suka ƙara haƙiƙancewa da shi boka ne.[309] Da suka zo wurin Sayyidi Abubakar sun yi tsammanin su ja hankalinsa. A lokacin bai riga ya ji maganar daga bakin ma'aiki ba. Sai suka faɗa ma sa labarin, ya ce da su Manzon Allah ne da kansa ya faɗi ya yi wannan tafiya? Suka ce, eh, ƙwarai kuwa. Ya ce, to, ya yi tafiyar kuwa babu shakka! Suka ce, ka yarda kenan?! Ya ce, abin da ya fi haka ma na gaskata shi a kai bale wannan!. Daga nan ne musulmi suka kira shi "Siddiƙ"; mai cikakkiyar gaskatawa. Sunan da ya zamo alami gare shi har ranar tashin ƙiyama.[310]

Wannan lamari ya zo a shekara ta 12, daidai lokacin da al'ummar musulmi take kan wata gaɓa mai muhimmanci a tarihinta. Domin kuwa, an fara wuce lokacin haƙuri a kan azabtawa da wulaƙanci. Abu kaɗan ya rage ayi hijira, a bar ma su garin, daga baya kuma a juyo - da ikon Allah - zuwa karɓar sa da kafa tutar addinin Allah a cikin sa. Shi ya sa ma aka wajabta ma su

[308] *Fath Al-Bari* na Ibn Hajar 8/200 da Tafsir na Ibn Kathir 4/247.
[309] *Uyun Al-Athar* na Ibn Sayyid An-Nas 1/140-142.
[310] *Al-Mustadrik* na Hakim 3/62.

sallolin farilla biyar don su ƙara shirin shiga mataki na gaba. Abin lura a nan shi ne, duk sauran ibadoji aiko da saƙo aka yi a kan su. Amma ita sallah sai da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya je da kansa. Don haka babu addini ga wanda bai san muhimmancin sallah ba.

### 3.25 Addinin Musulunci a Birnin Madina

Madina wani babban birni ne mai nisan kilomita 420 arewa daga birnin Makka. Mazaunan garin sun kasu kashi biyu; Yahudu da kuma larabawa. Larabawan su kuma ƙabilu biyu ne; Ausu da Khazraj, waɗanda aka san su da halin kirki da daɗin zamantakewa duk da yake suna faɗa da gaba a tsakanin junan su. Zamantakewar su da Yahud ta sa suna da wani ɗan haske game da addini da saƙon Annabawa. Har ma sun ji cewa, an kusa aiko Manzon ƙarshe wanda Yahudawa ke ce mu su za su bi shi don su yaƙe su.[311]

Mutum na farko da ya haɗu da Musulunci daga cikin 'yan Madina shi ne Suwaid ɗan Samit wanda ya zo aikin Hajji ko Umra sai ya haɗu da ma'aiki *Sallallahu Alaihi wa Sallam*. Manzon Allah ya kira shi zuwa ga Musulunci sai ya ce, watakila ai sha'aninmu iri ɗaya ne. Manzon Allah ya ce ma sa, mene ne sha'aninka? Ya ce, ai hikimomin Luƙman nake tafe da su. Sai ya ce, to karanta min in ji. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya saurare shi da kyau, sannan ya ce, lallai wannan sha'anin naka yana da kyau, amma ai nau ya zarce wannan. Suwaid ya ce, to wanne ne naka? Ya ce, Kur'ani ne aka saukar min daga wurin Allah. In taƙaice ma ka labari dai ba su rabu ba sai da Suwaid ya karɓi kalmar shahada. Amma da ya koma Madina an ce, tsotsayi ya haɗu da shi aka kashe shi a cikin yaƙin Bu'as.[312] Amma fa ya cika yana musulmi.[313] shekara ta sha ɗaya ne daga farkon manzanci wani ayari na mutane shida 'yan ƙabilar Khazraj suka zo aikin Hajji. Da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ji labarin zuwan su, sai ya fita bayan garin Makka ya tarbe su ya gana da su a wurin Aƙaba. Da suka ji kiran da yake yi da kuma ayoyin

---

311 *Zad Al-Ma'ad* na ɗan Al-Kayyim 2/50. Duba kuma Alƙur'ani mai girma a Suratul Baƙarah, aya ta 89.

312 Yaƙin Bu'as wani artabu ne da ya haɗa ƙabilun Madina guda biyu, shekaru biyar kafin hijira. Kuma a cikin sa ne aka gama da manyan masu taurin kai na garin kamar irin su Hudhair, mahaifin sahabin nan Usaid ɗan Hudhair wanda shi ne jagoran Ausu, da Amru ɗan Nu'uman jagoran Khazraj na wancan lokaci. Yaƙin sai ya zama wata shimfiɗa ga da'awar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam*. *Subul Al-Huda Wa Ar-Rashad* (3/192).

313 *As-Sirah As-Sahiha* (1/591).

Alƙur'ani da ya karanta ma su sai nan take suka ce ma junan su, wannan fa shi ne Manzon da Yahud ke cewa za su bi shi don su yake ku. Don haka kada ku bari su riga ku bin sa. Ba da ɓata lokaci ba suka karɓi kiran sa, suka ce ma sa daman mun baro garinmu a cikin matsalar rarrabuwa da yaƙi a tsakanin jama'armu. Don haka za mu je mu sanar da jama'armu, mu kira su zuwa ga wannan addini, muna fatar Allah ya haɗa kansu ta hannunka. Da komawar su suka duƙufa wajen kiran jama'a ga addini kuma aka yi ta karɓa ma su har ya zama ba wani gida a cikin Madina in da kiran bai ratsa ba.

Da shekara ta zagayo sai wani ayari na mazaje 12 da mace ɗaya suka sake zuwa aikin hajji kuma a asirce suka gana da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har suka yi ma sa mubaya'a a wurin Aƙaba. Da suka kammala aikin Hajjinsu sai ya haɗa su da wani saurayi masanin Alƙur'ani, shi ne Mus'abu ɗan Umair don ya karantar da su addini kuma ya jagorance su sallah. Da Mus'ab ya je Madina sai ya mayar da hankali sosai wajen kiran masu riƙe da madafan iko a birnin in da ya samu nasarar shigar da su Musulunci gaba ɗaya.[314]

A shekara ta uku sai ayarin mutane 73 suka zo Hajji daga cikin musulmin Madina, kuma saboda yaɗuwar Musulunci a can da ƙarfin da ya yi sun zo da niyyar su roƙi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yo ƙaura zuwa garinsu. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya tarbe su tare da baffansa Abbas duk da kasancewar har zuwa lokacin bai bayyana Musuluncinsa ba. Abbas kuwa ya yi ma su jan kunne mai girma game da wannan nauyi da suke son su ɗora ma kansu amma ba su razana ba saboda gaskiyarsu da imanin da ke cikin zukatansu. Daga ƙarshe sun so su ji ta bakin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* kuma ya yi ma su jawabi sannan ya karanta ma su Alƙur'ani. Kafin su tafi sai da suka yi masa mubaya'a ta biyu a kan ba shi cikakkiyar kariya irin wacce suke ba iyalansu daga ko wane irin maƙiyi babu togiya, kuma duk sharaɗin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa*

[314] *As-Sirah* na Ibn Hisham 268-269.

*Sallam* ya gitta ma su sai da suka ƙara ma kansu wanda ya fi shi nauyi don su tabbata ma sa cewa da gaske suke yi. Sannan ya nemi su naɗa wakilai 12 daga cikin su don su yi ma su jagora, sai suka zaɓi mutane 9 daga ƙabilar Khazraj da kuma 3 daga ƙabilar Ausu; daidai yawan su. Daga nan ne fa aka fara shirye shirye; musulmi suka fara yin ƙaura kaɗan kaɗan zuwa birnin Madina. A wannan karon hijirar ba ta da wahala sosai, ba don rashin nisan tafiya ko wahalar hanya ba. A'a, don za aje ne wurin ‘yan uwa musulmi waɗanda su da kansu ne suka yi gayyata, ga su kuma larabawa ne da suka yi tarayya da su wajen yare da abinci da yanayi da al'adu. Musulmi ba su yi gayya wajen fita ba, sai suka tafi a hankali, da ɗaya ɗaya, wasu kuma bi-biyu. Kuraishawa kuma kamar yadda suka saba suka rinƙa bin su da cutatarwa.

Daga cikin darussan da za mu koya a nan akwai irin tarbiyyar riƙon asiri da muhimmantar da sha'anin addini a wurin waɗannan bayin Allah 'yan Madina. Za mu gane wannan in muka ji abin da Jabir *Radhiyallahu Anhu* yake faɗi cewa, a mubaya'ar Aƙaba ta biyu sun kwanta tare da abokan tafiyar su daga cikin mushrikai, sai bayan sulusin dare suka rinƙa sulalewa da ɗaya-ɗaya da bi-biyu suna zuwa wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* har suka kai su 72.[315] Ana cikin haka ne Sheɗan ya yi wata hargowa don jan hankalin Kuraishawa, sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya umurce su da su tashi su koma wurarensu. wani sadauki daga cikin su; Abbas ɗan Ubadata ya ce, na rantse da wanda ya aiko ka da gaskiya idan ka umurce mu duk wanda yake Minna a yau za mu halaka shi. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya ce, tukuna ba a kai ga wannan ba.[316]

## 3.26 Waɗanda Suka Fara Yin Hijira

315 *As-Sirah An-Nabawiyyah as-Sahiha*, 1/199.
316 Duba littafin da ya gabata 1/201.

Bara'u ɗan Azib; ɗaya daga cikin musulmi mazaunan Madina ya ba da labarin cewa, mutane na farko da suka fara isa Madina a lokacin hijira su ne: Mus'ab ɗan Umair da Abdullahi ɗan Ummu Maktum, suka yi ta karantar da mutane Alƙur'ani. Daga bisani Ammar da Bilal da Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas suka zo. Sa'annan tawagar mutane ashirin ta iso a ƙarƙashin jagorancin Umar ɗan Khaɗɗabi yardar Allah ta tabbata a gare su baki ɗaya.[317] Akwai kuma ayarin da suka tafi a ƙarƙashin jagorancin Salim maulan Abu Huzaifa wanda ya riƙa ba su sallah a hanya.[318] Duka waɗanda suka tafi sukan shirya tafiyarsu ne a cikin dare sannan su fita da sanyin safiya da ɗaya ɗaya zuwa mahaɗar da suka yi matsaya a kan ta, sannan su ci gaba da tafiya a tare. Mutum ɗaya ne tarihi ya hikaito cewa ya tafi da rana tsaka yana ƙalubalantar masu hana tafiya. Wannan sadauki shi ne Sayyidi Umar ɗan Haɗɗabi yardar Allah ta ƙara tabbata a gare shi kamar yadda littattafan tarihi suka tabbatar.[319]

## 3.27 Kainuwa ba ki Nutsewa

Babu shakka Kuraishawa sun hana masu rauni tafiya Madina da ƙarfin tsiya. Wasu kuma sun so tafiya da iyalansu amma aka shiga tsakanin su, sai suka tafi dole suka bar su, wasu kuma sai da aka ɗaure su don kada su sulale. Tare da haka dai kafin wani lokaci Madina ta ɗau harami da baƙin alheri waɗanda aka tarbe su cikin murna da ban girma da mutuntawa.

Daga cikin labarai masu ƙayatarwa da suke nuna juriyar Sahabbai da gaskiyar manufarsu ga taimakon Musulunci akwai labarin Ɗalhatu ɗan Ubaidullahi wanda ya yi hijira tare da abokinsa Suhaibu ɗan Sinanu. Shi wannan na biyun kuma daman mai dukiya ne. Da aka cim ma su sai suka tsaya, Suhaibu ya ja kibiyarsa ya yi ma ta saiti, sannan ya ce, kun sani sarai

317 *Sahih Al-Bukhari,* Darajojin Ansar, Babin zuwan Manzon Allah da sahabbansa, hadisi na 3924 da 3925.

318 *Sahih Al-Bukhari,* Littafin sallah, babin limancin bawa da wanda aka 'yanta, hadisi na 692.

319 Duba: *Ar-Riyadh An-Nadhira Fi Manaƙib Al-Ashara*, na Muhibbuddin At-Tabari 1/259.

ƙwararre nike a wajen harbi, kuma kafin ku kashe mu wallahi zan iya kashe mutane da yawa a cikin ku. Don haka, ina ba ku shawarar ku shafa ma kanku lafiya. Sai suka ce to mun ji, amma ba zaka tafi da kuɗinka ba. Suhaibu ya ce, wannan mai sauƙi ne. Sai ya ajiye jakarsa, ya ce ma Ɗalhatu mu je gaba. Ba su bar shi a haka ba, sai suka ce, ai ba iyakar kuɗinka kenan ba. Sai ya ce ma su kada ku samu damuwa. Ku je wuri kaza da kaza duk kuɗina suna can ku yi ta sha'ani. Kafin su isa Madina Allah masanin gaibi ya labarta ma Manzonsa wannan namijin ƙoƙari da Suhaibu ya yi na sadaukar da dukiyarsa don ya tsira da addininsa. Don haka ya tarbe su yana murna yana cewa "Cinikin da aka yi ya yi riba baban Yahya"!. Malaman "Asbabun Nuzul" sun ce, a dalilinsa ne *Tabaraka Wa Ta'ala* ya saukar da aya ta 207 a cikin Suratul Baƙara in da yake cewa:

> *"Daga cikin mutane akwai wanda ke sayar da rayuwarsa don neman yardar Allah, kuma Allah mai yawan tausayi ne ga bayi".*[320]

Mu haɗu a kashi na biyu na wannan littafin don jin yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi wa Sallam* ya yi tasa hijira da yadda aka kafa sabuwar gwamnatin Musulunci a Madina.

Allah ya yi mana gamon katar da alheri.

[320] Suratul Baƙarah: 207